[12/6, 9:38 AM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*Dedicated*
*to* *my* *shadow*

wattpad@fatimaumarmoddibo

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

..............................................................

*~We are bearer's of so golden pen🖊️~*

*~we write assidiously perceive no pain~.*

*~So magical,Our creative golden pen✍,behold our words.~*

*~A product of our pen🖊️,savour our words, for it will cause you no pain.~*

.................................................................

Page 1
.

.....Cikin yanga da ƙasaita take saukowa daga matakalar benan gidan, idan ta ɗaga kafa daya kafin ta ƙara ɗaga ɗayar ta sai ta ɗau saƙonni,duk wanan abun cikin kayan makaranta take yi,sikit ne ɗan ƙarami iya gwuwarta nevy blue sai rigarta fara mai ratsi-ratsin blue ba hijjab a jikin ta sai hular da ke kanta.

Wata kyakykyawar dattijowar matar da ke zaune a cikin tanƙameman falon ta hango yadda take saukowa daga benan murmushi tayi sanan ta ce "ƴar aljanna!! ke kullum sai kinyi latti,kinsan ƙarfe nawa ne yanzu kuwa?
cikin tausasawa take mata maganar.

It kuwa wacce aka kira da ƴar aljanna ko a jikinta banda ma ƙara rage saurin da tayi.

Wanan dattijowar bata ƙara ce mata komai ba, binta da kallo da tayi ko kaɗan bata nuna alamun ɓacin rai ko wani abu makamancin haka a fuskarta ba banda ma wani lafiffayan murmushi da take yi .

Ƙamar ta ƙarye dan tsabar yanga,ta iso falon,kan jikin  dattijowar ta faɗa ,kanta matar ta taɓa,cikin so na nuna damuwa ta ce "Ƴar aljanna ko ba zaki makarantar ba ne? idan ba zaki ba muje ki cire kayan sai ki gayamin inda kike son zuwa mu je"

Kamar mai tsoron magana ta buɗe bakinta cikin shagaɓa ta ce "Zani *Hajiya* bana son wahala ne gashi wanan ƴar iskar malamar ce maiyar turanci zata fara shiga ajin ,ta kai ƙarshen maganar  haɗe da ramutse fuska tana kallon Hajiyar.

"Kam to kina jina,duk abinda aka miki ki kira ni,zasu ga wanda ya tsaya miki,ni da su ne shege ka fasa ɗan halar sai yanka"

Washe ƙaramin bakinta tayi ,tana jin daɗi da alfahari,rungume hajjiyar tayi "Ina sonki hajiyata"

Tana faɗa ta tashi tabar falon cikin jin daɗi.

"Nima ina sonki ƴar aljanna sai kin dawo"

Tun kafin hajiya ta gama maganar ta bar falon.

Ɗaidai waata ƙatowar makaranta wacce kallo daya zaka mata ka fahimce makarantar bata ƴaƴen yara ba ce,ta tsaro da navy blue da farin fanti,yanayin makarantar idan ka gani ka ce ba'a j9 ba ne dan yadda suka tsarata,ƙatowar motar ta tsaya.

 horn ɗaya direban yayi aka buɗe ya kunna kai,saida ya isa inda ake faking ɗin motoci sannan ya tsaya,bata wani tsaya ɓata lokaci ba ta fito.

J S S 3
Aka rubuta a saman  ajin,kai tsaye ta kutsa kai ba tsoro ba tantamar komai,kanta a ƙasa.

"Hy  how dare  u enter me class without  any excuse"

Saida nayi da ƙyar sanan naji abinda take faɗi,dan yadda take turanci kamar ba ƴar 9j  ba,ko wacce tai karatu a kasar turai.

Ko ƙadan bata ji tsoro ba ta ɗago kai ido biyu suka yi,da wacce tai maganar

Tsaye take a gaban Allon,kyakykyawa ce ajin farko kallo daya zaka mata ka fahimce yadda tsarin halitar jikinta yake,ƴar gajerace ba cancan ba,siririya ce ga dogon hanci kyakykyawa,bata da wani girman jiki amma kana kallon fuskarta zata san cewa wanan ba yarinya ba ce,dan ta kwana biyu.

Tun a kallo na farko na gane ƴar iyaye ce,dan yadda take yamutsa fuska kamar tana kallon

ɗanyen kashi.

Ido cikin ido suke kallon juna,bata ɗauke idanta ba ta fara tafiya.

"Keee wacce irin dabbace mara hankali da wayau kuma jahila"
Cikin ɓacin rai da kausassaiyar murya ta faɗa.

Wani irin mugun kallo ta bita da shi mai cike da tsana ,amma sai naga ta sake wani ɗan karamin murmushin keta ta ce "Au sari kinsan bana jin turanci balle irin naki me kama da yaren chaina"

Tana rufe baƙi yan class ɗin suka fashe da dariya wanda daman tunda ta shigo hankalin su ya dawo gareta dan sun san sai anyi drama...

Fita tayi daga  cikin ajin ranta a ɓace,ita kuwa ko a jikin ta daman hakan take so ,tana jin zafin maganganun da Aunty ke gaya mata,shiyasa ta ke son ganin ɓacin ranta.

" *Sabreen* *Muhammad* *mai* *taƙama*"
Da ƙarfi ya kira sunan cikin faɗa.

"Kina ina?yana maganar yana kallon ƴan class ɗin.

Gaba daya ajin yayi shiru kamar ba halitta a ciki dan ko numfashi a hankali suke yi dan tsabar tsoron wanda ya shigo ajin.

Cikin nuna ko a jiki na ta tashi daga gurin da take zaune ,hankali kwance ta nufi inda suke,kallon Aunty ta fara yi wacce tare suka shigo class ɗin da shi.

Saida ta matsu kusa da shi sosai sannan ta tsaya ,ta kuma zuba mishi manyan idanuwanta wanda ba alamar tsoro a tare da su.

"Me kika cewa Malama *Haulat* *Hashim* *Kabir* ?eyeeh ba dake nake ba,kin kafe ni da ido"

Saida ta kalle malama Haulat ɗin sanan ta dawo da kallonta gare shi "Ce mata na yi ni bana jin turancin ƴan chaina,tamin na ƴan nigeria"

Shi kanshi bai san lokacin da dariya ta suɓuce mishi ba,dan duk makarantar kowa yasan iyayenta gurin turanci amma ba wanda ya taɓa mata magana sai Sabreen.

Ganin shi ma ya fara dariya abin ya ɓata mata matuƙa ga yan ajin suna dariya,a fusace tabar class ɗin,tsanar sabreen kuma da niyyar ɗaukar fansa.

Ganin ta fita yasa shi ma yai sauri yabar ajin.

wani annuri ya baiya na a fuskar sabreen dan jin daɗin yadda ta ga ranta a ɓace,komawa tayi ta zauna amma duk ji take yi bata rama hulaƙancin da malama haulat ɗin ke mata.

Zaune take ita kaɗai  a staff room tana tunanin wani irin abu zata ma Sabreen ta huce,murmushi naga tayi wanda ya ƙara baiyana kyawun ramammiyar fuskarta,wato abinda zata ma Sabreen tayi shi yasa ta yin murmushi.

Ƙarfe ukku daidai aka buga ƙararrawar tashi,koya hankalin shi ya koma gidan, gaba ɗaya malamai da ɗalibai sun fito kuwa ya nufi hanyar gurin ajiyar motoci.

Har aka gama zuwa ɗaukan dalibai Sabreen tana zaune ita kadai ,ranta ya ɓace sai huci take yi,tana turo baki,tashi tayi zata fita bakin get.

Da mugun gudu motar malama Haulat ta zo wuce wa,ta gabanta kamar zata ɗauke ta,da sauri a ruɗe sabreen ta matsa har saida ta faɗi kasa,wani irin ƙululon takaici  ya kamata,da zafin nama ta tashi ta nufu motar.

Tana ganin ta  nufota ,ta fito daga motar tana wani yamutsa fuska kamar wacce tai arba da kashi

" U are very no what u are,okkk i forget u are illiterate ,baki da gwagwalwa ne ko a garin mahaukata aka daukoki da kina ganin mota ba zaki iya kaushewa ba"

Tunda ta fara magana Sabreen ki binta da idanuwa wadanda sukai jajiir dan tsabar takaici.

Ita kuwa malama Haulat ganin ta cinma burinta yasa ta wuce ta barta anan tsaye, ta kuma ja motar da karfi har saida ta watsa mata kura.

Wani lafiyayyan hawaye ya fara bin fuskar Sabreen wanda ita kanta bata san da zuwan su ba, sai jin su tayi a fili ta ce tana huce kamar wacce tai faɗa da zaki "Hmm baki san waye Sabreen Muhammad mai taƙama ƴar Aljanna ba ne,bana yafiya kuma bana biyar bashi zan rama ramuwar gaiyya"

Tana faɗa ta sa hannuwanta ta fara goge hawaye tana faɗin "Hm kika sa ƴar aljanna hawaye zai kin biyasu"

"To yah zanyi idan na gayawa hajiya ,A'a ba zan gayawa hajiya ba,ni da kai na zan ji da ita "

Ita fitowa bakin get ɗin direban ta ya zo ,bata ce mishi komai ba ta buɗe motar ta shiga.

"Ƴar aljanna kiyi hakuri wallahi faci tayar motar tayi,jikin shi har rawa yake yi dan tsoron karta gayawa Hajiya"

Banza tayi da kamar bata san da wani a cikin motar ba.

Sai magiya yake mata akan karta gayawa hajiya.

"To naji amma zai kamin abu ɗaya ta faɗa tana kallon shi

"to zanyi ƴar aljanna koma meye zanyi"

Murmushin mugunta tayi da jin dadi ,harda sauke ajiyar zuci.

Daidai wani katafaren gidan direban yayi horn aka buɗe mishi,giɗan ya haɗu iya haɗuwa abin sai wanda ya gani,dan tsayawa kwatanta muku sai ya ɗauke ni lokaci mai tsawo.

Tana jin ƙarar motar su,ta fito da sauri har bakin motar ta fito tana wace baki ,ita da buɗe mata kofar hade da faɗin "Ƴar aljanna kin dawo tun ɗazun naji shiru ina ta jira hankali na ya tashi ina fatan dai kina lafiya"

Murmushi tayi sannan ta rungumeta "Kina lafiya hajiyata yau bamu fito da wuri ba ne,wanan ƴar iskar malamar ce ta tsayar da mu"

"Cikin nuna damuwa ta janye jikin ta tace"Wai ko sai na tura anje gurinta ne aja mata kunne,ko na fitar da ke daga makarantar gaba ɗaya ma"

"A'a Hajiya ki barta kinji "

"to ni bansan duk wani mahalukin da zai ɓata miki rai,zan iya yin komai akan farincikin ki"

Daidai da isar su cikin katon falon wanda shi ma ya ƙyyatu har tsoro yaban dan tsabar kyaun shi,ga wani asirtaccen kamshi wanda ya haɗe da AC ɗakin.

Murmushi tayi cikin shagwaba ta ce "Nima na sani hajiyata,amma tunda na ce ki barta kawai ki barta zanyi maganin ta ,zan gwada mata ni ɗin ƴar gata ce"

"Hajiya bari na hau zama nayi wanka sai nayi sallah na huta"

"Yawwa ƴar aljjanna na manta ban gaya miki ba,ɗan india ya dawo an jima sai ki je ku gaisa"

Yamutsa fuska tayi yin sunan wanda ya dawo din"Wanan dan iyayin wanda aka je ɗauko mu tare"

"Eh shi fa"

"Tabbb gaskiya ni ba zani ba saida shi ya zo "ta faɗa tana hada rai

"to shikenan ba zai kin ɓata rai ba,zan sa ya zo da kanshi,kinji hankalinki ya kwanta"

ta washe baki "eh hajiyata,ta haye sama ,a ranta tana faɗin yadda zata ganshi dan tun sanin farkon da ta mishi kafin yaje india dan iyayi da kinibibi ne,to bari yanzu da yaje india....

Kasa kwanciyar tayi, tunanin abinda zata yi ma malama Haulat ta shiga yi, wani guntun murmushi tayi dan ta gano abinda zata mata , gajiya da zama ita kaɗai tayi ta sauƙo falo.

Ba Kowa a falon ,har zata ɗakin Hajiya sai kuma ta fasa ta dawo ta zauna.

"Banza dabba daƙiƙiya mara hankali"
Runtse idanuwanta tayi tuno zafafan maganganun da malama haulat ke gaya mata.

Bata san lokacin da hawaye suka ƙankaro mata ba,sai jin su tayi ,ƙasa share su tayi dan takaici a fili ta ce "Wallahi sai kin biya,baki san waye ƴar aljanna ba,bana yafiya kuma ba zan yafe miki.

Wani irin hamshakin ƙamshi hancin ta ya ji,wanda saida ta lumshe ido tai wata irin ajiyar zuciya ,ɗago da manyan idanuwanta tayi dan ganin wanda ƙamshin ke tashi a jikin shi.

Waw masha allah ,allah yayi halitta wanda duk wanda yai arba da ita saiya ɗan tsorata dan tsabar kyau,kyakykyawa ne first class ga kwarji ni irin na jaruman maza ga izza,abin kamar a novel,fari ne sul mai yalwar gashin kai da na ido da na gira,ga dugon hanci kamar na indiyawa,duk da fuskarshi a murtuke take amma saida kyawun shi ya fito

Tsaye yake a kofar falon hannuwan shi gaba ɗayan su ya rungume su a ƙirjin shi,fuskar nan a murtike sai yatsinata yake yi ,kamar wanda ya shigo bola.

Tun kallon farko da Sabreen ta mishi ta gane shi,ganin yadda yake yatsina fuska yasa ta kau da kai ,ta ƙara gyara zaman ta rimot ta ɗauka ta chanja tasha ta kuma ƙara bulum,ta gafen ido take kallon shi yakai saƙonni a tsaye a gurin kafin ya fara tawo wa,wani ƙululon takaici ya kamata,Sabreen ta tsana mutum mai iyayi da kilibibi.

Dan guntun tsaki ta ja,ta cigaba da kallon tivi abinta.
Har tsakiyar falon ya iso,kallon ta yayi yana mamaki hali irin ta,wanda zai kira da rashin tarbiyya,bai ce mata komai ba ya samu guri ya zauna yana wani yatsina fuska haɗe da hura ɗan karamin hancin ta,yana kuma taɓe ƙaramin bakin shi,ni dai kuwa kallon shi kawai nake yi ina murmushi dan abin ya mishi kyau.

Ganin bata da niyyar mishi magana gashi yana sauri yasa ya kalle ta a hankali cikin wata irin murya wacce zamu kira da ƴan kilibibi ya ce "Sabreen plss go call hajiya for me"

Da sauri ya juyo tana kallon shi bata san lokacin da wata irin muguwar dariya ta kubuce mata ba,"Bala'i yau ga wanda yafi malam haulat  bala'i to ikon allah "
A zuciyarta tayi maganar ta kuma ƙasa daina dariyar.

Wani irin kallo ya bita da shi yana yamutsa fuska haɗe da taɓe baki,cikin wani irin ƙaƙale ya ƙara ce mata "What  Rong  with you"

Haba ai sai ta ƙara fashewa da wata muguwar dariya harda hawaye dariya dariya kamar ba zata daina ba,idan zata daina sai ta ƙara tunowa ta ƙara kwacewa da  dariya.

"Ƴar aljanna dariyar me kike yi haka ,lafiya?

Hajiya ta faɗa lokacin da ta shigo falon gurinta ta ƙarasa,ɗagowan da tayi ta ganshi ,ta washe baki ta ce "Ƴan india ne a gidan yaushe ka shigo"

Saida ya yamutsa fuska  kamar wanda ke jin wari ko wanda  yake kallon kashi ya ce "Ɗazun ne"

Haba ai wata irin dariya ta ƙara fashewa da ita har saida ta faɗo daga kan kujerar dan tsabar dariya.

"Waiyo ni Sabreen hausar ma ba za'a barta ba"

A zuciyar ta faɗa,ita kuwa Hajia ruɗewa tayi dan ganin irin dariyar da Sabreen ke yi.

"Waiyo Allah na bani ƴar aljnna"

*Naufal* hajia ta kira shi, ka taimaka ka kira likita"

"u mean doctor"

Ba Sabreen ba ni kaina saida na dara dan yadda ya ƙira doctor ɗin,mugun ɗan ƙaƙale ne,dan abin dashi ya wuce iyawa ya koma kaƙale,kamar yadda ake fitar da harafin larabci haka yake fitar da kowanne harafi harda ƙari ma.

Kuka hajia ta fara "Waiyo na shiga ukku ni yau"

Ganin hajia na ƙara ruɗewa yasa ta fara kukarin tsaida dariyar amma ta kasa,saida ƙyar da sassauta dariyar ta kalli hajia ta ce "Waiyo hajia ta ba komai lafiya ta lau dariya ne Kawai"

Shi kuwa Naufal yana gefe yana kallon su dan bai gane shi take yiwa dariya ba,dan shi a nashi ganin baiyi abin dariya ba,kallon mahaukaciya yake mata.

"Jajia bari na tafi ana jira na"

yadda ya ke kiran sunan hajiyar ma abin a dara ne,dan mugun ɗan ƙakale ne na ƙarshe.

Kasa ɗaurewa Sabreen tayi haba ai sai ta cigaba da dariyar.

"To mutun india ka gaida hajiyar ku ,zamu shigo da daddare mu amshi tsarabar mu"

"Okkk hajia sai kun zo"

Kamar wanda ba bahaushe ba haka yake hausar.

Yana gama faɗa yabar falon yana tafiya cikin ƙasaita da izza tafiyar ma abin kallo ce,da ana karatun iya tafiya da sai na ce ,yayi digiri gurin iyawa.

Da ƙyar sabreen ta iya tsaida dariyar ta"Hajia ta wai ke ba ki ji abinda da nake yiwa dariya ba"

"Yo ina zan ji  ni tsoro ma kika ban"

"Wancam ɗan indian ne yaban dariya ji yadda yake magana kamar shi ya kawo magana duniya u mean doctor"

ta maimaita abinda ya faɗa ta irin yadda yayi maganar.

Dariya ita ma hajiyar tayi ta ce "kin san daga india yake shiyasa"

"Su ƴan indian haka su ke,ƙilibibi ne na bala'i,kai bari n Je nayi wanka dan jikina duk ya mutu .

"Ba dole ba irin wanan mahaukaciyar dariya ai dole jiki ya mutu"

hajiar na gama maganar ta haye sama tana dariya da mamaki dan bata taɓa  tunanin za'a samu wanda yafi malama haulat iyayi da ƙilibibi ba...

~~~~~~~~~~~~~

Zaune take a tankameman falon wanda yasha fentin pink da fari haka zalika komai na cikin falon kujeru da flowers da sauran kayan alatun rayuwa.

Fuskar nan tata dauke take da annuri wanda nake ganin kamar haka halitta yake wato smile face akan 2 sitter take zaune,ita ma karya kyakykyawace ga murmushi, babba mace ce mai halin girma.

A gafe guda kuwa  Wata kyakykyawar yarinyace ko na ce budurwa wacce shekarun ta ba sufi
~~~~~~~~~~~~~

goma sha takwas ba, tun kallo na farko na gane suna da alaka da matar nan dan irin Yadda suke gama.

Cikin siririyar murya ta kalli matar ta ce "Momy nifa na ƙagara naga tsarabar da yaya Naufal ya kawo min,wai ina ma yaje ne daga zuwan shi"

Murmushi tayi wanda ya ƙara baiyana zatin fuskarta ta ce "ke kuwa *farrah* kina da gajin hakuri kuma kin san halin Naufal baya son damuwa idan kika nuna mishi kin zaƙu ya hanaki,ya je gurin Hajia ya gaida ta"

Taɓa fuska tayi ,bata ƙara cewa komai ba,da juya ta fuskanci tivi.

"Assalamu alaikum ya faɗa a hankali ita kanta sallamar kamar da turanci yayi na ce da Sabreen nan hhh da tasha dariya.

A tare suka amsa mishi kowanne su fuska ɗauke da Annuri ,Farrah ce ta fara magana "Yaya ka dawo"

cikin yatsine ya ɗaga mata kai bai ce komai ba.

Ita kanta farrah bata son hali irin na shi ga rashin kula mutum ga sharewa ga yatsine.

"Naufal ya hajiar"

"Tana lafiya tana gaida ke wai anjima zata shigo"

Yana faɗa ya tashi cikin yauƙi yabar falon.

"Allah momy yaya  ya ƙara Chanjawa daa da ɗan sauki ,amma yanzu tunda ya dawo abin ya ƙaru"

Murmushi momyn tayi dan nasan gaskiya farrah ta gaya mata.

~~~~~~~~~~~~~

Cikin shigar doguwar jira ƙirar dubai ta ke baƙa ce rigar ta matuƙar amsar jikin ta kamar dan ita aka yi rigar,rolling tayi da ɗan ƙaramin gyalen waw,masha allah *Sabreen* kyakykyawa ba wani haske gare ta ba,amma akwai kyau kamar me,ɗan karamin bakin ta wanda yake kamar an zana shi,shi ke ƙara fidda kyawun ta,hancinta dogo ne amma ba siriri ba ne tana da cikar fuska ga fararen haƙora da ido  gata da yalwar gashin gira da na ido ,ga iya murmushi hmmm abin dai sai wanda ya gani dan kamar a novel lolx to meye wanan..

🤸🤸yehh yanzu zan fara.
~~~~~~~~~~~~~

ga me bukatar shiga grp ɗin 08155184562

comment
shire
✅ote me on wattpad@fatimaumarmoddibo

~Bhartoolerty~
[12/6, 9:38 AM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ 🅿σѕт 🅱у 🅶яσυρ 🅾 🅵 🅷уρє 🅷αυѕα 🅽σνєℓѕ 🅱σσк 🆆нαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/9, 1:05 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

Page 2

.....................................
Cikin yanga ta ƙara su falon tana murmushi ta ƙagara gobe tayi,dan taje makaranta ta rama abunda Malama Haulat tayi mata.

"Kai masha Allah ƴar Aljanna kinga yadda kike da kyau kuwa "
Hajiya ta faɗa tana kallon Sabreen ɗin.

Washe baki tayi ta ce"Hajiya ta ai ke na biyo shiyasa nayi kyau"

Ƙarasawa gurin Hajiyar tayi fuskan nan tata ɗauke da annuri, kan jikinta Hajiyar ta kwanta.

"To tashi muje tunda kin shirya"

Murmushi tayi tuno Gidan su Naufal zasu je,wanda ba wani tazara a tsakanin su dan a layi ɗaya suke.

"To muje ta faɗa haɗe da tashi ta fita gurin direba ta nufa ,yana ganinta ya taso a ruɗe.

"Kai kaji dai abinda na gaya maka,wallah inda aka samu matsala kasan abinda zan ma ba zai na gayama ba,da zaran ka ga kira na goben sai ka shirya,kasan yadda zaka yi da mai gadin makarantar ka kul....

"Ya dai lafiya ko wani abun ya miki ne" faɗar Hajia.

"A'a ba abinda ya min ,muje ko"

Buɗe musu motar yayi suka shiga,ba wani lokaci suka ɗauka ba dan daman duk a layi ɗaya ne.

Baban Gida ne mai ɗan karan kyau amma bai kai na su.

Hajiyar Gidan da farrah suna zaune a falo suka isa  cikin falon.

Ba wanda Sabreen take jin kunya a rayuwarta sama da iyayen Naufal musamman hajiyar shi.

Har kasa da duƙa a gaban ta ce "Ina wuni momy ya gida"

Fuska ɗauke da annuri ta kalle ta ce mata" Lafiya lau Sabreen ya makarantar baki son zuwa gidan nan bansan abinda aka miki ba"

Ita murmushin tay ta ce "Ba komai momy zan dunga zuwa"

"Yawwa ko kefa ƴar gatan hajia"

Dukkan su suka yi murmushi,momy ta gaida hajia cikin martabawa da mutuntawa.
Inda farrah take nan Sabreen da zauna suna shiri da ita sosai ɗan farrah bata da iyayi da nuna iyawa da alfahari da gadara shiyasa suke shiru sosai da ita.

Hajia ta kalli Momy ta ce "Wai ina mutan india ne,ya zo ya bamu tsarabar mu "

"Sun fita tare da Alhaji amma yanzu zasu dawo tunda yasan da zuwan ku"

"To allah ya kawo su "

"allah yasa kar nayi dariya" sabreen ke faɗi a zuciyar ta.

Basu wani jimaba sai ga sunan ,Alhaji babban mutum ne kallo ɗaya zaka mishi ka fahimce hakan ga Annurin fuskar ko da yaushe kamar yana murmushi haka fuskarshi take irin ta hajia.

Da sallam suka iso falon,Shi Naufal ba wanda yaji tashi sallamar dan bala'i irin nashi.

Kan kujerar da Hajia ke zaune a nan Alhaji ya Zauna fuskan nan tashi ɗauke da murmushi "Sabreen zo nan Alhajin ya kirata.

Cikin jin kunya ta taso kasa da tsugunna,yasa hannu ta ɗago ta ya zaunar da ita kan cinyar shi.

Wani gululun takaici ya kama Naufal "Duk kun lalata yarinya da gata sai abinda ta ke so ake yi

ba dole ta lalace da dinga yiwa mutane fitsara ba,kamar wanan katowar yarinyar zaka zaunar da ita kan jikin ka "

Duk a zuciyar shi yake wanan bambamin yana wani yatsina fuska kamar wanda ke kallon ɗanyan kashi.

"Sabreen ya gida ya makaranta?

"Lafiya lau dady"

"Masha allah Sabreen ki dage kinji,yanzu tunda ga yayan ku ya dawo kafin ya fara Aiki zai ɗinga zuwa har gida yana miki lesson"

Dumm Dumm gaban shi yai mugun faduwa,"shi xai ɗinga yiwa ƴar rainin wayun nan lesson kuma sanan shi zai bita har gida bama ita zata zo ba" a zuciya yake wanan tunanin dan baya gardama da dadyn shi.

"Aiki ja wanan ba zai iya da ni ba,nima kuma ba zan iya da bala'in kiliibin shi ba,yanzu ya zanyi"

"Naufal kullum zaka ɗinga zuwa indan ta dawo daga makaranta ka ji"

Maganar da dadyn yayi shi ya katse musu tunanin da kowannan su ke yi a zuci.

A sanyaye ya ce "Toh dady ,yana gama faɗa ya tashi zai wuce rai ɓace,dady yai saurin kiran shi "Naufal ka fito musu da tsarabar su,indan ka shiga ɗaki"

"To dady ya faɗa fuskar nan duk ta jagwalgwale da ɓacin rai.

Ya dade bai fito ba,har saida suka je daining table suka fara cin abinci sanan ya fito hannun shi dauke da kaya.

Yana zuwa ita ya fara miƙa mawa ,wani abu ne a baƙar jaka,ita ma kamar yadda ya ɓata rai haka tayi ta ce"Na godeee"

Ko nuna almar yaji bai yiba balle ya bata amsa.
"Ke baka ji ta ce ta gode ba" Dadyn ya faɗa.

Bai kalla inda take ba ya ce "u are wllcm"
Cikin salon kilibibi.

Dariya ce da zuwa Sabreen duk yadda taso ta shanye kasawa tayi saida tayi ciki-ciki bata so a gane sai da hau yin murmushi me kama da dariya

Iri ɗaya da abinda yaba ma Sabreen yaba farrah sai momy da hajia kowanne nashi a rufe,har ya juya sai tafi dady ya kira shi "Ina zaka ba zaka tsaya muci abinci tare ba yaushe rabonka da zama cikin ƴan uwa ,wai me yasa baka son mutane ne ,kuma har ƴan uwanka"

Bai ce mishi komai ba yaso ya zauna akan kujerar dake fuskantar Sabreen.

Kallon shi take yi tana son yin dariya ganin yake kallon abinci kamar kashi,yana fara cin abincin Sabreen tai kasa da kanta dan tasan zata iya yin dariya.

Bayan sun kammala cin abincin suka dawo falo.

*ASALIN* *SU*

Maryam sunan hajia na ainihi ƴar asalin kauyen bauchi ne,cikin rashin gata da taso gurin iyayenta,har suka mata aure,Muh'ad mai taƙama shine babban ɗan ta kuma shi ne mahaifin Sabreen,sai rabi'u (Alhaji)mahaifin su Naufal.

Muh'ad mahaifin sabreen yana zuciyar naima kuma ya taso yana son karatu duk da tasarar shekara ɗaya da rabi ne a tsanin shi da Rabi'u amma haka ya hakura da karatun shi  dan kanin nashi yayi,tun yana shekara goma mahaifin su ya rasu,shi ya ɗau dukkan nauyin su ci da sha sutura da makarantar rabi'u,wanan ne dalilin dayasa Hajia ke mugun son shi.

Bayan rabi'u ya kammala secondry ,yayi iya kuƙarin shi har samu gurbi a ABU zaria ya tafi ,bayan tafiyar muh'd ya cigaba da naiman kuɗi yana kula da kansu kuma yana turawa Rabi'u.

Bayan rabi'u ya kammala karutun digirin shi ya dawo gida,aka fara fafatukar naiman aiki,Cikin sa'a allah yasa ya samu a garin abuja.

Saboda riƙon alkawari da amana da biyayya irin na Rabi'u yasa ogan shi ya aure mishi ƴar shi Zainab ƴar ɗaya takk ƴar gata ga mahaifinta masu kuɗin gaske ne.

Bayan Auren Rabi'u ya ƙasa gaya ma ƴan uwan shi yayi aure gashi har matar da samu ciki,bayan shekara biyar ya lokacin zainab ta haifi Naufal yana d shekara huɗu,Rabi'u ya zo gida da sha tara na arziƙi,kuma ya ƙasa gaya musu yayi aure,kwana biyu yayi ya koma abujan.

Bayan tafiyar shi hajia(maryam)ta matsa mishi yayi tunda abubuwa sun daidata gashi yana ta manyan ta.

Bayan shekara hudu  da tafiyar Rabi'u aka kira shi yayan shi zaiyi aure,a lokacin ya yanke shawarar zuwa da iyalan shi.

Hakan kuwa ta faru ,basu nuna ɓacin ransu ba ko ƙaɗan sai ma farincikin da suka yi ga Naufal

ya girma a lokacin yana da shekara takwas.

Bayan bikin muh'ad Da shekara ɗaya aka haifi Naufal,lokacin Haihuwar Naufal allah yayi wa mahaifiyarta rasuwa.

Sabreen ta taso a hanun hajia cikin jin dadi,har ta girma,ta fara zuwa makarantar firamari har ta kai aji shidda.

Rana ɗaya aka wayi gari Muh'd ya rasu ,hajia tayi kuka tayi kuka kamar ranta zai fita dan tana matuƙar son shi,A lokacin da Rabi'u yaji yayi kuka kamar me dan duk duniya yafi son yayan shi sama da komai ,a lokacin Sabreen bata da wayau sosai.

Wanan ne dalilin dayasa suke matuƙar son Sabreen musamman Hajia dan son ɗanta ne ya koma kan sabreen ɗin gashi tana jin tausayin ta.

Bayan rasuwar shi da sati ɗaya Alhaji rabi'u yaso ya ɗauke hajia suka dawo Abuja.

Lokacin basu daɗe ba Naufal ya tafi india karatu.

Da aka kai Sabreen makaranta aka ce primary 3 za'a maidata,taƙi yarda da gyar da zauna a aji biyar.

Sabreen bata iya turanci ba,tana ji dai,ta tsana kilibaban mutum da mai nuna shi wani ne da son na iya ta gadara da taƙama.

wanan kenan nan to muje zuwa,kashh shadow tayi kira bari na tafi ma haɗe anjima🏃‍♀️🏃‍♀️.

.
Sir Dboy
[12/9, 1:05 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт Bу Gяσυρ O F Hуρє Hαυѕα Nσνєℓѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/9, 1:07 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

Page 3

---

Ta kai tsawon minti biyar a gurin da Malama Haulat ta barta , tsabar takaici da baƙin ciki, yasa

ta ƙasa komawa cikin motor ,sai da direban ya fito ya mata magana sanan ta koma cikin  motor.

Karfe hudu da rabi suka isa Gida,cikin ɓacin rai ta isa falon ,ko sallama bata yiba.

"Kee! ya buga mata tsawa.

Tsayawa chikk tayi bata kuma juyo ba,ganin bata da alamar juyowa yasa ya ƙara faɗin "Wai ke wacce irin yarinya ce kina ganin mutane ba zaki iya gaida su ba,kuma dan rashin tarbiyya ko sallama baki yi ba"

Yadda taji maganar yasa ta tabbatar  da Naufal ne dan iyayin da taji yana yi,ɓacin ran da take ciki ya hana da yin dariya.

Juyowa tayi Zaune ya ke akan one siter ta ganshi yasha baƙin glass fuskar nan a dagule kamar wande ke zaune a cikin bola.

Kamar zata ce mishi wani abu ta fasa,tai wucewar ta zama da sauri.

"Ɗuk ɗady ne zai ja min raini kamar ni za'a ce na zo har gurinta"

Cikin ɓarin rai yayi maganar wanda ɓacin rai har ya samu gurin zama a fuskarshi shiyasa ɓacin rai ke mishi kyau,tashi yayi yabar gidan gaba ɗaya.

Tana isa ɗakinta ta shige toilet ta daɗe tana watsa ma jikinta ruwan sanyi.

"Ba abinda na ya taɓa min rai ban rama ba,karki yi tunanin zan gyale ki dan kin kai ne ƙarshe zan miki abinda sai kin zubur da ƙwalla da idanuwan ki,kuma sai kin ce na haifu ni sabreen muh'd mai taƙama,bana ɗaukar bashi" wasu zafafan hawaye suka biyo kyakykyawar fuskarta.

Tana cikin yin Sallah hajia ta shigo ɗakin ,zama tayi har ta idar.

"Ƴar aljanna lafiya ki kuwa ,ki faɗamin abinda ke damunki zan miki maganin shi komeye shi"

Sabreen bata iya ɓoye ɓacin ranta ba shiyasa  hajia ke ganewa.

Kan jikin hajiar ta dawo ta kwantar da kanta,ta ƙaƙalo murmushi ta ce "ba komai hajia ta kin san ina gaya miki abunda ke damu na,karki damu ba komai"

"Taya ba zan damu ba,dumwarki damuwa take sa ni "

"hajia zan sha ice-cream muje ki sai min"

"Ice cream to yar aljanna muje direba ya kai mu ko"

Tai saurin katsi ta" a'a Yaya Naufal nake son ya kai mu"

Hmm baka san waye Sabreen ba da zaka min tsawa ni nace ka zo gidan mu ko da zaka sauke fushin ka a kai na ,a zuciyarta ta ke wanan tunanin haɗe da yin murmushin mugunta.

Cikin sigar rarrashi hajiar ta ce "Naufal to shi zai kai mu,karki damu je ki shirya,wai ba alhaji ya ce yazo yau ya miki karatu ba"

taɓe baki tayi "hm ai dan raini ne ba zuwa zai yiba"

"Bari zan haɗa shi da dady "

Murmushi tayi na jin daɗi ta ce " to ki kira shi bari na chanja kaya" tana faɗa ta tashi ta nufa gurin kayanta ,ita kuma hajia ta fita falo.

Cikin wata haɗaɗɗiyar doguwar riga ta shirya ,rigar ta matuƙar yi mata  kyau kuma ta kama jikinta wanda yasa dukkan shape ɗin ta ya baiya na,pich colour ne rigar da ratsin baki,bata ɗaura ɗangwalin ba ɗan karamin gyalen kayan ta yashi a kanta,kana iya hango baƙin gashinta mai santsi,duk da tana da ɗan tsawonta amma tana son dugon takalmi,shi kuwa ta sa ɓaki mai ɗan karen kyau,bata yi wata kwalliya mai yawa ba,huta sai kwalli da pink ɗin jan baki wanda yai ma ƙaramin bakin ta kyau.

Cikin yanga da ƙasaita take saukowa daga matattakalar.

Hango shi tayi a zaune cikin ɓarin rai duk da ɓarin ya saba zama a fuskarshi ,amma yanzu kam kana ganin shi kasan ɓacin ran mai tsanani ne,yai hura hanci yake yi yana wani yamutsa fuska.

Cikin fara'a ta isa fallon ,kallon shi tayi tana murmushin mugunta ta ce "Ya Naufal ina wuni ya gida ya aiki?

Ko kallon inda take bai yiba,ya miƙe tsaye "Zamu iya tafi?ya faɗa cikin salo da ƙaƙale.

Kasa ɗaurewa tayi saida dariya a zuciyar ta tana faɗin"Bala'i Wai hausa ma sai an mata ƙaƙele wannan da kai ka kawo yare da ni kuwa bani ba koyan magana"

Hajia ta kalle shi rai a ɓace ta ce"Kai kana jin tana gaida kai wai meyasa kake wa yarinyar nan haka ne"

Taƙaici kamar yayi kuka,gashi yanzu da yayi wani abu zata gayawa dady shi kuma baya son ɓacin ran dadyn shi ko kaɗan.

Wani mummunar kallo ya mata ya ce "Me kika ce Sabreen  maimaita ban ji ba"

Saida da lumshe idon daya kira sunanta ji tayi kamar ba wanda ya taɓa kiran sunan da daɗi,sabo sunan ya dawo mata,ydda ya kira har zuciyarta saida ta ji shi,amma saboda hali irin da Sabreen cewa tayi haɗe da taɓe fuska"Salo sunan ma da turanci za'a faɗa kai dai abunka yayi yawa"

A zuciyarta tayi wanan mgnr amma a fili cewa tayi" Cewa nayi ina son ganin gari,zaka kai ni duk inda ka sani"

Bai san lokacin da wani tsadaddan murmushi ya fito ba saida jin haƙurin shi a waje iskar falon ta duke su.

Ba komai ne ya haifar mishi da wanan tunann ba sai jin mamakin sabreen da ƙarfin hali,ita gani take ita me wayau ce.

"Laaah ashe ya iya murmushi to ko me yasa yayi ? ohhhon mishi .

Ta tambayi kanta sanan ta ba kanta amsa.

Har ya bar falon ,binshi a baya suka yi ,yayi tunanin a gaba zata zauna sai ya ga kuma ta zauna a baya.

Sai zubawa hajia shagwaɓa take yi da biyu ganin yana ɗan gutun tsaki yasa ta ƙara yinta da salo ma.

"Kun lalata yarinya,kun koya mata fitsara" a zuciyarshi yake wanan maganar.

ostrich bakery  wanda ke unguwar sarki ya fara kai su,kaya mai yawan gaske ta zaba duk da biyu tayi hakan dan hajia ta saka Naufal  ya ɗauka.

"Washh hajiata ba zan iya kai kayan na n gurin motor ba"

"To daman ai ba ke zaki ɗauka ba Naufal zai ɗauka"

Juyowa yayi ya kalle hajiar.

"Ko ba zaka ɗauka ba ne"

kasa magana yayi dan ɓacin rai bai iya cewa komai ba ya ɗau kayan,har yayi dan nisa Sabreen ta kira shi "Ƴaya tsaya na duba wani abu"

Tsayawa yayi yana mata wani irin mugun kallo ,wani murmushi yayi na mugunta dan ya ga yadda zai mata ,ruwan da ke hannun shi ya kalla,a hankali da dubara ya buɗe ruwan yayi

kamar zai sha ya zubar a ƙasan gurin.

Allah sarki Sabreen bata sani ba,kuma dai ita ma bata san ba ko wacce fansa ake ɗauka ba.

Cikin yanga ta tawo habba sai jinta tayi dimmm ta zame ta faɗi har saida ƙafarta tayi ƙara.

"Waiyooo Allah na hajia ta ,ta sake ihuu da karfi.

Da gudu a ruɗe hajiar ta ƙaraso gurinta "Na shigo ukku ƴar aljanna me ya same ki ,gaba ɗaya hajia ta ruɗe .

Ko mutsi daga inda yake bai yiba,kallon su kawai yake yi yana murmushin mugunta.

Sabreen ga raki kasa tashi tayi ita kuwa hajia ta ƙara ruɗewa.

chin chiɓar ta aka yi har cikin motar,shi kuwa ko gyalenta bai taɓa ba,gashin kanta  ya mishi kyau bai taɓa tunanin a 9j xa'a samu me kyaun gashi ba.

Motar shi ma ya shiga ya fara tafiya a hankali yake jan motar yana jinta tana raki,murmushi kawai yake yi.

"Yanzu ina zamu?
ya faɗa hankali kwance.

Cikin faɗa hajia ta ce "wacee irin magana ce haka,gana ganin halin da muke ciki"

"hajia daman naji ta ce wai tana son na kaita duk inda na sani ne"

"Toh a hakan"

ta juyo da kallon ta gurin sabreen ɗin "Sannu kinji ko muje asibiti ne?

Da sauri ta ce "A'a muje gida ki shafa min magana "

"to yadda kika ce ƴar aljanna"

Wanan karan har saida haƙuranci suka baiyana "Wai ƴar aljanna"

Gida ya maida su ,amma bai shigaba a harabar gidan ya tsaya suka sauka yai wucewar shi.

Ranar  a ɗakin ta hajia ta kwana.

~~~~~~~~~~~~~
~~~~~~~~~~~~~

Ƙiran sallar farko hajia ta farka,ɗakinta ta koma.

Sai shidda saura Sabreen ta farka tana farka ta ma manta da tana da ciwo a kafa saida taji zafi,amma haka nan ta ɗaure tayi sallah,ko kaɗan sabreen bata wasa da ibada.

Bayan ta idar ta sallar wata dubara ta faɗo mata,da sauri ta tashi ta hau shirin makaranta,Cikin kankanin lokaci ta gama shiryawa,ƙafar tana mata mugun ciwo amma haka nan ta ɗaure ta sauko ƙasa.

Ɗakin hajia ta nufa tana kiranta"Hajiata! hajiata?

Da sauri hajiar ta durgo daga saman gadon ta "Ƴar aljanna lafiya ƙafar ce..
ganinta da kayan makaranta yasa ta ƙasa maganar.

Murmushi Sabreen tayi dan tasan kallon da hajiar ke mata,mugun ƙarfin hali tayi ta ƙara gurin hajiar cikin tafiya mai kyau ta ce "Kin gani ko hajia naji sauƙi sosai yau ina da test ne shi yasa zanje da ba inda zani"

Cikin wata irin siga hajiar ta ce"Sabreen kiyi hakuri karki je"

Murmushi Sabreen ɗin tayi ta ce "Hajiata wai baki yarda da ni ba ne,baki ga yadda nayi tafiya ba ne,naji sauki sosai zamu yi test ne shiyasa"
Tana ƙarasa maganar ta isa gurin hajiar kwanciya tayi akan ta.

"To Sabreen duk abinda kike so shi zanyi ,dan bana son ɓacin ranki ko ƙaɗan"

Wani lafiyayayyan murmushi Sabreen ɗin tayi ta ce"Hajiata ina sonki !

"ni ma ina sonki Savreen ki kula sosai kinji bana son wani abu ya same ki"

"to hajita zan kula sosai,bari na tafi kar tana yi latti,byee sai na dawo,tana gama faɗa ta tashi.

Hajiyar ta ce "ba zaki bari na raka ki ba "

"Eh ki huta abinki lokacin har ta bar ɗakin.

Gaisawa da direban suka yi sanan ta shiga motar,a tsorace yake dan jiya yasan planing ɗin su bai yiba,kuma yasan Sabreen bata yafiya ba hakura zata yiba taurin kai gareta.

Jin bata ce mishi komai ba har suka isa makarantar ya bashi mamaki tunani ya farayi wani irin hukunci zata ɗauka kuma.

Ba mutane a makarantar sosai.

office ɗin malama haulat ta nufa kai tsaye ta shiga.

Zaune take akan kujerarta tana duba wasu litattafai cikin wani tsadaddan material wanda yai matukar yi mata kyau,fuskar nan a yamutse kamar kullum.

Saida ta tsorata jin an buɗe kofa ba'a ƙwanƙwasa ba.

Cikin ɓacin rai ta kalli Sabreen"Ke wacce irin dabbace jahila mara hankali"

Har Sabreen ɗin zatai magana ta fasa ko meye ta tuno? ohoo.

Takai tsawon minti talatin a tsaye a gurin ,ita kuma malama haulat ganin bata da niyyar magana yasa ta fita lamarinta ta cigaba da abinda take yi.

Ganin mutane sun fara yin yawa yasa Sabreen ta kalli Malama Haulat ɗin cikin ɓacin rai ta ce"Ke wawiya karki ƙara kira na da waɗan nan sunayen"

"Ɗago kai Haulat tayi cikin mamaki tsaye ta
tashi tana kallon Sabreen ɗin.

Ganin ta tunzura yasa Sabreen ɗin kara faɗin "ni ba wawiya bace ke ce wawiya kuma dabba jahila"

Ran Haulat ɗin yai mugun baci,bulalar take kan tebur ɗin ta ɗauko,ta zubawa Sabreen a jiki.

Haba ai abin naima ya samu ai da Sabreen ta sake wani irin gigitaccen ƙara ta zube ƙasa tana ihuun gaske tana birgema a kasa haɗe ta faɗin " waiyo Allah na zata kashe ni ƙafata ciki na waiyo kaina kai na nashi ukkku hajiata ku taimake ni zata kashe ni!!!

Dan tsabar mamaki Malama haulat tsayawa ma tayi tana kallon ta jikin ta duk ya mutu.

gafin ka ce me office ɗin ya cika da mutane Sabreen tana ganin haka ta fara nishi tana ɗauke numfashi ai sai suka ƙara ruɗewa ga malama Haulat tsaye da bulala a hannunta.

A ruɗe aka ɗauke Sabreen wani ɗaki aka kaita ita kuwa sai ɗauke numfashi take yi tana kiran hajia.

Ganin za'a mata allura ai sai ta fashe da kuka tana faɗin" waiyo ƙafata  ku kaini gurin hajiata ƙafa ta  ta ƙaryamin ƙafa"

da sauri ya duka ƙarfa ya ganta taji ji kuma ta kumbura duk da ba wani haske gareta ba amma

ƙafar tayi ja.

Gaba ɗayan malaman makarantar sun ruɗe suna tsoron kai wani abu ya faru da Sabreen ɗin.

Allura ya mata tana ihuu tana kuka dan bata son allura amma haka nan suka mata cikin ƙamƙanin lokaci barci ya ɗauke ta.

~~~~~~~~~~~~~~

Ranshi a ɓace ya kalli haulat wacce ita ma ranta a ɓacen yake ya ce mata"yanzu me kika aikata kina son ki ja mana wani abu ne a makaranta dan baki san waye wanda ke ɗaukan nauyinta ba ne,duk abinda ta miki ba zaki iya kawo kararta ba,zaki yi mata irin wanan dukan yanzu ga shi ta samu matsala a ƙafa,ni wllh yanzu ban san yadda zanyi ba,ansa ya miƙa mata wata takarda.

gabanta yai mummunan faɗuwa kallon takardar ta tsaya yi.

"Ki ansa nace" ya faɗa cikin faɗa.

jiki na rawa tasa hannu ta ƙarɓa.

"mun takatar dake na sati biyu"

Dumm Dumm gaban haulat ya fara faɗuwa da ƙarfin haske haɗe da zaro ido tana kallonshi.

"Tashi ki fita  ya faɗa rai ɓace"

jiki ba ƙwari ta tashi...

........................................

tirkashi!!!!

gaskiya ni comment na ke so,bana son wani tnx ko wata heart haba ga tawa ga taku ai sai tamin yawa.

ku ƙara gyara zama dn zanyu zan fara.

.

[12/9, 1:07 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ 𝗣σѕт 𝗕у 𝗚яσυρ 𝗢 𝗙 𝗛уρє 𝗛αυѕα 𝗡σνєℓѕ 𝗕σσк 𝗪нαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚

[12/9, 1:10 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
~~~~~~~~~~~~~~

*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

Page 4
..................................................

Fita tayi daga  cikin ajin ranta a ɓace,ita kuwa ko a jikin ta daman hakan take so ,tana jin zafin maganganun da Aunty ke gaya mata,shiyasa ta ke son ganin ɓacin ranta.

" *Sabreen* *Muhammad* *mai* *taƙama*"
 Da ƙarfi ya kira sunan cikin faɗa.

"Kina ina?yana maganar yana kallon ƴan class ɗin.

Gaba daya ajin yayi shiru kamar ba halitta a ciki dan ko numfashi a hankali suke yi dan tsabar tsoron wanda ya shigo ajin.

Cikin nuna ko a jiki na ta tashi daga gurin da take zaune ,hankali kwance ta nufi inda suke,kallon Aunty ta fara yi wacce tare suka shigo class ɗin da shi.

Saida ta matsu kusa da shi sosai sannan ta tsaya ,ta kuma zuba mishi manyan idanuwanta wanda ba alamar tsoro a tare da su.

"Me kika cewa Malama *Haulat* *Hashim* *Kabir* ?eyeeh ba dake nake ba,kin kafe ni da ido"

Saida ta kalle malama Haulat ɗin sanan ta dawo da kallonta gare shi "Ce mata na yi ni bana jin turancin ƴan chaina,tamin na ƴan nigeria"

Shi kanshi bai san lokacin da dariya ta suɓuce mishi ba,dan duk makarantar kowa yasan iyayenta gurin turanci amma ba wanda ya taɓa mata magana sai Sabreen.

Ganin shi ma ya fara dariya abin ya ɓata mata matuƙa ga yan ajin suna dariya,a fusace tabar class ɗin,tsanar sabreen kuma da niyyar ɗaukar fansa.

Ganin ta fita yasa shi ma yai sauri yabar ajin.

wani annuri ya baiya na a fuskar sabreen dan jin daɗin yadda ta ga ranta a ɓace,komawa tayi ta zauna amma duk ji take yi bata rama hulaƙancin da malama haulat ɗin ke mata.

Zaune take ita kaɗai   a staff room tana tunanin wani irin abu zata ma Sabreen ta huce,murmushi naga tayi wanda ya ƙara baiyana kyawun ramammiyar fuskarta,wato abinda zata ma Sabreen tayi shi yasa ta yin murmushi.

Ƙarfe ukku daidai aka buga ƙararrawar tashi,koya hankalin shi ya koma gidan, gaba ɗaya malamai da ɗalibai sun fito kuwa ya nufi hanyar gurin ajiyar motoci.

Har aka gama zuwa ɗaukan dalibai Sabreen tana zaune ita kadai ,ranta ya ɓace sai huci take yi,tana turo baki,tashi tayi zata fita bakin get.

Da mugun gudu motar malama Haulat ta zo wuce wa,ta gabanta kamar zata ɗauke ta,da sauri a ruɗe sabreen ta matsa har saida ta faɗi kasa,wani irin ƙululon takaici  ya kamata,da zafin nama ta tashi ta nufu motar.

Tana ganin ta  nufota ,ta fito daga motar tana wani yamutsa fuska kamar wacce tai arba da kashi

" U are very no what u are,okkk i forget u are illiterate ,baki da gwagwalwa ne ko a garin mahaukata aka daukoki da kina ganin mota ba zaki iya kaushewa ba"

Tunda ta fara magana Sabreen ki binta da idanuwa wadanda sukai jajiir dan tsabar takaici.

Ita kuwa malama Haulat ganin ta cinma burinta yasa ta wuce ta barta anan tsaye, ta kuma ja motar da karfi har saida ta watsa mata kura.

Wani lafiyayyan hawaye ya fara bin fuskar Sabreen wanda ita kanta bata san da zuwan su ba, sai jin su tayi a fili ta ce tana huce kamar wacce tai faɗa da zaki "Hmm baki san waye Sabreen Muhammad mai taƙama ƴar Aljanna ba ne,bana yafiya kuma bana biyar bashi zan rama ramuwar gaiyya"

Tana faɗa ta sa hannuwanta ta fara goge hawaye tana faɗin "Hm kika sa ƴar aljanna hawaye zai kin biyasu"

"To yah zanyi idan na gayawa hajiya ,A'a ba zan gayawa hajiya ba,ni da kai na zan ji da ita "

Ita fitowa bakin get ɗin direban ta ya zo ,bata ce mishi komai ba ta buɗe motar ta shiga.

"ƴar aljanna kiyi hakuri wallahi faci tayar motar tayi,jikin shi har rawa yake yi dan tsoron karta gayawa Hajiya"

Banza tayi da kamar bata san da wani a cikin motar ba.

Sai magiya yake mata akan karta gayawa hajiya.

"To naji amma zai kamin abu ɗaya ta faɗa tana kallon shi

"to zanyi ƴar aljanna koma meye zanyi"

Murmushin mugunta tayi da jin daɗi ,harda sauke ajiyar zuci.

Daidai wani katafaren gidan direban yayi horn aka buɗe mishi,giɗan ya haɗu iya haɗuwa abin sai wanda ya gani,dan tsayawa kwatanta muku sai ya ɗauke ni lokaci mai tsawo.

Tana jin ƙarar motar su,ta fito da sauri har bakin motar ta fito tana wace baki ,ita da buɗe mata kofar hade da faɗin "Ƴar aljanna kin dawo tun ɗazun naji shiru ina ta jira hankali na ya tashi ina fatan dai kina lafiya"

Murmushi tayi sannan ta rungumeta "Kina lafiya hajiyata yau bamu fito da wuri ba ne,wanan ƴar iskar malamar ce ta tsayar da mu"

"Cikin nuna damuwa ta janye jikin ta tace"Wai ko sai na tura anje gurinta ne aja mata kunne,ko na fitar da ke daga makarantar gaba ɗaya ma"

"A'a Hajiya ki barta kinji "

"to ni bansan duk wani mahalukin da zai ɓata miki rai,zan iya yin komai akan farincikin ki"

Daidai da isar su cikin katon falon wanda shi ma ya ƙyyatu har tsoro yaban dan tsabar kyaun shi,ga wani asirtaccen kamshi wanda ya haɗe da AC ɗakin.

Murmushi tayi cikin shagwaba ta ce "Nima na sani hajiyata,amma tunda na ce ki barta kawai ki barta zanyi maganin ta ,zan gwada mata ni ɗin ƴar gata ce"

"Hajiya bari na hau zama nayi wanka sai nayi sallah na huta"

"Yawwa ƴar aljjanna na manta ban gaya miki ba,ɗan india ya dawo an jima sai ki je ku gaisa"

Yamutsa fuska tayi yin sunan wanda ya dawo din"Wanan dan iyayin wanda aka je ɗauko mu tare"

"Eh shi fa"

"Tabbb gaskiya ni ba zani ba saida shi ya zo "ta faɗa tana hada rai

"to shikenan ba zai kin ɓata rai ba,zan sa ya zo da kanshi,kinji hankalinki ya kwanta"

ta washe baki "eh hajiyata,ta haye sama ,a ranta tana faɗin yadda zata ganshi dan tun sanin farkon da ta mishi kafin yaje india dan iyayi da kinibibi ne,to bari yanzu da yaje india....
.....Cikin yanga da ƙasaita take saukowa daga matakalar benan gidan, idan ta ɗaga kafa daya

kafin ta ƙara ɗaga ɗayar ta sai ta ɗau saƙonni,duk wanan abun cikin kayan makaranta take yi,sikit ne ɗan ƙarami iya gwuwarta nevy blue sai rigarta fara mai ratsi-ratsin blue ba hijjab a jikin ta sai hular da ke kanta.

Wata kyakykyawar dattijowar matar da ke zaune a cikin tanƙameman falon ta hango yadda take saukowa daga benan murmushi tayi  sanan ta ce "Ƴar aljanna!! ke kullum sai kinyi latti,kinsan ƙarfe nawa ne yanzu kuwa?
cikin tausasawa take mata maganar.

It kuwa wacce aka kira da ƴar aljanna ko a jikinta banda ma ƙara rage saurin da tayi.

Wanan dattijowar bata ƙara ce mata komai ba, binta da kallo da tayi ko kaɗan bata nuna alamun  ɓacin rai ko wani abu makamancin haka a fuskarta ba banda ma wani lafiffayan murmushi da take yi .

Ƙamar ta ƙarye dan tsabar yanga,ta iso falon,kan jikin  dattijowar ta faɗa ,kanta matar ta taɓa,cikin so na nuna damuwa ta ce "Ƴar aljanna ko ba zaki makarantar ba ne? idan ba zaki ba muje ki cire kayan sai ki gayamin inda kike son zuwa mu je"

Kamar mai tsoron magana ta buɗe bakinta cikin shagaɓa ta ce "Zani *Hajiya* bana son wahala ne gashi wanan ƴar iskar malamar ce maiyar turanci zata fara shiga ajin ,ta kai ƙarshen maganar  haɗe da ramutse fuska tana kallon Hajiyar.

"Kam to kina jina,duk abinda aka miki ki kira ni,zasu ga wanda ya tsaya miki,ni da su ne shege ka fasa ɗan halar sai yanka"

Washe ƙaramin bakinta tayi ,tana jin daɗi da alfahari,rungume hajjiyar tayi "Ina sonki hajiyata"

Tana faɗa ta tashi tabar falon cikin jin daɗi.

"Nima ina sonki ƴar aljanna sai kin dawo"

Tun kafin hajiya ta gama maganar ta bar falon.

Ɗaidai waata ƙatowar makaranta wacce kallo daya zaka mata ka fahimce makarantar bata ƴaƴen yara ba ce,ta tsaro da navy blue da farin fanti,yanayin makarantar idan ka gani ka ce ba'a j9 ba ne dan yadda suka tsarata,ƙatowar motar ta tsaya.

 horn ɗaya direban yayi aka buɗe ya kunna kai,saida ya isa inda ake faking ɗin motoci sannan ya tsaya,bata wani tsaya ɓata lokaci ba ta fito.

J S S 3
Aka rubuta a saman  ajin,kai tsaye ta kutsa kai ba tsoro ba tantamar komai,kanta a ƙasa.

"Hy  how dare  u enter me class without  any excuse"

Saida nayi da ƙyar sanan naji abinda take faɗi,dan yadda take turanci kamar ba ƴar 9j  ba,ko wacce tai karatu a kasar turai.

Ko ƙadan bata ji tsoro ba ta ɗago kai ido biyu suka yi,da wacce tai maganar

Tsaye take a gaban Allon,kyakykyawa ce ajin farko kallo daya zaka mata ka fahimce yadda tsarin halitar jikinta yake,ƴar gajerace ba cancan ba,sirirya ce ga dogon hanci kyakykyawa,bata da wani girman jiki amma kana kallon fuskarta zata san cewa wanan ba yarinya ba ce,dan ta kwana biyu.

Tun a kallo na farko na gane ƴar iyaye ce,dan yadda take yamutsa fuska kamar tana kallon ɗanyen kashi.

Ido cikin ido suke kallon juna,bata ɗauke idanta ba ta fara tafiya.

"Keee wacce irin dabbace mara hankali da wayau kuma jahila"
Cikin ɓacin rai da kausassaiyar murya ta faɗa.

Wani irin mugun kallo ta bita da shi mai cike da tsana ,amma sai naga ta sake wani ɗan karamin murmushin keta ta ce "Au sari kinsan bana jin turanci balle irin naki me kama da yaren chaina"

Tana rufe baƙi yan class ɗin suka fashe da dariya wanda daman tunda ta shigo hankalin su ya dawo gareta dan sun san sai anyi drama...

yawan comment yawan typing

.
[12/9, 1:10 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт By Gяσυρ  O F  Hуρє Hαυѕα Nσνєℓѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/9, 1:11 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

___________________________.

Sabreen bata daina dariyar ba har saida ta gaji ,ta tsaya dan kanta, ta juyo ta kalleshi ya ɗaure fuska kamar me shirin yin kuka,sai ya ƙara bata dariya ta  ƙara fashewa da dariya.

Ya ƙasa tashi ya fita kuma ya ƙasa mata magana kallon ta kawai yake yi,yana murmushi wanda bai san dalilin yin shi ba.

Bayan ta gaji da dariyar ta matso da litattafan gaban shi har ya ɗauka ya buɗe aka kira wayar shi yana ganin kiran na waye yai wani irin murmushi.

Kallon shi Sabreen tayi a zuciyarta ta ce "Ikon allah waye kuma da ake mishi irin wanan murmushin"

Duk yadda Sabreen ta so jin abinda yake faɗi ta ƙasa dan yadda yake maganar ko maciji ba zai ji ba.

Sun daɗe suna wayar har sabreen ta fara gajiya sai wurga mishi harara ta gefen ido take yi.

guntun tsaki taja ta tashi ta haye sama.

Bayan ya gama wayar ya ga ba Sabreen a gurin yamutsa fuskar yayi ya tashi ya wuce abinshi.

~~~~~~~~~~~~~

Yau ma ƙarfe ukku da rabi da dawo daga makaranta,kamar yadda suka saba zama a falo kafin a kira sallah yau ma hakan ne,kiran sallah shi ya tashi su kuwa ya wuce ɗakin shi dan gabatar da ibada.

Bata yi sunanin Ya Naufal zai xo ba,cikin ƙananan kaya da sauko kasa kanta ba ɗan kwalli ,lokacin hajiya ma bata fito ba.

Cikin salo da ƙarya murya yayi sallama ,kasancewar tibin a kashe yake yasa taji sallamar,amsawa tayi ba tare da ta juyo ba.

A yatsine ya shigo ya zamu kujera ya zauna,yana zama kiran Haulat ya shigo.

"Hello ita ta fara faɗa.

"Hi my dear ya kike?
~~~~~~~~~~~~~

"Lafiya qalau ya su momy,gaskiya yau ina son ganin da wuri jiya kawai amma ji nake kamar na shekara ban ganka ba,kasan irin damuwar da nake shiga kuwa idan ban ganka ba,plsss ka zo kar zuciyata ta fashe"

Murmushi kawai yake,ita ke kira kuma ta fishi yin magana.

"Ok to zan zo karki damu"

Duk wanan maganar  da suke yi Sabreen bata jin komai,tana jin ya gama wayar ta juyo ta kalle,bai san lokacin da murmushi ya kuɓuce mishi ba.

Yaƙuna fuska tayi ta ce "Ina wuni tana faɗa bata tsaya jiran amsar shi ba ta tashi ta hau sama"

daman bashi da niyyar amsa mata gaisuwarta.

Da jakar ta fito ,tun daga sama ya hango ta ,da sauri ya sauke kan shi ƙasa,duk sai yaji ya ruɗe kamar wanda bai taɓa ganin macce da irin wanan shigar ba.

Ita kuwa hararar shi ta dinga yi har ta matso kusa da shi ta aje jakar ta zauna,ganin bashi da niyyar cewa wani abu yasa ta ce "Gashi

Ɗagowa yayi fuskar nan a ɗaure tamau ya amsa littafin yana ɓuɗewa kira ya ƙara shigowa wayarshi,ɗaukar wayar yayi yana murmushi ya ce " my dear"

Wanan kalmar kuwa Sabreen tayi sa'ar ji  a ranta ta ce "Dear tabb yanzu wanan yana da budurwa ita kuwa wacce iri ce? eh fah saidai irin shi  dan idan ba irin shi ba wacce zata iya da shi"  har ya kama wayar idonta yana kanshi.

Ƙafin ayi karatun nan kuwa haulat ta kira yafi sau biyar,har Sabreen ta lura da tafi damuwa da shi,dan shi duk da bajin abinda yake cewa take yi ba,tasan ta fishi  yin magana dan tana lura da bakin shi.

~~~~~~~~~~~~~

Har sati ya zagayo sun ƙara turuwa a gidan su ɗin.

Sabreen har ta ƙama lura da Haulat  tafi son shi,dan kullum a gabanta sai ya ƙira shi a gabanta sama da sau biyar.

Yanzu ya rage bata dariya akan maganar shi,tayi mamaki da ta gane yana jin indian ,gashi tana mugun son yaran indiyanshi.
~~~~~~~~~~~~~

~~~~~~~~~~~~~

Yau sati ranar monday Haulat zata koma bakin aikinta.

Zaune take akan kujerar dake falon su tana latsa wayarta.

A fili naji ta ce "Hmm Sabreen kin sa an bani suspension ke kuma a makarantar zan saka a kore ki gaba daya baki san hali na ba, da zaki ce zaki ja da ni"

" ke dawa kuma aunty Haulat"

Kallon wacce tayi mata maganar tayi ƙaramar kanwar ta ce sadiya.

Murmushi Haulat ɗin tayi ta ce"Yarinyar da ta ja aka bani suspension"

"allah karki raga mata,ki ci mutuncinta"

Murmushin ƙeta haulat ɗin tayi ta ce"Ke ma kin san hali na ba zan raga mata ba,ko kaɗan"

Dariya suka yi,nidai ce kin ɓuture Sabreen ko wani sharrin zata miki kuma?
Ance ramin mugunta gina shi daidai kai dan haka sai ki bi ahankali Haulat ko ta kife da ke.

~~~~~~~~~~~~~

"Hajiyata"

"Na'am ƴar aljanna yadai

"Ina son zuwa yawo ne,

"To wa kike so ya kaiki?

"Ya Naufal a'a direba

"Direba ko Naufal"

"Naufal.

"je ki shirya bari na ƙirashi|

Tashi tayi ta hau sama,gurin kayanta ta nufa tana tunanin wani iri zata sa,tamfa ta ɗauko me ruwan maron da Ash da pink da brown a jikinta amma brown din yafi yawa.

kayan sun mata kyau ainun ga mayafinta brown tayi kyau kamar saman alale.

~~~~~~~~~~~~~

Kasan cewa Naufal bai sama kanshi son Aure a ranshi ba yasa har yaje india ya dawo bai taɓa sex da wata ba,amma tunda ya fara mafarkin yana saduwa da wata wacce bai san ko ita waye ba ya fara son aure kamar tsiya yanzu ko kiss yaga anyi sai yayi wanka.

Ita kama Haulat macce ce mai mugun sha'awa duk kawaicin Naufal saida ta sa ya fara biye mata suna taɓe taɓe da lashe-lashe yana jin sauƙi sosai idan ya je gurinta.

Kamar dai yadda ya saba yin mafarkin saduwa da wata yau ma hakan ne,jikin shi har ɓari yake yi ɗan tsabar sha'awa,cikin hanzari ya tashi yayi toilet wankan tsarki yayi,ya fito wayarshi ya ɗauka number Haulat ya shiga kira ringin ɗaya yayi ta ɗauka shi ya fara magana cikin wata irin murya

"Hello dear!

Saida tsikar jikinta ya tashi dan jin irin muryar da yayi maganar da ita.

Ita ma cikin irin muryar ta ce" my kana buƙata ne ka zo ni a shirye nake daman kai ne ka ƙi yarda"

Saida sparm ya fito mishi dan tsabar sha'awa cikin harɗaɗiyar murya ya ce mata "No Haulat mu ƙara hakuri har lokaci yayi zan zo yanzu"

Haulat bata ji ɗaɗin maganar shi ba,dan yadda take jin sha'awarshi shi baya jin sha'awarta duk wani jan hankali da dubara tana mishi akan ya yarda amma yaƙi daga yaji yana kokarin biye mata sai ya tureta ya ja motar shi ya dawo gidan,dan Naufal yana jin tsoran zina a rayuwarshi baya son ya aikata ta.

Cikin ɗauki da zumuɗi ya fara shiri saida ya ƙara yin wanka sanan,wasu ƙananan ƙaya ya ɗauko masu kyawun gaske ash colour sun mishi kyau yana cikin saka takalmi wayar shi tayi ƙara jin ringin ɗin dadyn shi yasa ya ɗau wayar da sauri haɗe faɗin "Assalamu alaikum"

"wa'alaikai sallam Naufal yi sauri yanzun nan ka je gidan hajia zasu fita kai so ke son ka kai su kayi sauri sun shirya kai suke jira"

Bai tsaya jiran amsar shi ba ya katse wayar.

Jifa yayi da wayar yana jin wani irin mugun takaici a fili ya ce "Wani irin abu ne wanan kuma duk wanan mara kunyar yarinyar nan ce Sabreen ita zata ce ni take son na kai su dan ta raina ni"
~~~~~~~~~~~~~

Hhhh allah sarki yana sauri yaje ya rage zafi gurin Haulat Sabreen zata  hanashi.

Ranshi a ɓace ya tashi ya ya ɗau key ɗin motarshi rai a ɓace sai hura hanci yake yi ,a ranshi ya ce "Zan gyara miki zama Sabreen sai kin yi dana sanin cewa ni zan kaiki"...

wai ke kuwa sabreen kin ɓuture kowa yana son ɗaukar fansa a kanki.

Idan kuma ta afka da su shikenan.

Ranshi a ɓace ya isa Gidan,yana shiga falon ya hangota da irin kalar kayan shi ranshi ya ƙara ɓace,ji yake yi kamar ya janyota yayi  mata mugun duka.

"Sai dai ka mutu dan baƙin ciki amma ni ba zan chanja kaya ba,kuma sai ka kaimu yawo"

Sabreen ta faɗa a zuciyarta tana watsa mishi harara ta gefan ido.

Hajiya ta kalle shi ta ga yana ɓata rai ta ce mishi"Kai Naufal nifa ban san irin haka idan ba zaka kai mu ba,ai da ka gayama wanda ya turoka ,ka zo kana baɗa rai kamar wanda aka yima wani laifi"

Banza yayi da ita,shi a tunanin shi bata sonshi ko kaɗan,dan kullum cikin tsungama da faɗa take mishi

Jiri Sabreen ta fara ji amma dan tsabar ƙarfin hali haka suka fito ita ce a gaba ma,duk dan ta bashi haushi yasa ta hau gaban motor tana murmushin ƙarfin hali.

Har sun fita daga layin su,cikin Sabreen ya fara murɗawa tun tana daurewa har ta kasa  wani rikitaccen ihu ta sake.

"Innalilahi wa'inna ilairaji'um shi ta fara faɗa.
"Waiyo allah na hajiata faɗawa kan jikin Naufal tayi da sauri ya taka burkin motar ya tsaya a ruɗe.

Hajia kuwa har ta fara kuka tsabar ruɗewa.

Ai motor ta musu ƙarama dan yadda Sabreen ki juyi tana birgema a ruɗe Naufal ya ɗauko ta kamar ƙaramar yarinya suka fito waje,ƙanƙame shi tayi tana ihu mai ratsa zuciya.

Gaba ɗaya ta kashe mishi jiki dan yadda ta maƙalƙale shi gaba ɗayan ƙirjin ta manne su a nashi ƙirjin.

Ganin ta fara ɗauke numfashi ya ƙara ruɗa su,cikin azama da zafin nama ya sunkuce ta,bayan motar yasaka ta hajia ta shiga,a kiɗime yake jan motar da gudu.

Allah yasa basu da nisa da Special Hospital,suna zuwa likita suka amshe ta da gaggawa aka kaita emergency.

Gaba ɗaya hajia ta ruɗe sai kuka take yi "Waiyo allah na Sabreen karki barni dan allah da me xanji ga rashin mahaifin ga naki"

Naufal ya janyota jikin shi a hankali cikin sigar lallashi ya ce mata "Kiyi shiru hajia ba abinda zai sameta kiyi hakuri"

Duk irin lallashin da Naufal yayiwa hajia taƙi hakuri,sai yanzun ne yaƙe ƙara tabbatar da mugun son da hajia ke mata.

Bayan minti talatin likitan ya fito,hajia tana ganin ya fito ya nufe shi da sauri tana kuka ,cikin kukan ta ce"Liki...likita ƴar...

"Zamu iya ganinta,Naufal y faɗa ganin hajia ta ƙasa magana.

"Eh zaku iya ganinta ,yaew ka same ni a office"

"okk tnx"

Tun kafin su gama magana hajia ta shige,tana shiga ta ganta a kwance an saka mata drip da alamun barci take yi,kusa da ita hajia ta je tana kuka ta shafa kanta ta ƙasa magana.

Kallonta Naufal yayi tundaga ƴan yatsun ƙafarta har zuwa fuskarta,ɗan guntun murmushi yayi ganin fuskar ta ɗauke da annuri duk da kasancewar barci take yi,tsintar kanshi da jin mugun tausayinta yayi,tuno yadda take da tsiwa da ƙarfin hali amma gata kwance," hmm banda ciwo da yaushe yarinyar nan zata ƙanƙame ni kamar zata haɗe jikinta da nawa guri ɗaya"
ya faɗa a zuciyarshi cike da jin tausayinta.

"To meke damunta?

Wanan tambayar da yayi wa kanshi ita ta tuno mishi da kiran da likitan ke mishi.

"Hajia bari naje gurin likitan ,bai tsaya jin cewarta ba ya wuce.

Zaune yake a cikin office ɗin likitan bayan sun ƙara gaisawa likitan ya jefu mishi tambaya"
Kwana nawa take yi idan tana al-ada kuma duk bayan wata nawa take yi"

Zare ido Naufal yayi dan bai san ta inda zai fara bashi amsa ba.

Murmushi likitan yayi ganin halin da yake ciki,sanan ya ce "ba kaine mijinta ba"

Da sauri ya ce"A'a ni yayan ta ne"

"ok to ina mahaifiyarta"

"Mahaifiya ya faɗa a hankali cikin rashin sanin amsar da zai bada.

"A gurin wa take zaune" likitan ya ƙara jefo mishi wanan tambayar.

"Hajia bari na kirata"Naufal ya faɗa y miƙe tsaye ya fita jiki a mace"

Yana zuwa ya ga hajia zaune kusa da Sabreen ɗin tana kuka,tausayin sabreen ya ƙara ji.

Sai yanzu ya tuno da bai gayama su momy ba,wayar shi ya ɗauko  ya kira momyn ringin ɗaya tayi momy ta ɗau wayar.

"Hello momy muna asibiti fa Sabreen bata da lafiya"

"innalilah wa'inna ilairaji'un momy ta faɗa a ruɗe.

"Wani asibitin?

"Special hospital.

Yana faɗa ta katse wayar.

A tare suka zo asibitin ita da Farrah,har lokacin sabreen bata tashi ba.

Har gurin ƙarfe goma na dare,Naufal ya so ta farka yana nan,amma taƙi haka  nan suka dawo gida,Haulat ta kira shi yafi sau biyar bai ɗauka ba ,bai ma ga kiran ba dan a motor yabar motar.

Yana isa ɗakinshi ya kirata ya sanar da ita abinda ke faruwa,bata ji daɗi ba,shi kanshi ya nuna mata bai ji daɗi ba.

Ƙarfe goma sha ɗaya Sabreen ta farka,ta ganta a gadon asibiti tuno abinda ya faru tayi tsaki ta ja tuno yadda tayi wa Naufal ranta ta ce"Yanzu zai raina ni"  🤣ji bala'i irin na Sabreen.

~~~~~~~~~~~~~~

Tunda sassafe Naufal ya tashi kamar yarda ya saba dai mafarkin nan yau ma hakan,wanka yayi sanan ya shirya,zama yayi yana duba computer tarshi.

kiran Dady ne ya shigo da sauri ya ɗauka haɗe da sallama,faɗa dadyn ya fara mishi mai yasa
~~~~~~~~~~~~~~

bai gaya mishi Ankai Sabreen asibiti ba.

Naufal yayi mamaki  irin son da suke yiwa Sabreen.

Ƙarfe tara suka shirya suka tafi asibitin har lokacin Sabreen bata tashi ba,dady ya ruɗe ganin halin da Sabreen ke cike.

Shi da hajia suka je gurin likitan  tambayar hajia yayi awata nawa take al-ada,Hajiar ta ce mishi"takan kai wata uku ko huɗu ko biyar bata yi bayi ba,amma idan ta fara takan yi kwana bakwai"

Likitan ya ce "To gskeyi dole  idan har ana son ta daina wanan matsanaicin ciwon ciki a mata aure.

"Aure! hajiar ta furta a hankali.

Alhaji ya kalli likitan ya ce "to mun gode sosai ya miƙa mishi hannu,sanan suka fito jiki ba ƙwari kowanne da abinda yake tunani a ranshi.

Har lokacin Sallah Sabreen bata tashi ba,Naufal bai so ba,bayan sun tafi sallah ta farka da ƙyar ta samu ta ci abinci sanan tasha magani ta ƙara kwanciya.

Kwana nan Sabreen Ukku a asibiti aka sallame su,har lokacin ba su haɗu ba,Kuma dady ne yakai su gida.

~~~~~~~~~~~~~

Cikin sky blue ɗin material riga da sikit sun mata kyau matuƙa,tafiya take yi tana yanga kamar zata ƙarye dan yadda ta ke rangwaɗa ga dugun takalmi ta saka a bakin glass,tana isa cikin glass ɗin ɗaliban suka tashi tsaye.

"Goodmorning Aunty Haulat!

Saida ta zauna ta gama iyayinta da yamutsa fuska sanan ta amsa musu.

Kamar yadda ta saba koyar da su cikin iyayi da kilibibi yau ma hakan tayi.

Tunda ta shigo cikn ajin ta ke wurga ido ko zata ga Sabreen amma bata ganta ba,tayi mamaki da bata ganta ba,har ta fara tunanin ko latti zata zo nan ma shiru ba amo ba labarin Sabreen a makaranta.

~~~~~~~~~~~

kwance take akan cinyar hajia ,kallon film ɗin idia take yi ,ita kuma hajiar tana shafa mata kai.

"Kitsonki ya tsufa Ƴar aljanna"

"Uhmm nifa bana son kitson nan,hajia gobe zanje makaranta"

"Me? bazan barki ba  sai kin ƙara jin sauƙi haka kawai

Hankalinta ya karkata ga film ɗin da take kallo,dariya ta fashe da ita.

Daidai lokacin ya sako kai cikin falon" Kin samu lafiya kenan" ya faɗa a ranshi a fili kuwa cewa yayi "Assalamu alaikum" cikin muryar shi wacce ya saba magana da ita.

ƙamshin turaran shi taji da sauri ta ɓata rai kamar ba wacce ta gama yin dariya ba.

Hajiya ce a amsa mishi fuska ɗauke da annuri.

Saida ya zaunan sanan ya ce "Ina kwana hajia ya me jikin?

bai jira amsawar hajia ba kalli Sabreen yadda yaga  tasha guno ya bashi dariya aran shi ya ce "yarinya ce ke" a fili kuwa ya ce "Sabreen ya jikin? yana wani yatsina fuska kamar yadda ya saba.

Hajiar ta ce "Lafiya lau mutan india ya kokari"

"Alhamdullah!

Ganin Sabreen bata da niyyar amsawa yasa hajia ta ce mata"Ƴar aljanna yana miki ya jiki,baki ga ɗawainiyar da yayi ba yayi kokari sosai"

"Da sauki ta faɗa ko kallan inda yake bata yi ba"

Shima bai bi ta kanta ya  tashi haushin kanshi ya fara da haushinta ta samu yana gaishe ta amma zata mishi haka.

"Hajia bari na tafi momy tana gaida ku,tana faɗa ya bar falon a fusace da ƙudirar ba zai ƙara mata magana ba.

~~~~~~~~~~~~~~

Hau ma haka Malama Haulat ta isa cikin ajin bata ga Sabreen ba.

Bayan an tashi har mutane sun fara watsewa ita tana nan daman jira take yi a watse ɗin.
~~~~~~~~~~~~~~

Wani ɗan matashi ne da dukkan alamun ma'aikaci ne a makarantar,kusa da ita ya matso wani ƙazamin kallo tai mishi sanan ta ce "Yau ma bata zo ba,amma nasan zata zo,ka tabbatar da kayi yadda na faɗa maka kana ji na ko

Murmushi yayi ya ce" Ai ko fyaɗen kike son nayi mata zanyi ni ba abinda ba zan iya ba akan kuɗi"

"No idan kai mata fyaɗe asirin mu sai tuno za'a gane dan iyayenta manyan mutane ne ba zamu iya ja da su,kawai kayi yadda na ce ma,ina son ta tozarta ta wulaƙanta gaban mutane a nan kuma nasan kurar ta za'ayi a makarantar,ta ƙarasa maganar tana murmushin mugunta.

"Waw kanki na ja Haulat"

~~~~~~~~~~~~~

Kissing ɗin juna suke yi cikin zaƙuwa da ɗauki ta ko ina a jikinta yake kissing wanda ita ta bashi damar hakan dan ita ta cire rigar jikinta,ƙokari take yi ta cire mishi wandon jikin shi,cikin mugun zafin nama ya tureta da ƙarfi har saida ta ɗan bugu ta murfin kofar.

Gaba ɗayan ilahirin jikin shi rawa yake yi ga idanuwan shi sun chanja kala a yadda yake ji ba zai iya tabuka komai ba,amma da yake zuciyar na buguwa da ƙarfin tsoro ta haddasa mishi ƙarfi,wanda hakan yasa ya maida rigarshi ya kuma gyara wandon daya kusa fita daga jikin shi.

buɗe motar yayi ya turata ta fita,kai ka ce ba zata ƙara kula shi ba,dan yadda ya turota ɗin duk wacce ke da zuciya a ƙirjinta kuma tana bugawa ba zata ƙara kula shi ba,amma kasan cewar anyi hakan yafi a ƙirga yasa nasan sai ta ƙara kula shi.

Jan motor shi yayi da ƙarfin gaske yabar nan a kasa.

~~~~~~~~~~~~~

Da Sauri ta tashi a firgici sakamokon mafarkin ta tayi Naufal ya tsareta da idanowan shi yana mata wani mugun kallo.

A fili ta ce "ta allah ba taka ba kurwata tafi ƙarfin ka" kamar yana ganin tayi maganar haɗa murguɗa baki da harara.

Zaukowa tayi jikinta duk ya mutu toilet ta shiga ta watsawa kanta ruwan sanyi.

Bayan ta fito da saka kaya mara nauyi duguwar riga ce baƙa tayi mata kyau sosai ko mai bata tsaya shafawa ba ta sauko ƙasa.......

.....................................................................
[12/9, 1:11 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт Ву Gяσυρ O F Hурє Hαυѕα Nσνєℓѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/9, 1:13 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*Dedicated*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

---

Page 6

---

_*Manzon Allaah(ﷺ)* *ya ce;{IDAN KANA DA HALAYE HU'DU, TO KAR KA DAMU DON KA RASA WANI ABU NA DUNIYA; TSARE AMANA, GASKIYAR MAGANA, KYAWUN HALI, SASSAUCI A CIN ABINCI.}*_

```[Sahihut Targib;1718]```

_Duk wanda Allaah Ya azurta da Wa'yannan halayen guda hudu to ya samu arzikin Duniya da Lahira, kada ya damu don ya rasa wani abu na Duniya, don ya riga ya samu abubuwan da suka fi alkhairi. Allaah Ya azurta mu da su. Allaahu a'alam._

```Allah ta'ala yasa mudace```

Na gode na gode sosai da sosai allah yabar kauna ke ɗin dai ta hannun daman batula.
.

Ba kowa a falon,daman tayi tunanin hakan dan tasan lokacin da Hajia ke zama a falon,zama tayi akan kujera ta kunna tibi,gaba ɗaya hankalin ta ya koma akan film ɗin da ake yi.

"Ƴar Aljanna" da ƙarfi Hajiya ta kirata.

A tsorace ta juyo "Na'am Hajiya ta"

"Sai kiran ki nake yi,ki zo na baki abinci"

cikin shagwaɓa ta ce"Na ci da kai na,yanzu na girma ba sai kin ɗinga bani abinci ba"

"To ni baki girma a guri na ba"

Dariya tayi sosai sanan ta ce" na sani  ni yarinya ce a gurikin ki,kuma bana son na girma a gurinki , amma a idanan wasu kallon  yarinya suke min,kuma ni na girma,a zuciyarta ta ce "Irin su Naufal"

Cikin shagwaɓa ta kwanta jikin Hajiar ta ce"Hajia gobe ina son zuwa makaranta"

"To Ƴar aljanna allah yakai mu da rai da lafiya"

"Amin hajiyata"

~~~~~~~~~~~~~

Ko da ya isa gidan nasu ba kowa falon yaji daɗin hakan dan duk wanda ya ganshi a irin wanan halin yai yayi zargin wani abu.

Yana shiga ɗakin shi ya faɗa bayi ya shiga ya daɗe a bayin yana zubawa kanshi ruwa kafin ya fito daga bakin.

Kan gadu ya faɗa yana kallon sama a hankali yake lumshe idanuwan shi haɗe da sauke wata irin ajiyar zuciya ,a hankali ya buɗe baki ya ce" Why! Why Haulat idan kina min hakan  wata rana ba zan iya control ɗin kai na ba"Runtse ido yayi,ya san halin mahaifin shi,da irin tarbiyar daya bashi.

Ya daɗe a hakan kafin barci yai awan gaba da shi.

Duniyar mafarki ya faɗa,bari na bishi na ɗauko mana rahuto..🏃‍♀️

Wani guri ne mai mugun kyau wanda tsayawa rubuta yadda tsaruwar shi take faɗa lokaci ne.

"Meye sa kike tafiya ki barni bayan kin ɗanɗana min zumarki wacce ki sa na fita haiya shi na"

Murmushi naga tayi  sanan ta ce "Kai ne baka shirya zama da ni ba"

Idanuwan shi suka kaɗa sukai ja,ilahirin jikin shi ya mutu,yanyo ta yayi jiki ba ƙwari ya shiga kissing ɗinta " uhmm....huuum.. na shirya zama da ke,ki zauna da ni ba zan iya rabuwa da ke ba....sanbato yai tayi kamar sabon kamu.

Sunyi nisa sosai har ya fara gigicewa,ta fara jan jikinta tana faɗin "Kabar ni" ita kanta da ƙyar tayi maganar.

"kar...k..kar...min..h..hak.. kasa yin maganar yy dan numfashin shi yana kokarin ɗaukewa,hawaye ne ya fara bin kyakyyawar fuskarshi har sautin kukan yana fiɗa.
~~~~~~~~~~~~~

Ita kuwa ƙara janye jikinta take yi daga na shi,faɗa ya fara yi da numfashin shi yana faɗin"karki min haka!!!!!

Da sauri ya farka da kalmar "Karki min haka" ga numfashin shi yana harɗewa,kokarin daidaita numfashin ya fara yi,ya daɗe kafin ya samu numfashin ya daidaita,wata irin nannauyar ajiyar numfashi ya fara yi,dafe kanshi yayi haɗe da runtse idanuwanshi.

Yana jin wani irin abu yana yawa a zuciyarshi,ko kaɗan bai ji daɗin  mafarkin ba.

Ya ɗau sama da minti talatin yana sauke ajiyar zuciya kafin ya samu ya shiga toilet nan ma ya daɗe yana watsa ma jikin shi ruwan sanyi kafin yayi wankar tsarki ya fito.

Yana fitowa kiran Haulat ya shigo wayarshi har ta kusa katse sannan ya ɗauka shiru dukkan su suka yi,daga bisani ta ce mishi a hankali cikin wata irin murya wacce tasan tana kashe mishi jiki"Naufal dear!

Saida ya runtse ido sanan ya ce mata shi ma a hankali "Yess dear!
Kina son mu faɗa halaka koh?

Taɓe baki tayi kamar tana kallon shi"Ba halaka ba ne ,kawai dai muna ɗan rage zafi ne,kuma ai aure zamu yi to meye"

 Hura hanci yayi a ranshi ya ce"Ban san da wani yare zan fahimtar da ke ba Haulat"

A fili ya ce"Haulat mu manya ne kuma muna da addini ya hana mu zina,wanan abun da kike kokarin ki ga munyi zina ce"

Taɓe baki take yi ,ta tsana wanan wa'azin da yake mata,dan ma karya ishe ta ce "Eh gani nan,dear momy tana kira na later" tana faɗa ta kashe wayar haɗe da jan tsaki a fili ta ce "Ni ban taɓa ganin handsome guy kamar ka ba,gashi a india kayi karatu amma duk a banza tunda baka waye ba"

To idan baka mutu ba zaka ga abubuwa wai yanzu fa idan mutum mai aikata zina bai waye ba tirrr allah ya tsare ya tsare zuciyar mu amin ya rahimm.

~~~~~~~~~~~~~

Duk da kasancewar ta tashi jikinta ba ƙwari amma haka nan ta fara shirin makaranta,bayan ta shirya tsabb na kafa mata ido wata ba ƙaramin kyau kayan suke mata be.

Ƙasa  ta sauko tana saukowa taga hajia ɗauke da plate a hannun ta murmushi Sabreen tayi,saida ta ƙaraso sanan ta ce "Ni da kaina zan ci "
~~~~~~~~~~~~~

Murmushi hajiar tayi "inah ni zan baki"

Zama tayi a hannun kujera dan ta san halin hajiar.

"Yauwo ko kefa ƴar aljanna" hajiyar ta faɗa sanan ta fara bata abincin ta shi kaɗan sanan hajiyar  tai mata rakiya har gurin motar.

Tun kafin su isa makarantar gaban Sabreen ya fara faɗuwa bata kawo komai a ranta kuma bata ba abin wani muhimmanci ba balle  tayi zargin wani abu.

Kasancewar ta je da wuri ba mutane sosai yasa ta zama ita kaɗai a class,rubutun malam Haulat da ta gani a jikin allon ne yasa ta tuno da ita,dan Sabreen bata da riƙo ko kaɗan shi yasa ɗuk abinda aka mata sai ta rama dan karta riƙe mutum.

Murmushi tayi a filli ta ce"Su malama Haulat ƴan kilibibi manya,ina fah kika iya kilibibi ai kilibibi sai Ya Naufal"
Dariya tayi tuno yadda yake gudanar da al-amuranshi.
Tana cikin tunani ƴan ajin suka fara isowa kowa tambayarta ya ke yi lafiya ,suna son Sabreen dan ta iya abin dariya gashi bata gani ta ƙyalle sai ta tanka.

Cikin ƴanga da iyayi da kilibibi Haulat ta shigo ajin,gaba ɗayan su suka miƙe tsaye suka gaida ita harda Sabreen dan yanzu bata riƙeta ba.

Kamar yadda suka saba gani sai ta gaya abinda ta ga dama sannan ta amsa musu gaisuwa yanzu ma hakan ne,har Sabreen zata zauna dan ta gaji da tsayuwar Haulat ta ce su zauna.

Haulat na miƙewa ta hango Sabreen wani daɗi taji murmushi tayi ta taka har gurin Sabreen ɗin ta ce"Sabreen ya ƙafar ko ita ce ta hanaki zuwa makaranta kwana biyu"

Ita ma murmushi tayi ta ce"No kike cewa ko?

"to No ba ita ba ce"

Murmushi Haulat tayi a ranta ta ce"Yarinya kenan wai da ni zaki ja"
A fili ta ce"Okkk

Tana faɗa ta juyo gurin allon kamar yadda ta saba karantar da su haka yau ma tayi,bayan ta gama ta fita tana murmushin mugunta.

"Hello kana ji na yau ta zo,ka shirya lokacin break ni kuma zan san yarda zanyi ta fito.

"Okk baki da matsala Haulat"

Ana kaɗa musu ball masu fita suka fara fita dan Sabreen ita bata zuwa break.

Tana Zaune tana fira da ƙawayanta wata yarinya ta shigo ta ce "Ina Sabreen muha'd mai taƙama?

kallon yarinyar tayi ta ce " gani wake naima na,wani uncle ɗin ku ne yana waje" yarinyar tana gama faɗa ta fita daga ajin.

"Toh gani nan zuwa"ta faɗa bin bayan yarinyar tayi ,tana fita bata ga yarinyar ba,tafiya ta fara yi tana  waige-waige.

Yana ganinta ya nufu ta,ga gurin ba mutane sosai,bata lura da zuwan shi ba,kawai sai taji ya bangaje ta,wani abu ja me irin jan jini ya watsa mata.

"Innalilahi wa'inna ilairaji'um Sabreen ta faɗa tana kallon jikin ta.

"Subhnanllah! yi hakuri ban kula ba,mu je dan allah ki wanke kar ya kama uniform ɗinki.

Ba musu kuwa ta bishi har wani ɗaki me kama da office,suna shiga ta tsaya mamaki ya kamata ganin yana cire rigar jikin shi,wani irin nishi ya fara yi.

Gaba ɗaya Kan Sabreen ya ɗaure bata gane abinda yake yi ko nufi ba,shi kaɗai yake wani irin abu,dan akwai tazara a tsakanin su da shi ma.

ƙwanƙwasa ƙoka aka fara yi,kallon kofar take yi tana kallon shi,da ƙarfi aka buɗe kofar aka shigo wani uncle ne mara mutunci  wani irin kallon mamaki yake mata"Me zan gani daman haka kike"

Cikin rashin fahimtar inda zancen shi ya nufa ta ce"Haka nake kamar ya"

"Rufe min baki ƴar iska kawai daman haka kike"ya daka mata tsawa.

"Iskanci!" ta faɗa cikin rashin sanin inda zance ya nufa.

"Dallah karki wani nuna baki san komai ba yau asirin ku ya tuno"

"Waiyo allah na shiga ukku wllh yau ne kawai kuma yau ɗin ma ba muyi koma....

Tsalla rufe min baki yau sai kun bar makarantar nan.

Gaba ɗaya kan Sabreen ya ɗaure ta kasa gane abinda suke nufi kalmar iskanci ya duki zuciyarta.

jiki ba ƙwari kamar wacce aka yiwa dukan tsiya ta ce "Ƴau ne kawai ku....

Tun kafin ta ƙarasa maganar taji zaukan  Wani wawan mari wanda ƙarar saukar shi ya tsayar mata da jin magana,ga hawaye ya ƙasa xubuwa.

Hannunta ya ja har office ɗin principal ɗin,har suka isa bata jin abinda suke cewa.

Suna shiga daman su huɗe ne malama suka gaya wanan mara mutunci ne ya ce mishi "A ɗakin sani naani su ka kama su suna iskanci"

Wanan kalmar ita ta  duki kunnan Sabreen zuciyarta ta buga ta karfin haske sai yanzu hawaye suka samu damar zubuwa.

A  ruɗe principal  ya ce "What! yana kallon ta no it c...

"Ya isa haka ki kwantar da hankalin ki Naufal ya zama naki"

A zuciyarta ta ce" Hmm Malama Haulat  kenan ba kin ce naje na aure jahili ɗan ƙauye iri na ba,to zaki ga jahili ɗan ƙauyen,zan iya yin komai dan ɗaukar fansa akan ki,dole na aure miki shi kuma ya zauna da ni"

"Ƴar Aljanna ya isa haka bana son jin kukan ki,kiyi shiru kinji"

"To Hajiyata zanyi shiru"

"Yawwa ko kefa"

"Hm Malama Haulat sai kinga ramuwar gaiya,wacce zata tsorata ki ,ta ɗaga miki hankali" a zuciyarta take wanan maganar.

Sun daɗe a ɗakin kafin suka fito falo suka zauna,hajiyar ta kalleta ta ce"Bari naje na kira Alhaji"

"Toh kawai ta ce mata.
  can ƙasan zuciyarta tana jin tsoro ya Naufal zai ɗauke maganar tasan baya sonta ita ma bata son shi ko kaɗan hali da ra'ayin su ba ɗaya ba,amma guguwar ɗaukar fansa ta hana ta yarda da jin tsoran yadda abuvuwa zasu kasance,ta ɗaukar wa kanta komai rintsi komai wuya sai ta ɗau fansa.

~~~~~~~~~~~~~~

Xaune yake a cikin office ɗin shi yana duba wasu muhimman takardu,kiran hajia ya shigo wayar shi,da sauri ya ɗauka haɗe da tattara dukkan hankalin shi,cikin girmamawa da biyayya yai mata
~~~~~~~~~~~~~~

sallama.

"Wa'alaikum salam"

"Hajia ya gidan ya Sabreen?

"Muna lafiya

"Ya jikin na ta?

"Jiki yayi sauki,ina son muyi wata muhimmiyar magana da kai idan ka tashi ka biyo"

"To shikenan zan biyo insha allah!

"Yawwa allah ya kawo ka lafiya

"Amin.
ita ta fara katse wayar.

~~~~~~~~~~~~~

Cikin sigar jan hankali take mishi magana"Dear meyasa kake min haka ne,kasan irin son da kishin da nake maka kuwa,kasan yadda naji da ka katsi min waya kuwa"

Kamar wanda ke koyan magana ya ce"Haba haulat meyasa kike da zargi ne,na kaya miki wata ƙan wata ce ta ɗau wayar ,kuma bata iya amfani da wayar ba shiyasa ta katse"

"To bata iya amfani da waya ba kuma"

"yes village girl ce ya fada had'e da ta'be baki.

"me ya haɗa ka da wata village girl kuma? ba wanan ba yaushe zaka zo?

numshe idanuwan shi yayi ,yana son zuwa gurinta tunda yana sonta,amma yana jin tsoran abin..

"Wai meyasa kake gudu na ne,ta katse mishi tunani.

"Ba gudunki nake yi ba dear ,ina son na yiwa zuciya faɗa ne"

Ɗan guntun tsaki ta ja"Kana ɗai gudu na kamar wata maiya anya kana sona kuwa"

"ina sonki Haulat"
~~~~~~~~~~~~~

Saida tsigar jikinta ya tashi dan yadda yayi maganar gaba ɗaya feeling ɗinta ya tashi.

Cikin sigar da tasan zata ja hankalin shi ta ce"prove it!

katse wayar yayi dan ya tabbata idan ta cigaba da mishi magana a haka ba zai kai labari ba,kashe wayar yayi ma, dan yasan zai ta kara kira tunda maiyace anace🤣.

~~~~~~~~~~~~~

Gaba daya ya rasa natsuwar shi tunda sukai magana da hajia, ƙarfe da ƙyar ya tsaya yayi salar maqrib a office ɗin,cikin gaggawa da hanzari ya iso gidan su hajiyar.

Suna zaune a falo ƴar aljanna tana kan cinyar hajia kamar yadda ta saba indai suna tare da ita to a kan cinyarta take kwanciya.

"Assalamu alaikum"

Sabreen tana jin sallamar shi ta miƙe
Hajia ta amsa mishi sallamar,yana ƙarasowa yayi gurin Sabreen ɗin fuska ɗauke da Annuri ko wani irin yanayi yake ciki idan yaga Savreen zai yaji farinciki.

"Sabreen ya jikin ki"
kanta a ƙasa ta ce"yayi sauƙi Dady"

"Alhmdllh! allah ya ƙara miki lafiya Sabreen"

Hajia ta katse shi da faɗin"ƴar aljanna je ki ɗaki"
"to kawai ta faɗa ,ta tashi ta hau sama ,duk da tasan dady ba zai ƙi amincewa ba amma saida ta tsinci kanta da faɗuwar gaba wanda ta rasa dalilin yin shi.

Bayan sun ƙara gaisawa ta kalle ta ce"Alhaji kana jina koh?

"Eh ina jinki hajiya"

"Yawwa to,tun lokacin da likita ya ce ayi wa Sabreen aure na shiga tunani da wa za'a haɗa ta,tun a lokacin Naufal ya faɗomin a rai ,domin bana son mu ba wani wanda bamu sanshi ba,kar ya cutar da marainiyar allah,amma zai ban nufe ka da maganar ba,kuma kai ma nasan kayi irin nawa tunanin ,duk ba mu san muyi mata dole shiyasa ba muyi wa juna maganar ba"

"Wanan haka ne hajia kuma ɗazun malamin makarantar su ya kira ni ya shawurce ni akan muyi mata aure"
~~~~~~~~~~~~~

"To alhmdllh! Allah yaga zuciyar mu ya ga kuma tsoran mu,yau tana dawo wa daga makaranta da tabbatar min da tana son Naufal"

Wani irin farinciki ya mamaye alhaji"masha allah alhmdllh,hajia allah ya dube mu,daman muna tunanin ko ba zata so shi ba,amma abin allah gashi tana son shi,ba ƙaramin daɗi naji ba,cikin gaggawa kuwa za'a ɗaura auran nan"

"Yawwa ni kaina naji daɗi mara misaltuwa,yanzu zai a tsaida ranar auren.

"To kwana nawa kike ganin ya kamata a saka"

"To bari mu sai gobe idan munyi magana da ita"

Hmm tofah ana wata ga wata,ko ya naufal xaiji idan yaji maganar auren shi da Sabreen,ga kuma mutumiya haulat.

Bayan ya tafi hajia ta shiga gurin Sabreen ɗin ,a kwance ta ganta tayi lamo kamar me barci,tana jin an buɗe kofa ta tashi zaune,kusa da ita ta zo ta zauna.

"Ƴar aljanna bana son ganin ki kina damuwa Naufal ya zama naki,yaushe kika so a ɗaura muku auren?

Dumm dumm zuciyarta ta fara buguwa wani irin abu zuciyarta ke bijiro mata da shi me kama da tsoro,amma dan tsabar ƙarfin hali irin na Sabreen ta ce"Sati ɗaya,A'a kwana huɗu ranar juma'a kenan,sati ɗayan ya mata yawa.

"To baki  da matsala yanzu ai a fara shiru"

"Hajita ina son a tsara bikin nan sosai irin na ƴaƴan gata"

"ke ƴa gata ce Sabreen karki ji komai ko da ɗukiyar alhaji zata ƙare akan yasa ki farinciki zai kashe,za'a haɗa biki irin wanda sai ƴaƴen manya ƴan gata"

Wani irin farinciki ya mamaye Sabreen ,amma a ƙasan zuciyarta tana jin wani iri.

~~~~~~~~~~~~~

Ko da dady ya koma gida suna zaune a falo suna fira.

duk da sun san dady da fara'a amma yau kuwa sunyi mamakin ganin irin fara'ar da ke fuskarshi kamar wanda akai wa bushara da aljanna,zama yayi suka yi fara sosai sai ƙarfe goman tare kowa ya tafi ɗakin shi.
~~~~~~~~~~~~~

"alhaji wai yau naga kana cikin wani irin farincike ne"

murmushi yai mata  sanan ya ce" hmm wani irin abu ne kike ganin zai sani irin wanan farincikin"

"eh to abu ɗaya ne zuwa biyu na farko dai magana akan Savreen na san ko...

da sauri ya katse takYawa uwar gida,ma tso kusa na baki labari"

Ba mutsu ta matso"to ina jikin ka

Saida yai gyaran murya ya kara natsuwa sanan ya ce"Kin san lokacin da likita ya ce ayi wa Savreen aure hankali na ya tashi akan da wa zana haɗa ta wanda sai riƙe ta da amana yaji tausayin maraicinta"

"Haka ne ni kai na abin yana damu na domin Sabreen abin tausayi ce"

"To allah ya ga zuciyar mu,ita da kanta ta ce tana son Naufal kinga faɗuwa ta zu daidai da zama,yanzun mun kama magana da hajia daman ba wanda ta cancanta da ya aure sabreen sai shi,kuma cikin satin nan za'a ɗaura auren nan"

Ba ƙaramin daɗi momy taji ba,dan tana son Sabreen tana jin tausayinta,amma abin da ya ɗaure mata kai daya ce wai Sabreen ta ce tana sonshi,a iya ganinta basu shiri dan ra'ayin su bai zo ɗaya ba.
  "To Naufal yana sonta kuwa?

"Tunanin me kike yi?

Murmushi tayi ta ce"Naji daɗi sosai da sosai amma shi Naufal ɗin ka ji ta baki....

Da sauri ya katse ta da faɗin"Ba buƙatar jin tashi Sabreen ƴae uwarshi ce dole ya sota yana ma sonta,idan jar jinin jiki na ke yawo a jikin shi,to na Sabreen ma yana yawo a jikin shi,kuma idan har yana so na to yana son Sabreen,kuma kar yaji wanan maganar sai ranar da za'a ɗaura aurank

Ganin rance ya fara ɓace yasa tai saurin tarar shi cikin sigar lallashi ta ce"Ba wai ina nufin wani abu ba ne,ina nufin ya kamata ace ya san da maganar ne...

"To idan bai sani ba ,wani abun zai yi?

Shiru tayi dan taga alamar ya hau sama,tashi tayi ta fita a ɗakin....

lallai Sabreen saboda ɗaukar fansa zaki aure wanda baya sonki baki son shi.
.

Sir Dboy
[12/9, 1:13 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт Bу Gяσυρ O F Hуρє Hαυѕα Nσνєłѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/16, 5:46 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

............................................

_*YAWAITA SALATI GA ANNABI S.A.W ARANAR JUMA'A*_
➖➖➖➖➖➖➖➖
_*Annabi s.a.w* yana cewa: (Yana cikin mafificiyar Ranakunku Ranar Juma'a, dan haka ku yawaita yin Salati agareni acikinta, domin ana bujuromin da salatinku gareni)._
_*@Saheehu Abu Dauda.*_

_*Annabi s.a.w* yace: (Duk wanda yayi salati a gareni, *Allah* zaiyi masa salati Guda Goma)._
_*@Saheehul Jami'i*_

Page 7
____________

Kallon Sabreen ɗin yake yi cikin mamaki,ya ƙasa yarda da abinda aka gaya mishi dan yanayin ta ba irin na matan nan ba ne,ga kuma hawayen da yaga tana yi.

"Dan Allah kayi hakuri karka kore ni,bamu taɓa yi ba sai yau.

Kamar wata wawiya ta juyo ta kalli shi,tana hawaye.

Shi kanshi principal ɗin kan shi ya ɗaure  ganin yadda sani nani yake magana,gashi ita ta kasa cewa komai.

"Daman ba tun yau ba nasha ganin ta tana zuwa toilet ɗin maza" cewar wani mai aikin makarantar.

Kallon shi cikin mamaki da tsoro Sabreen tayi, duk bakin Sabreen yau naiman shi tayi ta rasa.

"A hukunta su daidai laifin da ta aikata" cewar uncle ɗin maths ɗin su wanda shi ma yana cikin office ɗin.

Kallon su kawai Sabreen ke yi tana zubarda zafafan hawaye zuciyarta na ƙuna.

Saida yaja numfashi sannan ya ce" ku bani guri zanyi magana da ita"

Basu su hakan ba musamman sani nani shi da yaso jin hukunci da wulaƙancin da za'a mata,amma haka nan suka fita.

Kallonta yayi cikin jin tausayi ya ce"Sabreen mai ya faru?

Sai yanzu kuka mai sauti ya kamata,kuka mai tsuma zuciya ta fara wanda tunda ta zo duniya bata taɓa yin irin shi ba.

"Kiyi magana ganin ba zata yi ba yasa ya ce mata" to ya isa hakan.

A zuciyarshi y ce" kukan ki ya tabbatar min da baki aikata komai ba,amma dole zan yi hukunci dan dukace amma tabbas zan rufa miki asiri ba zan tuzarta ki ba"

Wata ƙararrawa ya danna alamar su shigo,cikin zuguɗin abinda zai faɗa suka shigo.

Kallon su yayi ya ce "Kamar yadda duka ta tanadar za'a gayama iyayenta sannan a koreta daga makaranta,amma ba zan koreta ba,zan dai gayama iyayenta sanan bana son jin wata ƙaramar magana na,kai sani ya kalle shi

"Kai ne abin ji wallahi idan har iyayenta suka ji wanan labarin ka bani,baka san matsayin su ba ne,balle ta tabbatar mu da ƙarya kake mata,ba kai ba har makarantar gaba ɗayanta ka ja mata kalle ta ya nuna Sabreen ɗin wacce dan tsabar kuka jikinta ya mutu yayi tiɓiss.
Sanan ya ɗaura da faɗin"Hm kai kasan komai,ni bani da abinda zan ce a cikin ku waye ma gaskiya ,amma abu ɗaya tabbas idan har iyayenta suka ji kai ne mara gaskiya dan sai sun hukunta ka.

Jikin sani yayi sanyi tabbas yasan bashi da gaskiya ko kaɗan.

Kallon shi principal ɗin yayi yaga yadda jikin shi ya mutu sanan ya ce"Hmm zaka iya taimakon kanka ta hanyar ƙin gayama kuwa dan wllh idan ka yarda iyayenta suka ji wanan mgnr ka kaɗe"

Kallon sauran malaman yayi ya ce musu"Ku kuma nasan kun waye mahaifinta kuma kun san abinda zai iya to wllh ku rufama makarantar nan asiri domin idan ba haka ba,kun san abinda zai biyo baya,kuma wllh duk idan naji wani yayi kokarin gayan wata magana a bakina aikin shi"

Gaba ɗayan su jikin su yayi sanyi dan sun san mai taƙama,musamman sani.

"Kuma abinda yasa ba zan koreta ba ,dan gudun kar ayi zargin wani abu,ina fatam kunji abinda na gaya muku da kyau"

"Eh munji suka faɗa a tare sanan kowa ya gama gaban shi.

Har suka gama magana suka fita Sabreen na kuka.

"Sabreen na san ƙarya ya miki,yana da wata manufarshi na yin haka,shiyasa ba zan matsa sai ya gaya ba domin idan nayi hakan wasu zasu ji daɗi,shiyasa na rufe musu baki,sanan ke kuma kiyi hakuri tunda kin san baki aikata komai ba,plsss Sabreen kiyi hakuri kuma karki gaya ma kuwa abinda ya faru harda gidan..

Sai yanzu Sabreen ta samu bakin magana cikin shekar kuka ta ce"Ban...s..san..abin..da..suk...ke..magana...b...n rantse da girman allah bansan...

"Ya isa haka ya ƙatse ta,na sani shiyasa na ce ki kwantar da hankalin ki,idan kika nuna danuwa waɗan da suke son ganin kin tuzarta daɗi zasu ji"

Allah sarki Sabreen baiwar allah ko kaɗan bata kawo Haulat a ranta ba,bata ma yarda wani zai iya mata hakan ba dan yasa ta wulaƙanta tabar shi a matsayin an samu kuskure.

Ya daɗe yana lallashin ta,har lokacin an kusa tashi ma,sanan yasa ta shi toilet ɗin office ɗin ta wanke fuskarta,ta wuce classa
ɗin su.

Number Alhaji ya fara naimo wa cikin sa'a kuwa ya ganta ya danna kira,ringin ɗaya tayi ya ɗauka.

"Assalamu alaikum Alhajn ya faɗa.

"wa'alaikum sallam Alhaji ya gida ya kokari ya iyalai.

"Alhamdulilah komai lafiya

"Mash allah! Alhaji daman ina son yin wata magana ne akan Sabreen"

yana jin ya kira sunanta ya natsu ya tattara dukkan hankalin shi"ina jinka lafiya take dai ko"

"Lafiya qalau take daman shawarace zan baka da wasu malaman suka lura suna ganin ya kamata ayi wa Sabreen Aure"

Zaida Alhaji yayi jim kaɗan shi ma bai kawo komai a ranshi ba dan likita daman ya gaya musu suyi mata aure.

"Ba komai insha allah daman nasan da zancen auren ina wani shiri ne dan Sabreen bata kula

maza ni kuma bana son yi mata dole"

Ba wani fahimtar maganar yayi ba ya ce"to haka ne kam  za'a mata dole ba"

A haka suyi sallama.

Ita kuwa Haulat ta kasa kunne taji labari ya fara yawo amma shiru bata ji komai ba gashi bata ga sani ba,gashi har an tashi gida.

Duk wanda yasan Sabreen idan ya ganta yau sai ya gane chanji ƙarara dan fuskarta a ko yaushe ɗauke da annuri amma yau kuwa ba annuri ba alamar shi sai ma yanayin ƙunci da ya baiya na a fuskar.

Tana tsaye tana jiran direba,kanta a kasa idanuwanta cike da hawaye dan ba abinda ya taba ɓata mata rai a duniya irin wanan abun taji zafi kamar me.

🤧lallai akwai aiki kuna ganin idan Sabreen ta gane aikin haulat ne zata iya hakura?

Cikin salon yanga da iyayi da kinibibi Haulat ta fito daga office ɗinta,hango Sabreen da tayi yasa tayi murmushin mugunta musamman da ta hango yanayin da take ciki.

Sabreen bata san Haulat ta matso kusa da ita ba sai ji tayi ta ce"My illiterated student! yadai

Ƙasa ce mata komai tayi dan bata cikin yanayin.

Ganin hakan yasa Haulat murmushi tana ganin kamar tayi nasara ta ce"Tun kafin a baiyana abinda kuka aikata har kin shiga wani irin hali.

Cikin rashin fahimta  Sabreen ta kalleta.

Murmushin mugunta Haulat tayi ya ce"Yess! baki kina tunanin zaki iya ja Haulat ba har kika sa aka bani suspension,to bari ki ji ni na haɗa komai na biya sani,ke ba kin sa an bani suspension ba,ni kuma zan sa a wulaƙanta ki ,ki tozarta ki kunyata kuma a koreki  a makarantar sanan a gaya ma iyayenki abinda kika aikata, daman baki son karutu ke jahila ce sai  a haɗa ki da jahili ɗan ƙauye irinki,dan ko mai washe bola ba zai iya auren ki ba"

Wasu irin zafafan hawaye ne suka fara bin fuskar Sabreen zuciyarta na ƙona tana mata radaɗi.

Ganin halin da take ciki yasa Haulat farinciki cikin dariyar mugunta ta ce"Hmm ja da Haulat ba irin ki ba jahila ƴar kauye kuma yarinya,hmm karki wahalar da kwakwalwarki gurin yin tunanin zaki iya ɗaukar fansa akai na yarinya domin ni ba tsararki ba ce,tana gama faɗa wushe tabar Sabreen tsaye da zafin zuciya.

Hmm ikon allah yau Sabreen baki ya mutu🤣.

Wani irin kuka mai tsuma zuciya ta fashe da shi,daidai lokacin direban ya iso ,tana ganin shi ta ruga da gudu ta buɗe motar ta shiga tana kuka.

A ruɗe yake tambayarta lafiya dan ko a mafarki bai taɓa tunanin akwai abinda zai sa Sabreen irin wanan kukan ba.

Suna isa gidan ta buɗe motar ta fito da gudu a falo ta hango hajia zaune gurinta tayi ta faɗa kan jikinta tana kuka,a ruɗe Hajiar ke tambayarta"Lafiya Sabreen ke da waye???????

A ranta ta ce" *NI* *DA* *MALAMA* *TA*.

Tsananin kuka ya hanata magana.
Hajiya ta ruɗe tana faɗin"Na shiga ukku ke dawa me ya faru wa ya taɓa ki,ko baki da lafiya ne????

charab ta ce"Bani  da lafiya

Ai hajia sai ta ƙara ruɗewa ta ma rasa abinda zata yi,ganin hakan yasa Sabreen,faɗin "zan kwanta ki kaini ɗaki na"

A ruɗe hajiar ta tallabo ta suka hau sama,suna shiga ɗakin Sabreen ta kwanta hajiar har ta rufe ta.

Amma Sabreen bata
daina kuka ba tuno kalaman malama Haulat take yi,tana jin zafi a zuciyarta.

Ganin hankalin hajia tana ƙara tashi yasa ta daina kukan ta fara yin na zuciya,tayi lamo kamar tayi barci,tana jin hajia tana ta maganganu,A haka har barcin ya ɗauke ta.

~~~~~~~~~~~~~

A hankali ta fara jin muryar hajia da na Momy da na farrah,bata ji muryar shi ba amma ƙamshin shi ya tabbatar mata yana nan,a hankali ta fara kokarin fuɗe ido domin taga a inda ta ke.

Akan hajia idonta ya saura dakin da mutanan da ke ciki ta fara ƙarewa kallo,ɗakinta ne,chan daga bayan su akan kujerarta ta hango shi fuskar nan kamar kullum a yatsine.

Sannu suka mata ɗaga musu kawai kawai take yi.

Momy ta kalle shi ta ce"Naufal baka ga ta farka ba"
~~~~~~~~~~~~~

Bai ce mata komai ba ya ƙaraso gurin tana ganin shi da juya kanta.

Taɓe baki yayi ya ce"Ya jikin?

Ɗaga mishi kai kawai tayi,bai damu ba,ya koma ya zauna ta gefan ido yake satar kallon ɗakin ,ɗakin ya mishi kyau ga wani irin ƙamshi irin wanda yake ji a jikinta,ya shagala gurin satar kallon ɗakin.

Momy kalleta ta ce"Ƴar aljanna bari mu barki ki samu ki watsa ruwa"

Bata ce bata komai ba suka tashi suka fita yana jin hakan ya riga su tashi,kash saidai ya manta da wayarshi a hannun kujerar da ya tashi a kai.

Hajia ta kalleta ta ce"Zaki iya wankan"

Murmushi tayi ta ce a hankali "zan iya"

"To ki kula kinji"

Kai kawai ta ɗaga mata,hajiar ta fita.

Tana ganin sun fita ta sauko daga kan gadon ,ta cire kayan makarantar ta ɗaura towel,har zata shiga bayi ringin ɗin waya taji kalle-kalle ta farayi charab idanta ya sauka akan wayar Naufal ɗin wacce ya manta da ita a ɗakin.

Ƙarasa gurin tayi tana faɗin"Garin ya ya manta da wayarshi a ɗaki na?

Tana kai hannu ta ɗau wayar ,tsaro idanu tayi tana ƙara tabbatar a abinda idanuwanta suka ga ni.

"Malama Haulat! ta faɗa ita ɗince pic ɗinta ne ya baiyana a gaban wayar har kiran ya katse Sabreen bata sani ba ,dan mamaki ƙara shigowar ringin ɗin ne ya dawo da ita daga duniyar mamakin abinda ba abin mamaki ba ne.

Katse wayarta"Malam haulat ita ce kenan"

Wani kiran ya ƙara shigowa a fusace ta ƙara katse kiran.

"Ya Naufal ne wanda keke mugun so daman"

Jin tafiyar mutum yasa tai sauri ta ajiya wayar ta faɗa toilet ɗin da sauri.

Farrah ce ta shigo ɗakin ta ɗauki wayar daya aikota ta ɗauko mishi.

"Sabreen zamu tafi amma anjima zamu dawo momy tayi baki"farrah ta gaya tana kallon toilet ɗin,bata tsaya jiran amsar Sabreen ɗin ba ta fita daga ɗakin dauke da wayar a hannunta.

"Malma Haulat"

Ta faɗa tana tuno kalaman da ta gaya mata.

kamar wace abu ya tsikara tayi zumbur ta mike ta ɗaura towel ɗin ta fito,tana fitowa hajia na shigowa,tana ganin hajiar ta fashe da kuka mai tsanani ta faɗa kan gadon.

A kiɗime hajia ke tambayarta"Lafiya Sabreen ki gayamin abinda ke damunki ko meye shi zan miki maganin shi"

Cikin kukan ta ɗago kai ta kalle hajia ta ce"Ya Naufal na ke so,kuma ya Aure ni"

Ba hajia ba ni kaina saida taji wani yarr

"Naufal kike son aura

"Eh kuma a wanan satin" Tana faɗa ta ƙara fashewa da kuka.

Cikin sigar lallashi hajiar ta ce"Kiyi hakuri indai Naufal ne ya zama naki ke kaɗai kuma ko gobe kike so za'a ɗaura muku aure!

tirƙashi!!!

😱😱 waiyo me kike shirin aikatawa Sabreen duk ɗaukar fansar ne!!
.
Dboy
[12/16, 5:46 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт Вy Gяσυρ O F Hypє Hαυѕα Nσvєℓѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚[12/16, 5:35 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

بسم الله الرحمن الرحيم

_*Manzon Allaah(ﷺ)* *ya ce;{KAYI ALKHAIRI, KUMA KA BAR LAIFUKA. ALLAAH ZAI

MAYAR DA LAIFUKAN KA(NA BAYA) BAKI 'DAYA SU ZAMA ALKHAIRI.}*_

```[Sahihut Targib;3164]```
~~
_Duk mutumin da Allaah Ya azurta da halin kirki ya rin'ka aika alkhairi, kuma ya guji aikata sabon Allaah, toh sai Allaah Ya mayar da laifukansa na baya ma su zama masa alkhairi. Allaahu a'alam._

```Allah ta'ala yasa mudace```

_*سبحانك اللهم وبحمدك, أشهد أن لا إله إلا أنت، أستغفرك وأتوب إليك.*_

Page 8
......................................

Kamar yadda ya saba yin mafarkin yau ma hakan ne,
Ya kai tsawon minti ashirin yana nazari akan mafarkin wanda yanzu abun ya fara tsorata shi, dan saidai idan har bai kwanta ba, amma sai yayi mafarkin ta.

Tashi yayi ya shiga toilet  ya daɗe yana watsa ma kan shi ruwa kafin ya samu yayi wankan ya fito.

Cikin jallabiya baƙa ya shirya ,ta mishi kyau ainun,ga ƙamshi da ke tashi a jikin shi saboda yawan saka turare yasa ko mai shafa ba,jikin shi yake ƙamshi.

Kallon agogon bangon dake ɗakin yayi ƙarfe tara na ranar laraba,ya mutsa fuska yayi haɗe da hura ɗan ƙaramin hancin shi,wayar shi ya ɗauko ya kunna,yana kunnawa saƙonnin Haulat suka fara shigowa,shefar da wayar yayi haɗe da jan tsaki.

Gaban shi yai mummunan faɗuwa jin ringin ɗin kiran Dady da sauri ya ɗauka murya a harɗe ya ce"Assalamu alaikum"

Cikin jin daɗi da annashuwa Dadyn ya ce"Wa'alaikum salaman"

"ina kwana dady

"Lafiya lau Naufal baka tashi ba ne?

"Na tashi dady

"To ka fito ina jiranka a falo"

"to ganin nan zuwa ,tun kafin ya rufe baki ya tashi ya fito,a ranshi yana tunanin me yasa dadyn

nashi cikin farin ciki tsakanin jiya da yau,sanin ba zai iya bawa kan shi amsar ba yasa shi ya bar maganar.

A Falo ya same su,da dukkan alama suna cikin jin daɗi,shi ma aro annuri yayi yasa wa fuskar shi,xai da ya zauna sanan ya kalli momy cikin kulawa ya ce "Good morning

"Morning Naufal

Farrah ma ta ce"Ka tashi lafiya Yaya Naufal"

"Lafiya lau"

Allah sarki momy tana son Sabreen amma bata son ya aure wacce baya so,dan ƙiyayyar namiji bala'ai ne.

A tare suka yi breakfast cikin son da ƙaunar juna,bayan sun gama Dady ya kalle shi cikin kulawa ya ce mishi"Naufal tashi muje yau akwai abubuwa masu muhimmanci da xamu yi"

Cikin rashin fahimtar abinda dadyn ke nufi ya ce"To Dady A office ne?

"A'a wanan yafi aikin offfice tashi dai mu tafi"

A ranshi ya fara tunanin wani irin avu ne wanda yafi aikin su mahimmanci.

"Gidan hajia zamu fara zuwa"

"to Dady ya faɗa ba komai a ranshi.

~~~~~~~~~~~~~

Zaune take akan tanƙameman gadonta ,gaba ɗaya jiknta ya mutu sakamaƙon mafarkin da tayi Naufal ya tsare da ido yana mata wani irin kallo wanda ƙaramar kwakwalwarta ta ƙasa gane ina kallon ya dosa.

"Ina haba Sabreen tun yanzun zaki karaya,dan ɗaukar fansa zaki yi fa,bai kamata ki karaya ba" Zuciyarta ke mata wanan maganar a fili ta ce haɗe da yin murmushi "Sabreen ƴar aljanna ƴar gatan hajia,duk abinda nasa gaba sai nayi shi"

Zuciyarta ta ƙara yin ƙarfi duk wani tsoro da fargaba ya fito,Cike da izza ta tashi tai toilet fuskar nan ɗauke da annuri.

A Falo suka iske hajia ,hajia tana ganin Naufal ta sake wani irin murmushi,ta ce "Mutan India manya Har ka fara ƙamshin    dogon buri"
~~~~~~~~~~~~~

Cikin rashin fahimtar zancen ta ya ce"Ina kwana hajia"

"Lafiya lau,yanzu fah ka ɗau hanya"

Banza yayi da ita tunda shi bawai ya iya hausa sosai ba ne,baya gane magana cikin magana,dan ma su momy suna mishi hausa da ba zai iyata sosai ba,a ranshi ya ce"To yau kuma ita ma naga tana cikin farinciki Sabreen fa?

"Sabreen meye nawa da ita,duk a zuciyar shi yake wanan maganar,ya kas....

"Naufal hau sama ka kira Sabreen"

Hajia ta katse mishi tunanin da yake yi,kallon ta yayi ta sakar mishi wani irin murmushi,kallon dadyn yayi shi ma murmushin yake yi.

Tsaye ya miƙe ya hau saman a ranshi ya faɗin"Meyasa hajia zata aike ni ɗakin ta?

Tura ƙafar yayi,lokacin ta fito daga toilet daga ita sai towel dan ƙarami iya karshi gwiwa.

Jin an buɗe kofa yasa ta juyo"Waiyo!! ta faɗa a tsora ce.

Ƙamewa yayi a tsaye zuciyar shi tana bugawa da karfin gaske kuma ya kasa sauke idanuwan shi da suka kafe akan brest ɗinta,lokaci ɗaya jikin shi ya mutu wani irin bakon yanayi ya fara ziyarta zuciyar shi,wanda ya ke tunanin yafi ƙarfin ya kira shi da sha'awa.

"Laaa.....fiii....y...yaa...me...y..yaaa....k.k..ka.wo..ka.."Ta faɗa a ruɗe.

Bai ma san tana magana ba,dan gaba ɗayan hankalin shi baya tare da ita.

Idanuwan shi ta kalla ai sai ta ƙara ruɗewa ganin yadda suka chanja kala,gashi ta ga nonowan ta ya zubawa ido,A ruɗe ta faɗa kan gadon ta ƙudundune da bargo tana ihu.

Ringin ɗin wayar shi ne yai nasarar dawo da shi haiyacin shi,lumshe idon shi yayi waɗan da suka rine.

Da ƙyar  ya iya sarrafa hannun shi gurin lalubo wayar da ke ringin ɗin,ringin ɗin kiran Haulat daban ne amma saboda tsananin shiga wani irin yanayi bai iya tantance ringin ɗin ba.

ya san ko ya ɗauka ba zai iya magana ba ,yasa ya kasa ɗaukan,ga shi kafafuwan sun mishi nauyin da zai iya saukar da kan shi ƙasa.

Hawaye ne taji sun fara bin fuskarta a hankali ta ce "daman ɗan iska ne! kuma zan aure shi"

Tuno irin yadda taga ya kafe nonowanta da ido tayi haba sai hawaye shaaa kamar an kunna famfo.

Ko kaɗan su hajia basu kawo komai a ransu ba ,daman tayi hakan ne dan suyi magana ita da dadyn.

Jin sheƙar kukanta yasa shi ya ƙasa shigowa ɗakin "Keee ya daka mata tsawa,uwar me kike yiwa kuka,wani abu ne ya faru banza kawai kiran ki aka ce na zo nayi"

Yana gama faɗa ya fita a fusace  ranshi a ɓace,kan me zata yi kuka wani abu yayi mata,ji ƙarfin hali irin na Naufal ko tabarmar kunya dai zai naɗe.

Ai wani sabon kukan Sabreen ta ƙara fashe wa da shi,abinda ya ɓata mata rai tsawar daya ɗaka mata,wacce saida tasa hanjin cikin ta yin kuka,dan tsoro,kuma meye nashi idan tayi kukan,ba shi ne yaja ba"

"Ko me zaka min ba zan fasa aurenka ba,kuma na baka bashin tsawar da ka dakamin amma bazan yafe ba"

Ita kaɗai tai tai maganganun ta,tana kuka.

baƙin glass yasa kafin ya sauko kasan,yana isa hajia ta ce mishi

"Tana ina?

"Gata nan zuwa"ya faɗa cikin wata irin murya,fita yayi daga falon yaji daɗi da dadyn bai hanashi ba ,yaɗai ce mishi ya jira shi a motor

A motor ya zauna ya jingina kai da sitiyarin motor zuciyar shi tana bugawa,kamar wanda bai taɓa ganin makamancin haka ba,yasha ganin mace tsirara amm bai taɓa jin irin na yau ba,ko Haulat tasha ɗaukar  hoto da towel a jiknta ta turomishi,amma yau sai yaji wani irin abu wanda ya kasa ganewa.

"Mtseewww me yakai ido na jikin wanan wawiyar yarinyar yanzu zata raina ni,dan taga irin kallon da na mata mtseww"

Ya faɗa cike da jin haushin zuciyarshi da idanuwan shi.

Hajia da dadyn sun gama magana akan ranar juma'a za'a ɗaura aure,hamshaƙin aure irin na ƴaƴan gata,Sanan sunyi magana akan gidan da zasu zauna da komai da komai,sanan dady ya bata maƙudan ƙuɗi dan yin wasu abubuwan,sanan ya tashi a falo ya tarar da shi.

"Ya Aka yi ne Naufal"

"Ba komai dady ya aro murmushi ya ɗaurawa fuskar shi"

Hoto nan gidaje Dady ya nuna mishi "Wanne yafi kyau Naufal"

Gaba ɗayan gidjen sun haɗu kamar ba'a 9j ba,saida ya tsaba wani madaidaici mai ɗankaran kyau sanan ya nunawa Dady ya ce"Waw dady wanan yafi kyau"

Murmushi yayi sanan ya ce"Sabreen zata so shi ko"

"Sabreen me ya kawo maganar Sabreen a nan kuma?ya tambayi kan shi a zuciya murmushi yayi tuno komai za'ayi sai idan yayi mata sanan ake yi.

"Eh dady zai mata kyau ai yana da kyau"

hhhhh Shiyasa baka da masoya Naufal dan baka gane komai🤣.

Murmushi dadyn yayi "Yawwa.

********

Ganin ta daɗe bata fito ba yasa Hajia ta shiga ɗakin ganin ta a kwance yasa hajiar ta ruɗe"Ƴar aljnna lafiya? ta ƙarasa gurinta da sauri.

Tana jin hajia ta ƙara duƙunƙunewa kamar me barci.

"Ƴar aljanna buɗe mana lafiya"

Cikin irin muryar barci ta ce"Barci nake ji hajia ki barni nayi"

Cikin nuna kulawa ta ce"Kin tabbata barci kike ji"

"uhm.. ta fara kukan shagwaba ta ce"Barci hajia ki barni"

"To ya isa haka,ta faɗa ta tashi ta fita.

*******

Kallon farrah momy tayi ta ce"farrah Naufal zai aure Sabreen cikin satin nan"

"What? ta faɗa haɗe da zaro idon.

"Taya momy Ya Naufal ɗin?

"Hmm nima saida naji wani iri anya kina ganin ba za'a zamu matsala ba kuwa"

"Tabbb gaskiya momy da kamar wuya a ƙi samun matsala dan Yaya ma yana da budurwa"

Jikin momy ya mutu  "Waya gaya miki yana da budurwa farra?

"Yasan da maganar auren?

"A'a me sani ba"

"Hmm to saidai kawai muyi addu'a dan yaya dai baya son Sabreen ita ma ɗin,amma zasu dace ita ce daidai ce,idan ya fara sonta zai chanja,na kam naji daɗi bari ma taje gurinta"

Tana faɗa ta tashi jiki na rawa,ita kuwa Momy jikinta ya mutu tausayin Naufal ya mamayeta,amma ya zata yi.

Cikin zumuɗi da rawa jiki Farrah ta isa Gadan  a falo ta isake hajia ta washe baki ta ce "Hajiya ashe muna da babban biki"

Ita ma hajiyar washe baki tayi "Bari dai farrah zamu sha biki ,ya hajiar ta ku"

"Tana lafiya ita ta gayamin ma,hajia ina  Sabreen"

"Tana ɗakinta barci take yi,amma halan ta farka"

ai tun kafin hajiyar ta gama magana ta haye sama.

Tana isa ɗakin ta faɗa kan gadon"yeeeh Amaryar Yaya,shi ne ba za'a gayamin ba na shirya faty"

Sabreen tana jin Farrah ce ta tashi  yana mutsike fuska cike da ƙarfin hali ta kalle farrah tana murmushi.

Dungurinta tayi akai  tana dariya ta ce "Gayamin yaushe kika fara son mutumin naki?

Bata son ta gaymata dan kar da gayawa hajia,murmushi tayi ta ce"Tun shekaran jiya na nayi mafarkin shi"

Dariya farrah tayi sosai "Ah lallai wato mafarki wani irin mafarki?

"Ke nidai karki ishe ni,da tambayoyi kamar wata ƴar jarida,yanzu dai faty nake so a haɗa.

Ƙara farrah tayi"Yeehhh ai lallai ana son yaya Wai nifa abin mamaki yake ban Wai Sabreen ɗin d na sai ƴar aljanna ƴar gatan hajia wai ita ke son Yaya Naufal ɗan iyayi da kinibibi"

"To meye"

"A'a ba komai duk love ne,amma abin da mamaki fa"

"Ni kidaina mamaki ,ki tsaya muyi magana"

"To na tsaya Aunty Sabreen"

Doka sabreen ɗin ta kai mata"Waye Aunty?

"Sabreen amaryar yaya"

"Ke fa ai"

"Ni me? yaushe ne bikin naji ance cikin satin nan ?

"Jibi!

ƙara farrah ta buka ta haye kan Sabreen ɗin tana ihuu.

"Wai hajia farrah zata kashe ni"

ɗaga ta farrah tayi tana dariya "Lallai Sabreen tun yanzu to gaba wa zaki kira ya taimake ki?

Cikin rashin fahimta ta ce"Hajiata mana"

Dariya farrah tayi sosai ta ce "Akwai wata ƙawar momy tana gyaran jiki na amarya ya kamata momy ta kai mu gobe,abubuwan ne sun matse kamar wata wacce ta ƙagara za'a sa biki kwana ukku,haba ace mai taƙama family zasu aurar da yara biyu yaran ma ƴan gata ace ba abinda za'ayi haba,gaskiya ba zai yuwu ba yadda nake da buri akan bikin wani daga cikin ku"

Ta kai hannu ta doki cinyarta,ƙara Sabreen tayi"Ann Haba farrah ke mugu ce daman"

Dariya farrah tayi ta ce"Tab akwai aiki kuwa yaya zai wahala,to nidai gasky tashi yanzun nan mu je kasuwa,muyi siyayya ya kamata ma kuyi photo fa wanda za'a sa a memo da jaka da wanda za'ayi amfani da shi gurin faty"

Kallon farrah Sabreen tayi "to yanzu ya za'ayi"

"yawwa ina da pic ɗin yaya zai muje ki ɗauka sai a haɗa kamar kunyi tare,daga nan sai muje a

haɗa mana memon da jaka"

"to bari ta saka kaya" ta faɗa tashi tayi daga kan gadon  ta je gurin drower towel ɗin ya zamo.

"Waiyo ni gaskiya Sabreen yaya zai ja kaya irin wanan hips haka"

Cikin rashin fahimtar abinda Farrah ke nufi ta watsa mata harara ta ce"To yanzu ina zamu samu kuɗi?

"Dady zaki tambaya"

harararta ta ƙara "baki da hankali kawai sai na tambaye shi kuɗi.

"Ke nidai yi ki saka kaya kuɗi ba matsala ba ne hajia zata ba mu,momy ma nasan zata ba mu"

Tana sa kaya suka sauko ƙasa farrah ta gayawa   hajia zasu fita su fara shiri,hajia taji daɗi sosai ta basu kuɗi sosai,har zasu tafi ta ce su jera tare zata gurin Momy suyi magana.

Ko da suka isa gurin momy ,momyn tana ganin su cikin farinciki ita ma farincikin ya kamata,musamman da taga Sabreen ta tuno da maganar da dady yayi"Idan har jini na ke yawo a jikin Naufal to jinin Sabreen ma yana yawo ajikin shi zai so ta idan har yana so na"

Hankalinta ya kwanta sosai,ta saka a ranta zai so ta ne.

Ita ma ta ƙara musu kuɗi masu yawan gaske ta kuma kira idan zasu je ai mata makeup sanan a haɗa hotonsu tare,kuma a haɗa komai da komai wanda za'a saka photon,kuma ta ce zata kama tsadaddan holl wanda za'ayi fatyn,sanan suka fito,ita kanta hajia daɗi ya mamayeta ainun.

.
[12/16, 5:35 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт Bу Gяσυρ O F Hуρє Hαυѕα Nσνєℓѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/16, 5:36 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

*By*
*fatima* *Batula*
Page 9

............................................

*_السلام عليكم ورحمة الله وبركا ته_

*_" بسم الله الرحمن الرحيم_

_*ZIKIRAN DA AKEYI BAYAN IDAR DA SALLAH*_
:
.
_*(1)* -“Astagfirullahi” sau uku,(3)_
.
_*(2)*“Allahumma Antas Salam, Wa minkas Salam, Tabarakta Yaa Zal Jalal Wal Ikram”_
_*[Muslim ne ya rawaito shi].*_
:
_*(3)* -“Laa ilaha Ilal Lahu, Wahdahu La sharika Lahu, Lahul Mulku, Walahul Hamdu, Wa huwa Ala kulli Shai’in Qadiir._
.
_*(4)* Allahumma La mani’a lima aadaita, Wala mu’udiya lima Aaxait, Wala Yanfa’u Zal Jaddi Minkal Jadd”_
_*[Bukhari ne ya rawaito shi].*_
.
_*(5)* -“Laa ilaha Ilal Lahu, Wahdahu La sharika Lahu, Lahul Mulku, Walahul Hamdu, Wa huwa Ala kulli Shai’in Qadiir._
_La haula wala quwwata illa billahi, Laa ilaha illal Lahu, Wala Na’abudu Illa Iyyahu, Lahun ni’imatu Walahul Fadlu, Walahus sana’ul Hasan, Laa ilaha Ilal Lahu, Mukhlisina lahudden, Walau karihal Kafiruun”_
_*[Muslim ne ya rawaito shi].*_
:
_*(6)* -“Subhanallah, Wal Hamdu Lillahi, Wallahu Akbar” Sau talatin da uku.33_
:
_*(7)* “Laa ilaha Ilal Lahu, Wahdahu La sharika Lahu, Lahul Mulku, Walahul Hamdu, Wa huwa Ala kulli Shai’in Qadiir”_
_*[Muslim ne ya rawaito shi].*_
:
_*(8)* La Ilaha Illallahu Wahdahu La Sharika Lahu Lahul- Mulku Wa Lahul-Hamdu, Yuhyi Wa Yumitu Wa Huwa ala Kulli Shai'in Qadir.._
_*sau goma(10)bayan sallar Asuba da magariba*_
:
_*(9)* -“Allahumma A’inni Ala Zikrika, Wa shukrika, Wa Husni Ibadatika”_
_*[Abu Dawud ne ya rawaito shi].*_
:
_*(10)* - Karanta ayatul Kursiyyi, da suratul Al-ikhlas, da Falaqi da Nasi *dai- dai.......1 -1*_
_*Sanna (Sau uku-uku)3-3* bayan sallar magariba da asuba_
_*[Nasa’i ne ya rawaito shi].*_
:
_*(11)* - Fadin “Allahumma Inni As’aluka Ilman Nafi’an, Wa zirqan Xayyiban, Wa amalan Mutaqabbalan”_ _*[Ibnu Majah ne ya rawaito shi]*_

_Bayan an yi sallah daga sallar asuba._
:
_An kar6o daga *Aisha – Allah ya yarda da ita*  ta ce, “Manzon Allah ( صلى الله عليه وسلم ) ya kasance yana bude sallah da kabbara, karatu kuma da “Alhamdu Lillahi Rabbil Aalamin”. Hakanan ya kasance idan ya yi ruku’u baya daga kansa sama, kuma baya sunkuyar da shi qasa, sai dai yana sanya shi tsakanin haka. Idan ya dago kansa daga ruku’u baya sujjada har sai ya daidaita a tsaye, hakanan idan ya dago daga sujjada baya komawa sujjada har sai ya daidaita a zaune. Ya kasance yana faxin tahiya a dukkan tsakanin raka’o’i biyu. Hakanan ya kasance yana shimfida kafarsa ta hagu, ya kafe ta dama (a zaman tahiya). Ya kasance ya hana zaman shaidan (zama akan dugadugai), yana hana mutum ya shimfida tsintsiyar hannunsa kamar yadda dabbobi suke yi. Yana qare sallah
:
_*سبحانك اللهم وبحمدك, أشهد أن لا إله إلا أنت، أستغفرك وأتوب إليك.
............................................
kallon Momy Hajiya tayi ,tana murmushi ta ce"Hajiya kinji yadda muka yanke shawara ba mu tambayi ra'ayinki ba"

"Ah haba Hajiya ba komai kun isa ne,kuma shawarar tayi daidai naji daɗi sosai, ubangiji Allah ya haɗa kan su,ya basu zaman lafiya da zuri'a ɗaiyaba"

"Amin ya Allah"

"Bari nima na tashi  ba'ayi biki haka ba,naje nayi siyayya na gaiyaci ƴan uwa da abokan arziƙi"

"To gaskiya kuwa abin ne yazo da sauri"

Bayan sun gama maganar su Momy ta kawo Hajia gidan ta,ita kuma ta wuce kasuwa daga nan ta tafi gidan su gurin iyayan ta.

~~~~~~~~~~~~~

Tun Safiyar ranar da Haulat ta tashi take jin ɓacin rai duk saboda Wayar Naufal a kashe tun jiya da  ya kashe bai kunna ba, da safen ma  ta kira bai shiga ba,ranta ya ɓaci haka nan ta tafi makaranta ranar student sun sha zagi da bala'i ,ganin bata ga Sabreen ba yasa ta ɗan ji daɗi,amma bata ji labarin wani abu ba,akan sharrin da ta haɗa mata ba.

Tun a makarantar ta kira shi yafi sau biyar amma yaƙi ɗauka a lokacin suna tare da dady.

Haka ta dawo gida jikinta ya mutu.

"Haulat wai ke ba zaki ragewa kanki wanan irin mugun son da kika ma wanan mutumin ba"

Saida ta ɗago tai mata  wani irin kallo sanan ta ce"Ni ban san meyasa yaƙi ɗaukar wayata ba
~~~~~~~~~~~~~

tun ɗazun nake kiran shi,ko yana fushi da ni ne"

"Fushen me?

saida taja guntun tsaki sanan ta ce"Shi wani iri ne kamar bai waye ba,ni na ɗauka ma baya sha'awa ne"

"Kamar ya kika ce a india yayi karatu"

"A nan ne ,amma karki ga yadda gudu na,idan kika ga yamin kiss to ba ƙaramar sha'awa yake ji ba,ni haushi nake ji "

"Kai Haulat,yanzu ke da zaki yi alfahari da hakan,kana gani dai kowa burinshi ya taɓaka,amma har ki samu wanda ba jikin ki yake so ba,amma kina wata magana,kin san komai haulat a.....

tun kafin ta ƙarasa maganar ta katse ta"ke allah dan baki ganshi ba ne,amma ina tabbatar miki duk macen da ta ganshi sai taso wani abu ya haɗa su..

"Haulat sha'awarshi kike yi ko sonshi?

"Duka biyu"

"Hm Haulat kenan ni yanzu ƙawarki ce dole na baki sha'awa"

"Yawwa ƙawar Arziƙi mu je ɗaki na"

Ashe duk wanan maganar da suke yi a falo ne.to allah ya kyauta.

Zama suka yi akan gado salma ƙawar Haulat ɗin ta kalle ta tace"Irin waɗan nan mazan a hankali da dubara ake binsu,tunda ya nuna yana jin tsoran wani abu ya faru,to karki matsa mishi ,idan ba haka ba kuwa zai fara ja da baya,hankali xaki haɗa mishi tarko daya faɗa shikenan"

Dariya Haulat ɗin tayi suka taɓa" shegiya ƙawa shiyasa nake sonki,yanzu  ba wanan baki na kira  faisal(tsohon saurayinta) dan a matse nake,yaushe rabo na,nayi ma ƙokari"

"Ke Haulat baki da dama,ni kuwa kinga tun lokacin da na rabu musa(saurayinta)ban ƙara saduwa da wani ba,saidai ƴan abun da ba'a rasa ba,yawwa ban tambayeki amma zai aureki dai ko"

Kallonta Haulat ɗin tayi tai dariya"Aure ni da aure yanzu ina,allah ya kyauta haka kawai na haihu na tsofa,ke ma kin san bani da ra'ayin aure yanzu,shi dai tunda bai waye ba,daya min maganar auren nake katse shi"

Shiru Salma tayi tana mamaki ina da ita ta samu irin wanan damar"Haulat ni kin ban tsoro na ɗauka kin cire wa kanki wanan ra'ayin banzan,Ina jiye miki abun da zai iya biyo baya"

"mtseww na me? ba abinda zai faru"

"hm murmushi tayi kawai suka cigaba da firar su mara amfani.

~~~~~~~~~~~~~

Saida nayi da ƙyar na iya gane Sabreen ban taɓa tunanin tana kyau irin haka ba sai yau,nayi fitinan kyau,makeup ɗin ya amshi fuskarta ainun,cikin wata dugowar riga wacce ta ɗan kama ta,pink da golden colour kalan ya ƙara fito da ita ga ɗaurin ɗan kwalin ,ita kanta rigar abun kallo ce,bayan an gama yin makeup ɗin aka ɗauke ta hoto na,kala-kala,idan ba ita ta gayama ba son auran take yiba,ba zaka taɓa yadda ba,dan yadda ta saki jiki tana zabga fara'a.

Kallon ta farrah tayi tana washe baki"Da yaya ya ganki na tabbata bazai gane ki ba,ko yanzu sai yayi da ƙyar zai iya gane ki balle an haɗa pic ɗin ku"

Murmushi  Sabreen tayi bata ce komai ba,ita yanzu yarda zata haɗu da malama Haulat take yi gashi bata da number ta.

Sunyi yawo sosai da n farrah saida ta je gurin ƙawayanta,ta gaya musu,Da aka haɗa hoton abun ba magana kamar a tare suka yi hoton sun dace sosai ita kanta  Sabreen da taga pic ɗin saida taji gabanta ya faɗa da ƙarfi wanda bata san dalilin faɗuwar shi ba.

Gidan su momy suka sauka bayan sun dawo ita ma lokacin bata daɗe da dawowa ba,taji daɗi sosai musamman da taga an haɗa hoton sai ta ƙara tabbatar da sun dace da juna,ita ma nayi siyayya sosai da kayan da zasu saka da komai da komai.

Ana idar da Sallar maqrib Su dady suka dawo,a lokacin suna zaune a falo suna fira akan bikin,Da sallama suka shigo,Sabreen tana jin muryarshi gabanta yai mummunan faɗuwa.

Ko kaɗan bai kula da Sabreen tana nan ba,dan shi ba mutum ba ne mai kalle-kalle ba,har suka iso falon suka zauna bai kula da ita ba.

Dady ya kula da ita tun isowar shi ɗakin yana zama ya kirata"Ƴar aljanna zo nan"

Jin dady ya kira sunanta yasa ya ɗago kai da sauri haɗa ido sukai wani abu ji ya soki ƙirjin shi,da sauri da kau da idonta,a harɗe ta ƙaraso gurin dadyn kanta a ƙasa ,hannu ta Dady ya riƙo yana murmushi ya ce"Ƴar aljanna ya kike"

Kamar me tsoron magana ta ce" lafiya qalau"
~~~~~~~~~~~~~

"Momyn ku ta gayamin kun fita ke da farrah ,kunyi siyayya,kuɗin sun isa ko kuna buƙatar wasu?

"Am..dam..sun is..

Charab farrah ta ce"Eh dady ba mu gama ba,kuma sai maganar holl ɗin da za'ayi...

"Eh baku da matsala da wanan zanyi komai ni da yayan duk mun shirya komai"

Ko kaɗan Naufal bai gane ba,mamaki yake yi,wani abu xa'ayi..

Bai ƙarasa yin tunanin shi ba Wayar Momy ta fara ringin duk hankalin su ya koma gurin ta.

Ganin mai kiran yasa momy tayi murmushi ta kalli Dady shi ma murmushin yayi,ɗaukar wayar tayi.

"Assalamu alaikum,Haba hajia tun kafin Ayi Auran zaku rike min ita ,yanzu idan aka yi auran shikenan"

"A'a hajia ba haka bane,kin san basu dawo da wuri ba ne,kuma...

"To naji yanzu dai ku turomin ita"

Tana gama faɗa ta kashe wayar.

Dady ya kalle ta yana murmushi ya ce"hajia ku"

ya juyo ya kalli Naufal ya ce"Naufal kai Sabreen gida"

"Toh"
Kawai ya faɗa Amma ranshi a ɓace baya son raini Sabreen kuwa ƴar raini ce,bai tsaya jiran wani abu ba ya fito daga falon yana hura hanci.

Momy ta ce "zo nan Sabreen"

A kunya ce ta isa gurinta,zaunar da ita momyn tayi kusa da ita "Sabreen ki kwantar da hankalin ki kinji,gobe da sassafe zan zo ni da Farrah mu fita,ki tashi da wuri dan da safe zamu zo"

"To momy"

"A'a ya zaki ce ta tashi da wuri"

Murmushi momy tayi ta kalle shi ta ce" hmm tafi abinki Sabreen yana jira ki gaida hajia"

"To saida safen ku"

"Yawwa ki tashi lafiya suka faɗa a tare.

A hankali take tafiyar har ta isa gurin motar shi,gaban motar ta buɗe ta shiga,bata ce mishi komai ba.

"Mtseww! ya ja tsaki Sabreen ta tsani tsaki a rayuwarta,bata san lokacin da ita mata ta ja tsakin ba.

A fusace ya ɗago kai,hannun shi yakai kan lips ɗinta masu taushin gaske ya tsungule su da kunbar shi,ƙara tayi da ƙarfi ta ce "Waiyo hajia"

"Wa kike wa tsaki ni tsaranki ne,hajia ko kirata ta zo"

Jin xafi yasa ta cije shi a hannu ,yaji zafi ya cire hannun shi da sauri.

Kallonta yayi ya kalli hannun shi inda ta cije shi ɗin,bai ce mata komai ba yaja motar suka fita daga  cikin gidan su,sai da ya raba tafiyar tsakanin gidan su da gidan su hajiar sanan ya tsaida motar,ganin ya tsaida motor yasa ta ce"Me muka tsaya yi a nan ,ni ka kaini gida"

"Ke ba kin raina ni ba,ni kike so ki maida direba ko,janyo ta yayi jikin shi,ya rungumeta  wani irin abu yaji yarr tsigar jikin shi ta tashe  wani irin shuƙi ya kama shi ,bai taɓa tunanin zaiji wani iri ba,da ko kaɗan  baiyi karanbanin haɗa jikin shi da nata ba,ya raina Sabreen ne,kallon kwaila yake mata.

lokaci ɗaya ya tsinci kanshi cikin wani yanayi gashi ta ƙasa natsuwa sai goga mishi dukiyar fulaninta take yi a ƙirjin "Waiyo Allah na hajia ,ka sake ni ,ka sake ni,bana so ni ba ƴar iska ba ce"

Da sauri ya sake ta,yana maida numfashi sama-sama shi kaɗai yasan abinda yake ji,"Meye yasa nake jan abinda xai sa yarinyar nan ta ƙara rainani? wanan tambayar yake wa zuciyarshi yana me jin haushin zuciyar shi

Jan motor yayi da gudu nan da nan ya isa gidn,yana tsaida motor ta fito da ƙarfe ta tura motar"Allah ya isa"

Tana faɗa ta wuce tana tafiyarta hankali kwance.

Dokan kujerar yayi inda ta tashi haɗe da jan wani dogun tsaki yana jin tsanarta a ranshi.

**********

" Alhaji gobe  ya kamata ka gayamishi tunda zai ga mutane sun fara zuwa"

Cikin tausasawa ya kalleta ya ce"Xan gayami shi,ki kwantar da hankalinki nasan Naufal ba zai ja da ni ba,ban taɓa saka shi abu yaƙi yi ba komai girman abun,nasan zaiji wani iri amma na ɗan ƙankanin lokaci  ne"

A haka ya kwantar ma hajia hankalin.

~~~~~~~~~

"ohhh ni Allah ƴar aljanna tun yanzu zaki fara min haka"

Idanuwanta tabb ta kwalla ta ce"Hajia ba zan iya nisa da ke ba,ko yaushe zan kasance tare da ke,wa gare ni banda ke,hawayen da suka maƙale suka gangaro.

Ita ma hajiar kuka  ta fara yi haka suka kwana suna kuka.

~~~~~~~~~~

Haka ya koma gida jikin shi a mace yana ƙara jin tsanar Sabreen,  amma wata zuciyar tajin shauƙin yadda take abubuwanta kai tsaye ba tare da jin shakkar komai wai ta kalli shi ta ce mishi allah ya isa, shi mamaki ma abin ya bashi, kashe wayar shi yayi gaba ɗaya.

Yau ma irin mafarkin nan yayi,tashi yayi yana keta zufa,haɗe da sauke nannauyan numfashi "Idan har haka zaki dunga min ki daina zuwar min mafarki" ya faɗa kamar wanda yake jin tsoron maganar,wankan tsarki yayi ,sanan ya fita zuwa masallaci salar asuba,yana dawo wa ya shige ɗakin shi,wayar ya kunna,sakonin Haulat ne suka fara sintirin shigowa,number ta ya kira,tayi ringin tayi har ta katse bai iya kira sau ukku ba iyaka biyu shi ma idan ya matsu yake yin shi.

~~~~~~~~~~~~~

"Yanzu taya xan haɗu da Malama Haulat gashi bani da numberta kuma ban san gidan su,dole na haɗu da ita,numberta ya kamata na samu"

Hajia ta shigo ta ganta ita kaɗai a zaune kan gado tana magana ita kaɗai "Sabreen ke dawa?

Juyowa tayi ta kalli hajiar a ranta ta ce" *NI* *DA* *MALAMA* *TA*

"eyyah ki dawa kike magana ki kaɗai?

Murmushi tayi ta ce"Hajia ba kowa ina tuno wani abu ne"

"Meye shi?
~~~~~~~~~~~~~

"Hmm Hajia ta ba komai "

" to na yarda tashi ki je kiyi wanka ,yanzu xaki ga su Momyn ku"

"Toh tana faɗa ta tashi ta faɗa toilet"

~~~~~~~~~~~~

Tana farkawa ta duba wayarta ganin kiran Naufal yasa ta ruɗe ta shiga kiran shi da sauri,a lokacin yana ɗakin shi yana duba laptop din shi kiran ta ya shigo yana jin ringin ɗin ya ɗau wayar
ita ta fara magana"Hello dear lokacin ban tashi ba,kuma wayar bata kusa da ni sai yanzu na tashi"

"ok ba komai,kin tashi lafiya?

"Lafiya lau,meyasa kake min haka dear,dan ina sonka shine na cancanta irin wanan wulaƙancin"

cikin sigar lallashi ya fara bata hakuri"ba haka ba ne,duk lokacin ina tare da Dadyne mun fita.

"to  shikenan bana
 iya fushi da kai ko kaɗan"

A haka suka cigaba da fira cikin so da ƙaunar juna.

Suna gama wayar Dady ya kira shi yace mishi ya fito falo,yayi mamaki bai ga su hajia ba ya kalli dadyn ya ce"Dady ina zu hajia naga ban gansu ba?

"Eh sun fita zasu je gurin su Sabreen wai zasu je gurin gyaran jiki"

Murmushi yayi ya ce"Mata ƴan kwalliya"

Gyaran murya Dadyn yayi ,ya ƙara gyara zama ya tattara dukkan hankalin shi gurin Naufa ya ce"Naufal ka natsu kaji abinda zan faɗa maka da kunnan basira"

Yadda yaji Dadyn yayi maganar yasa ya tattaro dukkan natsuwar shi yai ƙasa da kai "Ina jinka Dady"

"Naufal Naufal Naufal,Sau nawa na kira ka?

"Sau ukku!
~~~~~~~~~~~~

"To ina son ka ji avubuwa ukku da zan gayamaka,ka ɗauke su ka saka su a cikin kwakwalwarka da tunaninka"

Zuciyar shi ta fara buguwa da ƙarfin gaske kamar zata fasa ƙirjin shi ta fito.

"Abu na farko Naufal ni na haifeka kuma ina sonka ina alfahari da kai,baka taɓa faɗa min rai ba ,ko na saƙon ɗaya kullum cikin bin umarni na kake,wanan dalilin yasa na son na tausasaka akan hukuncin da na yanke akan rayuwarka ba tare da naji naka ra'ayin ba,Naufal gobe zan ɗaura ma aure da  Sabreen

Dumm Dumm zuciyar shi ta fara buguwa da ƙarfin gaske wanda tai nasarar sandarar da tunanin shi komai ya tsaya mishi chikkk ,sai zufa da take keto mishi ta ko ina a jikin shi,gashi ya kasa ɗaga kai ya kalle Dady.

"Ban san ra'ayinka akan ta ba,Naufal da wanan nake cewa kayi hakuri.

"Abu na biyu Naufal Inhar ka ɗauke ni uba to ina so ka ɗauke Sabreen a matsayin matarka kuma ƴar uwarka,ko kaɗan karka nuna mata ƙiyayya idan ka nuna mata ƙiyayya ban yafe maka ba..

A zabure ya ɗago kai da jajayen idanuwan shi ya kalli Dadyn na shi.

"Sabreen ina sonta fiye da yadda nake son ka,idan ka cutar da ita ko bayan ba raina ban yafe maka ba,Naufal,kuma idan har ka ɓata mata rai ta zubda hawaye Naufal ban yafe ma ba.

"Sai Abu na ukku wanda shi zan roƙe ka akai ,idanuwan shi sukai jajir muryarshi ta fara rawa abinda bai taba faruwa ba kenan tunda Naufal yazo duniya bai  taɓa jin mahaifin shi a irin wanan raunanniyar muryar ba.

"Naufal dan allah dan annabin Rahma Naufal ka riƙe amanar marainiyar allah nan,ba dan hali na ba...

"Dady...dad..dady ka..

"A'a naufal wanan ba umarni ba ne,roƙan ka neke yi,Sabreen amana ce a guri na,zan danƙa mata ita,Naufal ka riƙe ta amana.....

.

[12/16, 5:36 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσsт Bу Gяσυρ O F Hуρє Hαυsα Nσνєℓs Bσσк Wнαтsαρρ 08064400100_ 📚📚

[12/16, 5:41 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*
Page 10
.................................................

*_السلام عليكم ورحمة
الله وبركا ته_*

*_*بسم الله الرحمن الرحيم*_
_*Manzon Allaah(ﷺ)* *ya ce;{IDAN ALLAAH YAYI NUFIN MUTANEN WANI GIDA DA ALKHAIRI, SAI YA MUSU JAGORAR (SAKA) 'KOFAR SAU'KIN HALI(A GIDAN).}*_
°
```[Silsilatus Saheeha;523]```

_Duk gidan da suke da saukin hali to lallai Allaah Ya na nufin su da alkhairi. Arziki ne babba mutum ya siffantu da saukin hali. Allaah Ya azurta mu da shi. Allaahu a'alam._

```Allah ta'ala yasa mudace```

_*سبحانك اللهم وبحمدك, أشهد أن لا إله إلا أنت، أستغفرك وأتوب إليك.*_

...............................................
Kasa ƙarasa maganar Dady yayi,jikin shi ya mutu ga kwalla ta cika mishi ido.

Cikin wani irin yanayi Naufal ya ce "Dady baka yarda dani ba ne, Dady komai girman abu zanyi shi idan har ka saka ni yinshi k....

"Ba haka nako son ka ce ba Naufal ina son naji ka ɗau alkawarin da zan baka ne"

Cikin raunanniyar murya Naufal ya ce"Na ɗau alƙawari zan riƙe Sabreen,zan kula da ita kamar yadda zan kula da kai na,ba zan bari wani abu ya faru da ita ba,nayi alkawari"

wata irin raguwar ajiyar zuciya Dady ya sauke"Kasan daraja da muhimmanci alƙawari ,ba sai na tunatar da kai ba.

"Naufal tun farkon rayuwarka kake min biyayya,amma ban taɓa jin daɗi abunda ka min irin na yau ,na gode Naufal"

"Dady dan allah ka daina gode min"

"Dole ne,amma Naufal karka yarda ka ƙara min alƙawarin da ka ɗauka,karka wulaƙanta

Sabreen ,wllh Allah idan makamancin hakan ta faru zan iya fushi da kai ,zan iya rabu da kai,daga ranar ma karka ƙara kira na da sunan Dadyn ka"

Wasu zafaffan hawaye suka fito mishi zuciyar tana radaɗi da zafi,yau shi mahaifinshi ke gayama irin wanan maganganun masu zafi gaske "Dady ba zan ƙara alƙawari"

"Na sani Naufal kai jini na ne,ina ƙara ma ƙarfi ne yadda zaka riƙe da muhammanci,Sabreen tana sonka ita ta fara magana,na san kai ma kana son ta"

A razane ya ɗago yana kallon dadyn maganar da yayi tana mishi yawo a cikin kaI"Sabreen tana sonka ita ta ce tana sonka" kai anya ina wa...

"Naufal bamu ga ta zama ba,tashi mu fita gobe ne fah

Gaban shi ya faɗi" gobe gobe!!

"Ba'ayi biki haka ba,bakin ƴaƴan gata ka tashi mu fita,baka da wani abu da kake son ayi"

ƙasa yayi da kai,dan  kanshi yayi nauyi.

"Naufal ko auran dole ne"

"uhm ina tunanin abinda za'ayi ne"

"to mu fita"

dadyn ya fara fita yabar nan,da ƙyar ya iya jan jikin shi,ba abinda yake tsorata shi irin da yaji Dady ya ce wai sabreen ta ce tana sonshi,tabbas yakan sabreen bata son shi,ko kaɗan" to meyasa zata min haka? dan tsana"

ya tambayi kanshi ya kuma bawa kanshi amsa"meyasa Why?Sabreen ke wacce iri ce kin dagula min rayuwata,da kika haɗa rayuwar mu tare,bana sonki bana ra'ayinki amma saida kika cusa kanki a rayuwata meyasa baki gane bana sonki ba, am helpines,ba zan iya komai ba Sabreen kin cuci ni kin....

"Naufal kayi sauri ina jiranka, dady ya katse mishi tunanin daya ke yi"

~~~~~~~~~~~~~

Su Sabreen manya ana chan ana gyaran jiki ita da farrah harda Momy ma, tasha lalle wanda ya fito da yar madaidaiciyar hasken jikinta,yaƙe kawai take yi amma  bata jin daɗi a zuciyarta.

"Toh yanzu taya zan haɗu da malama,ko na bari bayan an ɗaura aure"
~~~~~~~~~~~~~

"Keeee tunanin me kike yi Aunty Amarya"

Ɓata rai Sabreen tayi"Farrah ki daina ce min aunty bana so"

"To matar yaya"

harara da gallama ta "waye matar yaya?

Dariya Farrah tayi "Kai Sabreen lamarin ki sai ke,ranar da kuka ,kina son yaya ya ɗaura muku aure amma yau wa waye matar yaya kike tambaya"

"ina son Yaya  allah ya kyauta me xanyi da ɗan kilibibin nan"A zuciyarta tayi wanan maganar ,A fili kuwa harar ta tayi.

Momy bata gurin su kaɗai ne,ita ta koma gida dan tayi wasu aikin.

Sun daɗe har bayan maqrib suna nan ana abu ɗaya.

~~~~~~~~~~~~

Bayan su dadyn sun dawo ya tambayi momy ina su Sabreen ta gayamishi suna gurin gyaran jiki,Ɗadyn ya ce Naufal ya je ya ɗauko su.

\***********

Wayar Farrah ya ya kira"Hello Ki fito ina waje" Ya katse wayar

Kallon Sabreen farrah tayi"Angon ya ƙaraso"

"Mitsewww!

"Ni tashi mu je yana jira idan mun je kin mishi tsakin"

Suna fitowa daga shagon motor shi,gaban Sabreen ya faɗi amma ta ɓata rai.

Daman ya lafiyar giwa balle tayi hauka,wanda ko farinciki yake ya ga damar ya ɓata rai balle kuma.

Bai ɗago kai ya kalle su ba,har suka shiga cikin motar,harar shi sabreen ke yi  ta gefan ido a ranta tana faɗin"Ban kaddara da me zai haɗa ni da kai,kuma burina yana cika na son ɓatawa Haulat rai zan rabu da kai ne,dan ba zan iya rayuwa da kai ba"
~~~~~~~~~~~~

kiran wayar farrah ne ya katse musu shirun da suke yi,ƙawarta ce,ita kuwa farrah ko a jikinta ta saki jiko suna fira akan bikin ma,hayaniyar ta fara damun shi

ya daka mata tsawa"Keee baki da hankali ne"

Bata san lokacin da wayar ta faɗi a hannun ta ba,jikin ta ya fara rawa,Ita kuwa Savreen ko a kafaɗar ƙafarta.

A haka suka isa Gidan su ya fara sauke ta,sanan ya zo gidan na su.

Hankali kwance tayi wa Farrah Sallama harda faɗin "Sai goben kenan,ki fito da wuri"

A tsora ce farrah ta ce" toh"

Ba wanda ya kalli juna a cikin su.

~~~~~~~~~~

Ta isa falon ta hango hajia zaune akan kujera.

"Hajiyata ya baki tasu kin min oyoyo ba"

Ganin hajia wani iri yasa ta ce"Hajia lafiya?

Saida ta ƙaraso gurinta ta rungumeta"yanzu shikenan xaki barni ni kaɗai"

"Waya gayamiki ba inda zani ina nan"

"Zaki barni mana,zaki koma gidan Naufal"

Gabanta yai mummanan faɗuwa"zan koma gidan Naufal"

"Eh tare zaku dunga yin komai"

Ai sai hawaye ta ƙara rungume hajia,tana kuka ita ma hajiar kuka take yi,basu iya lallashin junan su ba,saidai gajiya suka yi da kukan,a ɗakin Hajia ta kwana.

~~~~~~~~~~~~~

Naufal ƙasa barci yayi abin duniya ya dame shi.

"Meyasa Sabreen zata min haka?
"Yanzu ya zanyi da Haulat na mata alkawarin aure?
Ba zanyi iya rayuwa da Savreen a matsayin matar aure na ba?

"Haulat nake so, ita ce zaɓina ita ce ra'ayina"

Tsanar Sabreen tana ƙara yawa a ranshi,amma na banza tunda ba abinda zai iya"Ban taɓa ganin irin wanan rayuwar ba"

"Sabreen sai kin gayamin dalilinki na ɓata rayuwa"

Ƙasa barci yayi duk tsawon daran ganin abu yana son mishi yawa yasa ya tashi ya ɗauro alwala ya fara sallar ko ya samu sassauci,ya kowa samu raka'a shidda yayi barci yai awan gaba da shi.

~~~~~~~~~

Tun a masallaci suka fita shi da Dady.

Yau Juma'a
Yau ne ya kama bikin Sabreen muh'ad mai taƙama tare da Angonta Naufal mai taƙama.

Gaba ɗaya Abuja da kewayan ta sunyi labarin wanan bikin kuma suɓ hallara,ƴaƴan government tana manyan yan kasuwa da na ma'aikata duk sun hallara,dubbanin mutane ne suka hallara gurin ɗauren Auran.

Chan na hango Naufal cikin Shadda purple harda malum-malum kayan sun mishi kyau matuƙa,amma kallo ɗaya zaka ma fuskarshi ya gane yana cikin wani yanayi wanda ba wanda zai iya tantance wa,amma yanayin yafi kama da damuwa,kusa da shi Dady kalar kayan su iri daya komai da komai,kai ka ce Dady ne Angon dan yadda yake washe baki yana farinciki.
Ƙarfe biyu za'a ɗaura Auren wanda yanzu saura minti ashirin da takwas a ɗaura auren.

~~~~~~~~~~~~

Da gudu ta faɗo ɗakin a ruɗe tana haki tana nishi "Haulat Haulat!!

Haulat wacce ke kwance tana mulka barcin ba abinda ke damunta.

Ganin ba zata tashi ba yasa ta ɗaka mata doka a baya "Haulat ke tashi banza kina nan kina barci baki san abinda ke faruwa ba"

"Ke dallah kinsan bana son ina barci a tashe"

"Au haka zaki ce ko"

"To me ya fara?

"ina ce Naufal ɗan Alhaji mai taƙama ne saurayinki?

Yamutsa fuska tayi"Eh shi ne lafiya dai

"Hmm ina lafiya to wllh yau za'a ɗaura mishi aure yanzu haka an hallara gurin ɗauren Auran..

Tsaki Haulat taja"Ke  ni bana son irin wanan abun kawai zaki so ki ɗaga min hankali"

"Haulat kenan kina ganin wasa ne to shikenan ba zan matsa miki akan sai kin yarda da ni ba,amma nasan gaskiya zata baiyana,tana faɗa ta fita daga ɗakin.

Ita kuwa Haulat ƙara komawa barcin ta tayi,ko a jikinta.

Ƙarfe biyu daidai aka ɗaura auran Naufal da sabreen fiye da mutane dari sun shaida ɗaurin auren.

Tunda aka ɗaura auran jikin Naufal yayi sanyi zuciyar shi sai faman bugawa take yi,kamar wanda ya tashi daga dogon jinya haka ya ke ji.

~~~~~~~~~~~

Zaune take akan gadonta tasha kyau har ta gaji,ita kanta jikinta yayi sanyi"hmm ko bakomai yanzu na ɗauka fansa akan ki Malama Haulat tunda na aure wanda kika fi so a duniya kina ji kina gani ba abinda kika iya akai,Naufal ni ba  tsarar auranka ba ce kamar yadda nasan kai ni ba ra'ayinka ba ce,dan haka bazan zauna da kai ba,nan da ƴan wasu lukuta kaɗan zan rabu da kai"

"Aunty Sabreen tunanin me kike yi"Farrah ta faɗa ta ƙarfi haɗe da jijjiga Sabreen ɗin.

"To meye na tunani bayan an ɗaura auran Naufal ya zama naki ke kaɗai,ko tunanin rabuwa da hajia ne"

Harara ta mata"Ke baki jin magana ko nace karki kira ni da Aunty ki"

Dariya farrah tayi sosai ta ce"Maida wuƙar ƴan mata"

~~~~~~~~~~~~~

Ba su suka samu damar zuwa gida ba sai ƙarfe biyar da wani abu,suka shigo gidan lokacin ba mutane sosai a gidan,kowannen su ya nufi ɗakin shi.

Yana zuwa ya faɗa kan gado,haɗe da sauke nannauyar ajiyar zuciya,ya daɗe a haka yana tunani Tunanin Haulat kawai yake yi ita yake so ita ce ra'ayin shi ita yake da burin ya aura"bazan karaya ba Haulat ina sonki zan kuma aureki dan ke ce muradin raina" ya fili ya faɗa.

Ringin ɗin wayar Dady ne ya shigo wayar,yana ji ya ɗauka

"Naufal karka Zauna  fa akwai dinner da za'ayi karfe  shidda kayi sauri ka shirya sun gama shiri kai kawai suke jira gidan hajia zaka ku tafi tare da Sabreen ɗin" yana gama faɗa ya kashe wayar shi.

"Why Sabreen? i cant i cant,ba zan iya rayuwa da ke ba Sabreen" idanowan shi  sukai jajir.

Da gyar ya iya sarrafa jikin shi yayi wanka ya fito,kallon kayan drower ya tsaya yi ,ya rasa wanda zai saka,wata baƙar suit ya ɗago mai haɗe da ash colour ya saka sun mishi kyau ainun,kallon kanshi a madubi yayi.

"Wai ni aka ɗaura wa aure da Sabreen yanzu ni mijinta ne?

ya nuna kanshi"Ni Naifal nine mijin Sabreen"

Ƙasa yayi da kanshi yana sauraran bugun zuciyarshi wanda take buguwa da ƙarfin gaske.

Turaran da ya shafa sunfi kala goma ta ko wacce gaɓa ya shafa mata turaran da ake shafawa.

Bayan ya gama shiryawa ya fito cikin ƙasaita da izza   yana tafiya kanshi aƙasa,baiyi mamaki ba ganin ba kowa a falon,yana fita yaga motoc irin na alfarma gudu shidda kalar su ɗaya ash colour irin kayan shi,sun ganin fitowar shi daga gidan suka fito,suka buɗe mishi kofa ya shiga cikin isa da mulki.

~~~~~~~~~~~~~

"Sabreen ki saka wanan kalar tafi kyau"

"Ke ni bana son shi,wan xan saka,ta nuna wata dugowar riga baƙi da ash kala,rigar ta haɗu iya haɗu

"To bana matsa miki ba Amarya"

Tana saka kayan aka fara mata makeup waw masha allah ashe haka Sabreen ke da kyau ,tayi kyau har ta gai.

Ba'afi minti goma da gama makeup ɗin ba aka aiko Naufal ya iso su fito,taɓe baki Sabreen tayi.

Rigar dugowace sosai tana tafiya tana binta Farrah da hajia su suka riƙo ta har wajen gurin motorcin,motor da yake aka buɗe mata ta shiga,tana shiga wani irin sinadarin ƙamshi ya doki hancinta har saida ta lumshe ido.
~~~~~~~~~~~~~

Kusa da juna sosai suka zauna hakan ya ƙara haifar musu da matsanaicin bugun zuciya,kowanne yana jin fitar numfashin kowa

"Bata sonka ko kaɗan"

"Na sani kuma kema kin san bana sonki"
"But why Sabreen?

Bata kalle shi ba,daman ko ɗazun bata kalle shi ba"Saboda ɗaukar fansa"

wanan karon saida ya kalleta ,zuciyarshi ta buga dan ta bashi tsoro ganin irin kyaun da tayi gashi kalar kayanshi ta saka,cikin wata siga wacce shi kanshi bai san lokacin da ya tsinci kanshi da shiga yanayin tausasawar ba ya ce"Sabreen!

Lumshe idanowa tayi tana jin dadin yadda yake kiran sunanta a tata cewar da indiyanci yake kiran sunanta.

Shi kanshi saida yai jimm,bai san abinda ya yasa shi yin hakan ba,ganin bashi da niyyar magana ya ce tace mishi"Nima ba zan zauna da kai ba,zamu rabu ne,dan wata manufa na aureka,karka ji wani avu nasan baka so na ka kwantar da hankalinka zamu rabu"

Da mamaki yake kallonta kanshi ya ɗaure hali irin na Sabreen yana bashi mamaki yadda take mishi magana ma abin mmk ne har ya buɗe baki zai mata magana motor ta tsaya tana tsayawa aka buɗe musu kofa.

Yana sauko da kai idanowan shi sukai arba da ƙaton hutun su wanda suka yi matuƙar kyau mamaki ya ƙara kamashi ganin yadda Sabreen tayi murmushi a hoton kamar wacce take son shi,ga hoton yayi kyau kamar ba haɗa shi aka yiba,a tare aka yi shi.

Tana fitowa taga ƴan jarida da masu ɗaukar photo  a ranta ta ce" Za'ayi vedio kuma za'a nuna a tibi,wanan dama ce"

Daman yana tsaye yana jiran fitowar ta,murmushi ta fara mai ƙyayatarwa tana kallon masu ɗaukar hoton su kuma sai ɗauka suke yi.

ji yayi ta riƙe mishi hannu da sauri ya juyo ya kalleta cikin mamaki,wani irin murmushi ta mishi mai ɗaukar hankali bai san lokacin daya maida mata da martani ba,a daidai lokacin wani mai hoto ya ɗauke su,suna kallon juna suna murmushi gashi hannuwan su a riƙe da juna.

~~~~~~~~~~~~~~
Waw guri ya haɗu ya haɗe abin kamar ba'a 9j ba ,waiyo ni batula abun mamaki daga gefen hannun daman Sabreen sai ga shadow da my Aunty nabeela,waiwai su khadija da fatima shariff
~~~~~~~~~~~~~~

suma suna gefe mr parrot da hauwa sule bakin su yaƙi rufuwa ,hauwa'u da ramb kuwa suna gefe sai satar kallon Naufal suke yi,my sis khadija da nafisa kuwa suna kusa da farrah sai fira suke yi,Dr halimatu ma ta faso ita da jermielat , wai su hafsat da safiya abudullahi kuwa hankalinsu yayi gurin kaji, Aysha zango ita da mrs sunusi sai kwaso shoki shoki suke yi,ita kuwa sarauniya jidda ta saki baki tana kallon yadda Naufal ke yamutsa fuska.

Ina zan manta da ku yanzu dai na hango ku,cunkuso ne ya rufe ku iyalan jamliya,dan tsabar ɗauki tun ranar da Sabreen tace Naufal zata aura suka hallaro😅,daga chan gefe gudu kuma jamar batula fans novels ne suka baiyana suma ba'a barsu a baya ba,chan kuma sai ga iyalan bintu Ahmad wato ƴan gidan Shabihaty suma sun ɗan yi kara,iyalan lipton ma na hango wasu ƴan ƙaɗan,tawagar farida kuwa tun kafin a buɗe gurin suka iso,ƴan tangantakar mu,kuma na hango ku,amma ku da alama ƴan team ɗin Haulat ne,tawagar waye sila,kuma sannunku da ƙokari,wai ai idan ba'a ganku ba wa za'a gani😅iyalan tawan,ku da tun kafin a ɗaura aure kuka iso,chan taro ya fara nisa sai ga wasu gungumin al-umma,masu yawan gaske gashi ban gane su ba,gaba ɗayan jama'ar gurin kallon su ake yi ,kasa hakuri Sabreen tayi,ta tambaye su daga ina,

"Mu masoyanki ne masu miki fatan alkairi,muna da nisa amma haka muka ɗugunzumo mu tayaki murna,kuma ki miƙa mana gaisuwa gurin batula"

Suka gayamata haka sanan suka zamu guri suka zauna.

Taro yayi taro al'umma sun hallara taya Sabreen da Naufal murna,chan na hango wasu manyan mutane,tun isowar su aka fara buɗa musu hanya,Abin mamaki Sai na ga Aunty Nabeela ta tashi da murnar ta,guri na ta iso tana murmushi ta kalle ni ta ce"My batul zo muje ki ga waɗan da suka zo"

Kallonta nayi nai murmushi na ce"Toh muje my Aunty"

waiyo allah na wa zanga ni Sarah ce da alfaga da kuma mutumina Sul harda Ruƙaiya,nayi mamaki sosai ganin su gurin Bikin Sabreen.

Hhhh baku ga da Sarah da zauna kusa da Sabreen ba,kunga Sabreen kuwa sai tai wani irin mugun muni,to kyau na gaskiya ya baiyana a gabanta.

"Toh wai ko yarima mu'utasim ya zo kuwa?

hhhh to ya zan sani tunda ba ganinshi zanyi ba.

Ina cikin wanan tunanin Aunty nabeela ta ce min"My batul yarima mu'utasim yana gaisuwa"

A ruɗe na ce"My Aunty ya zo ne"

"Eh kin shiga ruɗani ne"

Wanan shine *Ruɗani* ,littafin  Sarauniya beelat(My Aunty nabeela).

biki yayi biki Tunda manyan mutane suka hallara bikin harda su Yarima mu'utasim,na so ganin baba me gadi dan yaban dariya.

.

[12/16, 5:41 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт Bу Gяσυρ O F Hуρє Hαυѕα Nσνєℓѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚

[12/22, 5:26 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*

*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

Page 11

............................................................

_*Manzon Allaah(ﷺ)* *ya ce;{WANDA YA RUFE WA MUMINI WANI SIRRI(NA LAIFI) KAMAR YAYI CETO NE GA WANDA AKA BINNE DA RAI!.}*_

```[Sahihut Targib;2337]```

~~

_Duk wanda ya rufa ma mumini sirrinsa na laifi, bai ba mutane labarin abinda ya sani game da shi na sharri ba, to kamar an binne shi da rai ne sai ya ceceshi. Allaahu a'alam._

```Allah ta'ala yasa mudace```

_*سبحانك اللهم وبحمدك, أشهد أن لا إله إلا أنت، أستغفرك وأتوب إليك.*_

.................................................................................

Ansha shagalin baki abun ba'a cewa komai, sai wanda ya gani kawai.

Kallon ta kawai Naufal yake yi yana mamaki gashi sai washe baki take yi ,maganar da ta gayamishi yake tunowa"Bana sonka ba zan iya rayuwa da kai ba,na aure ka ne dan ɗaukar fansa"

A haka taro ya watse hankalin shi baya tare da shi abubuwa sai yawo suke mishi kwakwalwa ,daga sun haɗa ido ya su harara juna suja tsaki.

Karfe Tara taro ya watse,kowa ya kama gaban shi,su kum suka ɗau hanyar zuwa gidan su hajia.

Kallonta yayi rai a ɓace ya ce"Sabreen  meyasa kika min haka kin san bana sonki kika ce zaki aure ni"

Ɗagowa tayi ita ma ranta a ɓace ta kalle "Hmm to kai me kake tunani ,ni Sabreen zan iya auran haka kawai allah ya kyautamin da auran....

yaji zafin maganar matuƙa ya janyo ta jikin shi da karfi ya rungumeta ɓacin ran da yake  ciki bai bar shi ya saurara feelings ɗin da yaji ba "Ke ni tsaranki ne zaki gayamin irin wanan maganar,ni wllh ko banga dalilin da zai sa na aureki ba,dan banga abinda zanyi da ke ba,ko a jerin mata ban saka ki ba,balle ki xama class ɗina,ke kanki kinsan ke ba aji na ba ce,banda kaddara da wallahi ko kallan ki bazan yi ba"

Ran Sabreen kai ƙololuwa gurin ɓaci idanuwanta sunyi jajir dan takaici gashi ya matseta,cizo ta ganna mishi a hannu da ƙarfin gaske da sauri ya sake ta.

Har yakai hannu zai janyota farrah ta buɗe kofar

"Am. .. sorry"

Har zata maida kofar ta rufe Sabreen ta fito rai a ɓace,gaba tayi ta barshi a ciki.

Wani ƙululon takaici ya kama shi,idan har haka sabreen zata tunga mishi bai jin zai iya riƙe alƙawarin Dady,ya daɗe a cikin motor kafin ya fito.

Yana isa falon gaban shi yai mummunan faɗuwa   ganin kowa da kowa yana falon,har ya samu wani guri gefe zai zauna Dady ya ce mishi"Naufal matso nan kusa da matarka."

Ba Naufal ba ita kan Sabreen zaida taji haushi.
Ba musu ya matsu kusa da ita ya ɗuka dan a kasa suke harda ita ɗin.

Dady yayi gyaran murya ya ce"Naufal mun gama magana da kai,ni yanzu ba abinda zan ce maka,illa na ƙara tunatar da kai haƙƙin aure wanda su ma kasan su."

Juyowa da kallon shi yayi gurin Sabreen ya kalleta duk da ƙarancin hasken da ke ɗakin amma yana hango fuskarta "Sabreen yanzu zaki shiga wata sabuwar rayuwa wacce baki saba yin irinta ba,abinda nake so da ke sabreen kinga Naufal ɗan uwanki ne,ki riƙe shi, ki mishi biyayya ki bi umarni shi wannan ce shine haƙƙin mata akan mijinta,nasan kina da hakuri amma sai kin ƙara,Sabreen ku riƙe junanku da amana,sanan duk abinda ya miki ki same ni ki faɗimin kina jina?

Ɗaga mishi kai tayi alamar taji.

Kallon hajia da Momy yayi ya ce"Toh baku da abin faɗi ne?

A hankali momy ta buɗe baki saida ta fara gabatar da addu'ar buɗe taro sanan ta ce"Naufal ba wata magana mai tsawo zanyi ba,kasan Sabreen marainiyace karka cutar da ita ka riƙe ta ƴar uwarka ce ,sanan wanan auren shi ne alkairi a gare mu da kai ma,bansan ko zaka fahimce abinda nake nufi ba,sabreena alkairi ce a gareka dan haka ka Naufal ka kula da Sabreen"

Tunda suka fara magana gaban shi ke faɗuwa,ya rasa wani irin tunani zai yi ma.

Hajiya kuwa kasa magana tayi sai kuka sabreen najin hajia ta fara kuka ita ma,ta fara yi,kusa da ita hajia ta zo ta rungumeta suna ta kuka ba wanda ya dakatar da su.

Naufal ma ji yake yi ina ma zai iya yin kukan da yayi ,dan shi ne abin kuka ba su ba.

Ganin basu da niyyar daina kukan Dady ya ce"Ya isa haka kuyi hakuri dole daman sai wanan ranar ta zo."

Kallon Naufal  yayi ya ce"Naufal tashi ku tafi"

Gaban shi ya faɗi"Na tashi mu tafi"ya maimaita abinda Dadyn ya faɗa a hankali,shi kanshi zaida yaji wani iri wai yau zai bar gidan su ya kwana a wani gida daban.

Sabreen tana jin abinda Dady ya faɗa ta ƙara ƙanƙame hajia tana kuka mai tsuma zuciya.

Tashi momy tayi taje da riƙo  Sabreen tana san ta rabata da jikin hajia.

"Waiyo hajia Momy dan Allah ,Hajia bazan tafi na barki ba,waiyo hajia ki riƙe ni,momy momy kiyi hakuri na fasa auran bana so Allah na fasa bana son ya naufal,hajiyata bazan tafi ba...

Duk da yanayin da suke ciki saida suka yi ƴar dariya,musamman Naufal da farrah A ran shi ya ce"Banza daman haka kike amma kika ce  kina son aure n..

"Naufal zo ka jata"
Dady ya katse mishi tunani.
Hajiya ya fara ja dan baya son ya taɓa Sabreen.
"kai ita zaka ja", Dadyn ya taɗa.

Hannun shi yakai kan kafaɗar ta,ya fara janta ,ita kuma momy taja hajia.

"Yawwa  kamata ku fita",cewar dadyn

Kuka Sabreen take yi tana ihu "Waiiyoo!  wllh Dady na fasa bana so,dan allah ku barni,na zauna da hajia bana son auren,Yaya Naufal dan allah ka barni bana so waiyooo"

Dariya ta bashi sosai har ya kasa ɗaurewa zaida yayi,ita ma farrah dariya tai tayi.

"Karka sake ta Naufal."

"To Dady."

Har suka fito daga fallon tana kuka,gurin shiga motor ma,saida momy ta turata da ƙarfi tana shiga aka kulle kofar,hajia bata fito ba tana chan tana rusa kuka an rabata da ƴar aljanna.

shiga motor yayi direba yaja suka fita daga gidan,Su momy suna nan tsaye har motor ta fita,sanan suka dawo suyi ma hajia sallama su koma gidan su.

Dariya Naufal ya fara yi sosai da sosai wanda bai taɓa yin irinta ba.

Ƙara fashewa da kuka tayi mai sautin gaske.

"ke dare ne ki mana shiru baki son rabuwa da ita kika ce kina son aure."

ys ƙara fashewa da dariyar shi.

Kuka Sabreen ke yi sosai bata kuma kula shi ba har suka isa unguwarsu,wani katafaran gida ne,wanan kallo ɗaya zaka mishi kasan ankace dala,dan ya fituno da kyau abin zai wanda ya gani.

Suna isa harabar gidan direban ya tsaida motor,shi ya fara fitowa"Idan kin ga dama ki sauko idan baki ga dama ba ya maida ke gidan hajia."

Yana faɗa ya shige abinshi yana tafiyar kasaita da izza.

Kamar ta ce direban ya maida ta gurin hajia sai kuma ta fasa ,ta sauko ta bi bayan shi a falon ta isko shi,tana kuka ta karasa gurin shi ta ce"Idan na koma zance kaika kuro ni,ka ce na dawo."

A fusace ya miƙe har zaiyi wata magana ya fasa tuno halin Sabreen ba abinda ba zata iya ba,wani mugun kallo ya mata sanan ya juya ya haye sama.

Har lokacin bata daina kuka ba,kallon falon tayi ya mata kyau sosai,kan gujera ta hau,tana ta kuka har barci ya ɗauke ta.

Daman yasan gidan ya kuma zaɓa ɗakin shi,yana zuwa ya shige saida yayi wanka yayi sallah sanan ya kwanta,ya daɗe yana tunanin irin zaman da zasu yi da sabreen sanan shi ma barci ya ɗauke shi.

~~~~~~~~~~~~~

"mtseww!

"Wai ke wa kike ma wanan tsakin tun ɗazun."

Wani mugun kallo tayi mata sanan ta ce"Ban sani ba".

taɓe baki tayi ta cigaba da yin abinda take yi.

Kallon wayarta tayi ta ce"Naufal meke faruwa ne?

ƙanwarta wacce suke zaune a ɗakin ta kalleta a ƙaro na biyu ta ƙara cewa"Ai daman na sani"

"Kin san me,banson iskancin banza."

Tana rufe baki saƙo ta whatssap ya shigo wayarta,kamar ba zata duba ba,dan baƙowar number ce.

Sai ta duba, a tsorace ta miƙe tsaye haɗe da zaro idanowa,xuciyarta ta fara bugawa da ƙarfin gaske"Wa.i..y.."
Numfashin ta ya fara sarƙewa dushu-dushe ta fara gani.

"Aunty haulat lafiya mai ke faruwa? a ruɗe take tambayarta,ko kafin ta ƙarasa  gurinta ta faɗi kasa zummama.

"Innalilahi! momy momy Aunty haulat mun shiga ukku.

~~~~~~~~~~~~~

kiran sallar farko a kunnan Sabreen a ruɗe ta fara tambayar kanta "Nayi Sallah jiya?
"Innalilahi ta faɗa da sauri ta miƙe tuno bata yiba,saman ta hau a ruɗe ,kasancewar bata san wani ɗaki ba ne tashi ta faɗa dakin shi,bata ma lura da yana kwance akan gadon ba tayi toilet da Sauri.

Jin ƙarar ruwa ya farkar da shi,kunna guluf mai hasken yayi,"waye a baya" ya faɗa a hankali saukowa yayi,sautin tafiya taji a tsorace ta ce"Waiyo Allah na waye"

"Ke meye ya kawoko ɗaki na?

"Bansan ɗakin ka ba ne"

"Bakin san ɗaki na ba ne".

"eh!

"To fito nima zan shiga ne".

"Waiyo karka shiga ya hakuri dan allah dan allah".

Dariya ta bashi a ranshi ya ce "Kamar wata wacce zan ga wani abu ƙwaila da ita"

Murmushi ya fara yi tuno hali irin na ta,mawuyacin abu ne ta ba mutum hakuri,amma yanzu harda wani haɗa shi da allah.

"To na baki minti biyar kafin na dawo ki fito"

Yana faɗa ya juya yana murmushi.

Tana jin ya fita ta fito da sauri,ta faɗa ɗayan dakin wanda ba tazara a tsakanin su da juna,tana shiga ɗakin ta kulle,kallon ɗakin ta tsaya yi,ganin zai shagaltar da ita yasa ta maida hankalinta akan abinda zata yi.

Yana dawowa yaga bata nan daman yasan ba ganinta zaiyi ba,shiga toilet ɗin yayi ,saida yayi wankar tsarki sanan ya fito ya gabatar da ibada.

Zaune yake kan sallayar yana hailala da tasbihi wa ubangijinki,tunanin Haulat ya shigo ranshi zumbur ya miƙe ya fara naiman layinta...

Ringin wayar tayi har ta katse ba'a ɗauka ba,tsoro ya kama shi,tunda yake da Haulat bata taɓa ƙin ɗaukar wayar shi,cikin hanzari da zaƙuwa ya ƙara kira,nan ma shiru ba'a ɗauka ba,saida yai kira biyar abinda bai taɓa yiba ,amma shiru ba'a ɗau wayar ba,jefar da wayar yayi akan gado ransh a ɓace,haɗe da hura hanci.

"Haulat Allah yasa kina lafiya?
"Taya zata kasance cikin lafiya bayan abinda ka mata."

Da kanshi yayi tambayar kuma ya ya ba kanshi amsar da ta ƙara ruɗa shi,yasan bai kyauta ma Haulat ba,ya kamata ya sanar da ita koma meye,yanzu idan taji a bakin wani fah.

Tashi yayi ya fara safa da marwa a tsakiyar ɗakin,lissafin shi duk ya dagule,kanshi yayi zafi tunanin halin da masoyiyar shi take ciki yake yi,wanda ya ɗaura laifin akan Sabreen ko kaɗan baya jin zai iya raga mata kan abinda da mishi,zumbur! kamar wanda aka tsungula ya fito da sauri,bibbiyu yake taka matalakar dan sauri,har ya iso cikin falon bai kula da mutanan dake ciki ba,ya fara ƙokarin fita.

"Ango Naufal ina kuma zaka je ka bar amarya ita kaɗai."

Tsayawa chikk yayi sakamakon jin muryar ko ta wacece,a hankali ya juyo dan ƙara tabbatarwa zaro ido yayi ganin ba ita kaɗai ba..

"Naufal saurin me kake yi,baka kula da mu ba."

Momyn shi ta katse mishi tunanin shi,kallon su yayi,Hajiaya ce ita da Momy da farrah sai Sabreen ɗin wacce ke manne a jikin Hajia, "Meye kuma ya kawo su da safe haka? taya zasu zo mana gida a irin wanan lokacin jiya ne fah muka tare", a ranshi yake wanan tambayar,"To meye wani abun zamu yi waɗan da ba son juna muke yiba",duk a zuciyar shi yake wanan tunanin,bai san lokacin da ya ƙaraso tsakiyar falon ba,sai jin shi yayi zaune a ƙasa,cikin harɗaɗiyar murya haɗe ta aro murmushi ya yafawa fuskar shi ya ce"Ina Kwana momy."

Bai tsaya jiran amsarta ba ya juyo da kallon shi  ga  hajia ya ce"Ina kwana Hajia ya gajiya."

yana kai aya hajia ta ɗauka"Lafiya lau Naufal ka barni da kewa shi ne ko tambayata baka yiba,au naga kamar ba baka so ganin mu yanzu ba."

Kallonta yayi ,yana tuhumar kanshi akan maganar da ta gayamishi ,a fili ya ce haɗe da ɗan guntun murmushi, "Ba haka bane hajia,ya kewa?

"Ba sauƙi jiya ban iya barci ba ,da zan iya da nayi kishi da kai"

Gaba ɗayan su sukai dariya banda Sabreen wacce ta murtike fuska.

"yi hakuri Naufal munzo kawo abinci ne da farrah zata kawo to sai hajia ta ce tana son zuwa."

Murmushi yayi ya ce"Ba komai Momy."

"Amma ina kake ƙokarin zuwa?

"Am..amm..da. amman daman zanje gurin hajia ne na samo mata abinci bata ci komai ba."

ya faɗa yana kallon Sabreen ɗin yana mata guntun murmushi.

Charab hajiar ta ce"Hm to na hutar da kai,amma naji daɗi da kake nuna kulawarka akan Sabreen na gode Naufal Allah ya biyaka da aljannar shi."

"Ba komai Hajia ko kin manta Sabrewn ƴar uwata ce,zan iya yin komai  a matsayinta na ƴar uwata,sanan kuma matata! daidai gurin yji zuciyar shi ta buga ƙara maimaita kalmar yayi "Matata!

Wani irin kallo Sabreen ta mishi na mamaki,shi ma ɗago kai yayi suka haɗe ido mugun kallo suka yiwa junan,amma sai suka yi murmushi.

Wani irin daɗi ya mamaye Momy wanda ta kasa ɓoyewa sai yaƙar baki take yi,kamar Ango.

Ita kanta farrah dake gefe murmushi take yi,dan jin daɗin yadda naufal ya aminta da ita cikin ƙanƙanin lokaci haka.

Wai kuma kunsan farinciki gurin hajia ba sai ance komai ba.

Sun ɗan taɓa fira kaɗan,sanan momy ta kalli hajia ta ce"Hajia to mu tafi ko,yadda zasu sake su iya cin abincin da kyau."

Kallon momy yayi a ranshi ya ce"Hm wai mu sake kamar wasu masu cin amarshi."

Sabreen naji abinda momy ta ce,idanowan ta sukai jajir kwalla ta shika su famm,cikin murmuyar kuka ta ce"Hajia yanzu tafiya zaki yi."

Momy ta ce"Kinga idan kuka zaki dunga yi,xata daina zuwa,muma zamu daina zuwa,kina son gobe ta zo?

ɗaga mata kai tayi alamar eh.

"Toh idan kina so ta zo gobe,kiyi shiru."

"Tohhh! kawai ta faɗa.

Kallonta hajia tayi ita ma hawayen ne a idonta ta ce"Kiyi shiru kinji ga mijinki nan zai tayaki zama,kuma baga waya ba,sai ki kira ni mu gaisa."

"Ba zaki xo gobe ba."

"zan zo."

A tare suka fita fita har harabar gidan,suna kallo suka shiga motor,Sabreen sai hawaye shaaa kamar famfo,ko kallon inda take baiyiba ya juyo ɗakin,yana zuwa ya janyo kulolin abinci ya fara ɓuɗewa,kunon gyaɗa ne sha madara sai waina da miyar ita kanta wainar sai tashin ƙamshi take yi,miyar ma haka ga nama zaƙo-xaƙo,sai dangalin turawa soyayye da dafaffe wanda ya haɗe da hanta, sai kuma farfeson kaza,da soyayyan gwai harda lipton,kallon abincin yake yi yana yamutsa fuska kamar wanda yai arba da ɗanyan kashi.

Kunon gyaɗan da waina ya xuba ya fara ciki,yana cikin ci Sabreen ta shigo,kallon shi ta tsaya yi.

"Waya ce ka cimin abinci ai ba kai aka kawo mawa ba."

Bai ɗago ba balle ya  tanka ta,saida ya gama ci ,tana kallon shi yana hura hanci kamar warin abincin yake ji.

Yana gamawa ya tashi saida ya fara goge hannunshi da hankey sanan ya tashi har lokacin bai kalla inda take ba.

"Ina zaka?

A fusace ya juyo gabanta ya ƙaraso dabb da ita har suna jin fitar numfashin juna,kallon ta yayi ido cikin ido ya"Momy ko Dady,kuyi hakuri dan allah zani gurin wacce nake so ne."

"Toh ban aminci ba."

Dariya ya fashe da ita sosai yana mamaki hali irin na Sabreen,a lokaci ɗaya kuma ya murtike fuska kamar ba taɓa dariya ba,rikiɗewa yayi ya dawo ainihin Naufal mara dariya ɗan gilibibi da iyayi da yatsine isa izza mulki.

kallon ta yayi ya ce"me zan miki idan na tsaya?

"Ai.. dan...

"Hm Sabreen dan kin aure ni,da ƙarfi ba ki da ikon juyani,kin gane yana maganar yana ƙarya harshe cikin iyayi.

Kallon ƙaramin bakin shi Sabreen ke yi,yadda yake fito da maganar take kallo.

Ƙara matsuwa yayi dabb ta ita ƙokarin haɗe bakin su ya fara yi,tureshi Sabreen ta fara ƙokarin yi,amma ina ta kasa.

"Yadai ba abinda kike so ba kenan."

"Allah ya kyauta ni ba ƴar iska ba ce."

"Ni kuma ɗan iskane,u know what Sabreen?i cant share anything  with you,"

"Ni bana jin yaren india."

Haba me Naufal zaiyi dariya ya fashe da ita harda komawa baya ya zauna kan gujera.

Ta ƙule gurin takaici  hararshi take yi ,shi baima san tana yiba,saida yayi me isarshi sanan ya

tsaya ,ɗaure fuska yayi ya ce"u are very funny Sabreen."

Ko kaɗan Sabreen bata gane abinda yake faɗa,ko hausar ma ba ko wani lokaci take ganewa ba.

Fita yayi yabarta a tsaye tana jin hauci.

"Kai Anya banyi kuskure ba,gashi gurin Haulat zaije kuma sai ya gayamata abinda ya faru ni nace zan aure shi baya so na,waiyo allah na yanzu ya zanyi? ya zanyi???

Naime naime ta fara yi,chan ta hango abinda take naiman wayarta ce.
"To yanzu wa zan kira?
"Dady nace mishi me?
"Na kira Naufal yawwa shi ,to me zanje mishi ya dawo.

Cikin rashin abinda zata faɗa mishi ta kira shi,yana tafiya a cikin motor shi da tunanin yadda zai fusanci Haulat a ranshi,jaji ringin ɗin waya,baƙowar number ya gani dan bashi da number ta,kamar kar ya ɗauka sai kuma ya ɗauka,tana jin ya ɗauka tai shiru.

"Hello! waye?

"Ya Naufal ka dawo gida yanzu Dady ya zo yana son ganinka."

"Ohhh no! Am coming" yana faɗa ya katse wayar ya juyo da sauri a zuciyar shi yana tausayawa kanshi halin da zai shiga,ya kamata a kyaleshi ya sarara amma yaga alamar ba'a da niyyar barin nashi.

"To ni yanzu idan ya zo me zan ce mishi,ko na ƙara mishi wata ƙaryar ."

"Ah'ah ba zan kara mishi wata ƙaryar ba,gaskiya zan faɗa mishi."
"To idan yaji hauci fah?
"to sai me ba abinda ya isa ya miki"

Murmushi tayi haɗe da juyo kanta"Hm ni ce fah ƴar aljanna ƴar gata kuma shalelen Hajia da Dady,sai abinda na ce,baka da yarda zaka iya Ya Naufal zan juyoka"

🤕waiyo aka ce raahin sani yafi dare duhu  Sabreen kina da ƙuruciya kuma kinyi kuskure.

Tana gaba faɗa ta haye sama tana jin daɗi,wanka tayi ta saka riga da sikit na atamfa shiff-shiff suka mata kamar dan jikinta aka yi kayan,ko mai bata shafa ba,ta fito falo ta zauna akan 1seater ta kunna tivi  tana kallo hankali kwance.

********************

Kwance take akan gadan ta hannuta ɗauke da drip,barci take yi,tun jiya har yanxu bata farka ba.

Momynta ta kalli ƙanwarta salma ta ce"Kai salma lamarin Haulat yana ban tsoro ,ban taɓa tunanin akwai namijin da zata shiga wani hali akan shi ba,tun yaushe nake gaya muku,daga kun ga abinda yake son ya gagareku ,kuje gurin  malam gajere zai warware muku komai amma kun ƙi jira kuke yi saina kama ku na kaiku".

"Ba haka ba ne momy,shi ma yana sonta dan ya sha matsa mata akan ta bashi izini ya turo."

"Yana sonta shi ne zai aura wata ke baki ga hoton ba,yadda suke wa juna kallon soyayya."

"Wllh momy yana sonta bansan yadda aka yiba,kuma ita ma tana da laifi tunda tun lokacin yake mata mita ya fito taƙi amcewa."

"Ni na kasa gane abinda kike son faɗi,kina nufin wanan zoƙeƙen saurayin ne zai tsaya a mishi auran dole,bari kiji yanzu ko wacce mace ba'a zaune take ba ,musamman ma shi wanda kowacce mace ke buri ,to da ƙyalla ido ta ganshi bazata bari ya ƙuɓuce mata ba,amma ita dayake bata da wayau shashace ta zauna haka ai gashi nan tana ji tana gani an ƙwace mata shi,ba yadda zata yi."

"Hm momy kenan ai ko ni kinsan ba hakura zanyi ba,balle Aunty Haulat kuma akan abinda tafi so a duniya ai wallahi zata iya yin komai akan shi,ba zata haƙura ba."

"To da dai yafi mata,ta ɗau mataki,akwai wani sabon malami wanda ƙawata tamin hanyarshi ya iya aiki,aikin shi kamar yankan wuƙa yake,idan ta tashi sai muje a san yadda za'ayi"

"Yawwa momyn mu shiyasa muke sonki kuma muke alfahari da ke allah yabar mana ke."

Murmushi tayi ya ce"Hm dole na so ku,ban yarda da rashin nasara ba,shiyasa zanyi komai akan nasararku.....

.
[12/22, 5:26 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт Bу Gяσυρ O F Hуρє Hαυѕα Nσνєℓѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/22, 5:28 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

.......................................................................................

🌈 *FALALAR* *KWANCIYA* *DA* *AL* *-* *WALA* .

_Hadisi ya inganta daka *Annabi Sallallahu Alaihi wasallam* yace:_

*→(من بات طاهرا بات في شعاره ملك فلم يستيقظ إلا قال الملك :اللهم اغفر لعبدك فلان فإنه بات طهرا)*

...•

_( Wanda ya kwanta da alwala, mala'ika zai kwana acikin mayafinsa bazai gushe ba yana masa Addu'a yana cewa "Ya Allah ka gafartawa bawanka wane domin ya kwanta yana da tsarki (alwala)"_

...•

_*Abdullahi bin Mubarak yaruwaitoshi acikin littafinsa "azzuhudu" (64) ta hanyar hasan bin Zakwaan, Ibnu hibbaan ya fitar dashi acikin saheeh dinsa (1052).*_

...•

_Saidai isnadine mai rauni, domin Alhasan bin Zakwann imamu Ahmad ya raunatashi da ibnu ma'een da sauransu.._

...•

_*Duba Mizanul I'itidali (1/489),*_

...•

_Amma yanada wani hadisin dake mara masa baya wanda imamul dabarany yaruwaito acikin *Mu'ujamul kabeer (13620) da waninsa.*_

...•

_Hadisin dake goyawa wannan baya wanda imamu dabarani ya ruwaito daga Abdullahi bn Umar Allah ya kara masa yarda shine wanda manzan Allah sallallahu Alaihi wasallam yace:_

*→"( طَهِّرُوا هَذِهِ الْأَجْسَادَ طَهَّرَكُمُ اللهُ، فَإِنَّهُ لَيْسَ عَبْدٌ يَبِيتُ طَاهِرًا إِلَّا بَاتَ مَعَهُ مَلَكٌ فِي شِعَارِهِ لَا يَنْقَلِبُ سَاعَةً مِنَ اللَّيْلِ إِلَّا قَالَ: اللهُمَّ اغْفِرْ لِعَبْدِكَ فَإِنَّهُ بَاتَ طَاهِرًا )*

...•

_Ma'ana"ku tsarkake jikinku Allah zai tsarkake ku, domin babu wani bawa da zai kwanta da alwala face  mala'ika ya kwana tare dashi acikin mayafinsa babu wani lokaci a cikin dare da zai shude face wannan mala'ika yanai masa addu'a yana cewa:  " ya Allah ka gafarta wa bawanka domin ya kwanta da alwala"._

...•

_Wasu malamai Suntafi akan hadisine kyakkyawa saboda wasu hadisan da suke mara masa baya._

...•

_Duba *"Attargeebu wattarheeb, na munziry (1/231) da muj'ma'ul zawa'id na haisami (1/226) da Sil-sila saheeha na Albany (2539), dabarani yaruwaitoshi acikin Ausaad (5087) daka ibn Abbas*_

...•

_isnadan hadisin dukkansu babu wacce ta kubuta daka wata tawaya saidai idan ka hadasu wani yana karfafa wani saboda haka Albani ya hukunta hadisin da cewa kyakkyawane idan ka

hadashi da waninsa. *Saheehul Targeebu wattarheeb (599).*_
...•
_*Falalar karanta Suratul Mulk*_
 _Falalar karanta Suratul Mulk (Tabarakallathi biyadihil Mulk) tazo adunqule sannan kuma Falalarta tazo kafin kwanciya bacci a kebance, *Imam *Tirmidhiy yaruwaito  hadisi (2891) da Imam Ahmad a cikin musnad nasa hadisi na (7915) daga Abu huraira  Allah ya kara yarda dashi* daka Annabi Sallallahu Alaihi wasallam yace: ( Akwai wata Sura mai aya talatin a cikin Alqur'ani, ta ceci wani mutum har aka gafarta masa, itace Suratu Tabarakallathi biyadihil Mulk), Sheikh Albani ya ingantashi a cikin sahihul Tirmidhiy "_
...•
_*Tirmidhiy ya ruwaito hadisi  (2892) da Imam Ahmad  (14249) daga Jabir Allah ya kara masa yarda"* Manzon Allah sallallahu alaihi wasallam  ya kasance baya barci har sai ya karanta Alif laam miim Tanzeel da kuma Tabarakallathi biyadihil "Sheikh Albani ya ingantashi a cikin sahih sunanul Tirmidhiy._
...•
 _Abinda yafi  shine mutum ya karanta Suratul Mulk kafin ya kwanta barci a kowane dare, saboda irin yadda Annabi tsira da amincin Allah su tabbata agareshi ya yi, da zai karanta ta a sallarsa ta isha'i to da hakan ya isar masa, saboda gamewar zancen Hadisin farko da ya zo game da ceton Suratul Mulk ga wanda ya karanta ta, domin lokacin karanta ta ba a iyakance shi ba._
...•
_Saidai ba'a shar'anta dawwama akan karanta ta cikin sallar isha'i ba, domin dawwama akan karanta ta nau'i ne na iyakancewa, ita kuma iyakancewa a cikin Ibada bata kasancewa face da dalili, amma don anyi haka lokaci bayan lokaci to babu laifi._

......................................................................
" Ni Naufal yanzu shikenan rayuwata a haka zata tabbata cikin rashin ƴanci,sai abinda Sabreen ta ke so zanyi,ba'amin adalci ba,an aura min ita bata son ta amma ba za'a gyale ni ba,yanzu ya kenan idan naje ma Dady da maganar auran Haulat..

   Da ƙarfin gaske zuciyar shi ta fara bugawa,zufa na ƙeto mishi ta ko'ina a sassan jikin shi,kamar motor ba AC a cikin ta.

Da gudun gaske yake jan motor kamar wanda zai bar ƙasa,cikin ƙanƙanin lokaci ya iso unguwarta su,yana zuwa gurin get ɗin gidan mai gadi ya buɗe mishi gidan da sauri ya kunna kai,bai kai ga gurin da ake yin parkin ba ya tsaida motor ya fito.

Har yana harɗewa dan saurin gurin isa cikin falon,yana isa ya fara kalle-kalle yaga Dady bai ganshi ba,a kwance ya hango ta akan 3 seater ko ɗan kwali babu akan ta,hankali kwance take kallonta tana murmushi tana jin daɗin kallon ga juice a gaban ta.

ƙarasawa yayi kusa da ita bata san ya shigo ba sai ji tayi ya ce,"Sabreen ina Dady har ya koma ne?

Hankali kwance ta juyo ta kalle shi tana murmushi ta ce,Wani Dady?

"Wani Dady? tambayata kike yi wani Dady."

Ɗan yaƙuna fuska tayi ta ce,"Eh!

"Haba Sabreen me kika maida ni,ki kira ni ki ce min Dady ya so yana jira na,kuma shi ne kike tambayata wani Dady."

Ta sigar da yayi maganar ya ɗan bata tausayi abinda tayi niyyar ce mishi ta fasa.

"Ba Dady ba ne,Dady bai zo ba,bana jin daɗi ne kuma ina jin tsoro shiyasa na kira ka dan ka dawo nasan idan ba hakan na ce maka ba,ba zuwan zaka yi ba."

Zama yayi kan kujera ya dafa kanshi, "Sabreen wai dan allah meye matsalarki da ni ?

kai tsaye ta ce mishi "Haulat karka je gurinta ka daina sonta"

"Na so wa? naje gurin kuwa? tashi tsaye yayi kusa da ita ya matsu ,yasa hannuwan shi ya ɗago ta daga kan kujerar da take zaune ,suka fuskanci juna sosai har numfashin su yana cuɗanya da na juna,mayun idanuwan shi ya zuba mata,yakan rasa dalilin da yasa idan ya fara kallonta baya so ya tsaya,kawata-kawata.

duk fitsara irin ta Sabreen saida ta sauke kanta kasa yau kawai yai mata ƙwarjini idanuwan shi suka tsorata ta,mutsu-mutsu ta fara yi alamar ta gaji da tsayuwar.

cikin wata irin murya ya ce"Na so ki! na zo gurinki ɗan iska fa kike ce min"

"am.. ni...nifa.."

"ke fah me?

"Ni bance ka so ni ba,amma karka so Haulat"

"Meyasa?

"Malama ta ce!

Tura ta yayi ta faɗa kan kujerar" Whay? Sabreen meyasa kike son taƙura rayuwar mutane ne,kin san irin son da haulat ke min kuwa? ko kina ganin zaki iya hanani son Haulat,kinyi kaɗan Sabreen,ina son Haulat ita ce muradin Raina da ita zan rayu zan aure ta,idan kuma kina ganin zaki iya hanani to mu  zuba mu gani."

Yana faɗa ya juya zai hau zama har ya taka matakalar ta ce ,"Ya Naufal!

Chikk ya tsaya,ƙarasawa tayi idan yake jin ta a bayan shi yasa shi juyowa.

"Hm ni Sabreen muhammad sai na sa ka mata da waye Haulat ,ko sunanta sai ka manta da shi ." cikin izza da ƙwarin gwuwa tayi maganar.

Dariya ta bashi sosai,ya kalleta yana dariya maimata abinda ta faɗa yayi,"Ke Sabreen muhammad mai taƙama sai kin saka na manta da Haulat."

Anan ya dakata kafin ya murmusa ya ce"So fuuny! how? When Where?

"Sabreen muhammad kike,plss ki tabbatar min ke ɗin ce ta hanyar cika avinda kike faɗa,ko ma nace tatsuniya,yana faɗa ya juya.

"Yaya Naufal har yanzu baka san ko ni wacece ba,ban taɓa faɗin abinda bazan iyaba,duk abinda nace zanyi sai nayi shi,amma zaka ni,wanan alƙawari ne sai ka manta da ka taba sanin wata me irin suna Haulat."

Bai juyo ba jin ta gama maaganar yasa ya wuce abinshi yana mamaki da hali irin na Sabreen.

Yana zuwa ɗakin shi ya faɗa kan gado kanshi yana kallon sama "Meyasa yarinyar nan take magana da ƙwarin gwauwa ne? zata iya aiwatar da abinda ta faɗa ne? to taya?

Bai bawa kanshi wahalar naimo amsoshin ba,dan yasan ba sanin su zai yiba,deep breath yayi "any where! ba zata iya ba ,dariya yayi tuno yadda tayi maganar"Sabreen kenan!

A hankali ya ƙara kiran Sunan "Sabreen" wani irin murmushi yayi wanda bai san dalilin shi nayi ba.

hhhh banza tun yanzu har ya manta da batun Haulat,tun kan aje ko ina😅

~~~~~~~~~~~~~

sama-sama ta fara buɗe idanuwanta waɗan da sukai mugun nauyi,"Naufal!Naufal!

Da sunan shi a bakinta ta ƙarasa buɗe ido,saida ta kalle ɗakin tsabb sanan ta kara rufe ido ,hoton su Naufal Da Sabreen ne kwakwalwarta ta hasko mata ,wani zazzafan hawaye suka fara fito mata,zuciyarta na zafi da raɗaɗi,"Sabreen! Ta faɗa sunan ta cike da muguwar tsana.

Kanwat bai binta wacce suke kira da baby ta shigo ɗakin jin Auntyn tata tana kiran Savreen ya
~~~~~~~~~~~~~

bata mamaki a iya saninta,Naufal ne sillar shigar ta wanan halin,kusa da ita ta kasara,"Aunty Haulat kin tashi? ya jikin? waye kuma Sabreen?

Hawayen ta basu yanke ba,kuma bata da niyyar daina su yanzu.

"Ya isa haka kiyi hakuri Aunty"

Kamr bata san da wata halitta va,a gurin,kiran sunan shi kawai take yi "Naufal Naufal.

"fiye da sau biyar ya kira ba'a ɗauka ba."

Zumbur da miƙe,da sauri baby ta komar da ita"Ki natsu Aunty,karki ɗaga hankalinki akan mutumin da ya yaudare ki...

ta katse babyn da sauri
"Ina sonshi Baby ba zan iya rayuwa idan babu shi ba,pls baby kira min shi "

"Ya isa  ki kwantar da hankalinki bamu rasa abinda muke so Aunty."

"Yana so na Baby basan yadda aka yiba,bai taɓa kira na sau biyu ba,amma tunda kika ga ya kirani sau biyar yana so na,amma taya zai yi aure..

Sittt tayi kamar wacce ka tsaida tuno waye amaryar ta shi ,"Sabreen!

"Waye Sabree?

"Ɗalibata!

"ɗalibarki meye haɗinki da ita kuma?

"Ban wayata ,ki ban wayata na ce, a fusace tai maganar

"Tana ɗakin momy na saka ta a charji."

"Je ki ɗauko min"

"Toh! tana faɗa ta bar ɗakin da sauri.

~~~~~~~~~~~~~

Safa da marwa take yi a tsakiyar falon,"Taya zan saka shi ya manta da ita? ta ya?

"Yaya yana da taurin kai naci,waiyo allah  na taya? nannauyar ajiyar zuci tayi,"""koma taya sai
~~~~~~~~~~~~~

na aiwatar da abinda nai alƙawari, Malama Haulat ba zaki iya yin nasara akai na ba,yanzu taƙamar ki yana son ki ,to zanga abinda zaki yi idan ya manta da ke"

"Waiyo allah yanzu ta ina zan fara yaya murɗaɗan mutum ne,ya zanyi? ya zanyi? dafe kanta tayi rashin madafa yadda zata ɓullowa al-amarin.

"Farrah! ta faɗa a gaggauce,"na kira farrah ,to me zance mata?
"na gayamata gaskiya,a'a yawwa nasan abinda zan faɗa mata"

Da sauri ta haye sama,kai tsaye ɗakinta ta nufa naiman wayarta ta shiga yi da kira farrah.

Hango wayar tayi a gaban mirrow ƙarasawa gurin tayi,ta dau wayar number farrah ta shiga naima,ringin ɗaya tayi farrah ta ɗauka
"Hello farrah pls ki zo yanzun nan akwai maganar da zamu yi me muhammanci."

Cikin zaƙuwa farrh ta ce"ki natsu abin sai ahankali da sannu zaki saba.",dariya tayi sosai.

"Mtseww ke fah banza ce,na saba uwar me?ni idan zaki zo ki zo."

"To fah ai da gudu kuwa ko dan nasha lavari zan zo,yanzu kuw." tana faɗa ta kashe wayar.

~~~~~~~~~~~~~

kyakyyawan ɗaki ne mai ɗauke da kalar fari zalla ,komai na ɗakin fari ne fess irin farin nan me haske,kallon gurin nayi da kyau sai naga kamar na taɓa ganin gurin,to bari dai mu gani.

Kwance suke akan makeken gadon su,kanta na kan lafkeken ƙirjin shi ,mai ɗauke da kwantaccen baƙin gashi,gashin kanta yake shafawa cikin zalo so.

"Ina sonki! ki rayu da ni,zan kula da ke fiye da yadda zan kula da kai na,ki aminci da ni."

Hasken dake ɗakin bai bari ya gane yadda fuskarta take ba,a hankali ya fara sarrafa hannayen shi a sassa jikinta ba inda bai taɓa ba a jikinta,kasancewar ba kaya ajikin ta,wani irin nishin daɗi suke yi,charrab ya tallabo fuskarta bai sha wahala ba gurin haɗa bakin su,cikin zaƙuwa suke kissing ɗin junan,lokaci daya suka rasa natsuwar su,bakin shi yakai🤦‍♀️ya dinga kissing,gaba ɗaya ya fita haiyacin shi.

jan jikinta ta fara yi,"A'a ni ka gyale ni"

Cikin wata irin murya wacce baiyi tunanin abinda zai faɗa zai fito ba ya ce"Sorry don't do ds to me,i need u ,plss try to understand."

bata saurari magiyar da yake mata ba,ta cigaba da janye jikinta daga nashi.
~~~~~~~~~~~~~

Wani irin nishi mai ɗauke da kuka ya fara faɗi,"I need dan allah ki tausaya min karki barni srry i beg u."

Ita ma kukan ta fara yi "No i can't stay with u let go of  me ."

Da ƙarfi ta tureshi ta tashii,hasken da ke ɗakin bai bari yaga inda tabi ba.

Kuka mai tsuma zuciya ya fara yi yana faɗin,"Pls i need u!i need u! don't like ds."

Zummbuurrr! ya miƙe daga barcin da yake yi,da kalmar" i need u" a bakin shi.

Wani nakasaccen numfashi yake futarwa ,gaba ɗaya jikin shi rawa yake yi,ga uban zufa da ta wanke dukkan jikin shi,ga yadda zuciyarshi ke zafi,inda sabo yaci Naufal ya saba da irin mafarkin da yake yawan yi,amma kullum abun zabo yake zuwar mishi,na baƙinciki da takaicin barinshi da take yi a lokacin da yake matsanaicin muƙatar ta.

Cikin wata irin murya ya ce"Meyasa?idan kinsan haka zaki dunga min meyasa kike zuwar min,abin yana ɗauremin kai,kullum ke kike zuwa inda nake kuma ki ban kanki but sai kinga na shiga wani hali sai ki tafi ki barni, whay?

Nidai na ce shirme wa kake tambaya.

ganin ba wanda zai bashi amsar daye buƙata yasa shi ya tashi jiki ba gwari ya faɗa ban ɗaki.

Cikin Sauri Farrah ta tashi ta fara shiri,bayan ta gama shiryawa ta fito falo.

Momy ta kalle ta "Farrah ina zuwa haka kina ta sauri."

"Momy gurin Sabrewn."

"Zaki je ki takura musu ko."

"A'a wllh momy ita ta kira ni."

"Ta kira ki kuma lafiya dai?

"eh lafiya halan wani abun ne,shine nake son zuwa naji."

"To ki gaidar min ita da sosai."

"To zata ji insha allah."

tana faɗa tai gaba abinta,direba yakai ta,kasancewar ba wata lafiya a tsanin su ,yasa ta isa gidan  cikin ƙanƙanin lokaci,tana iya fallon ta kirata a waya.

"Hello kina ina na hauwo ne.?

"kin iso ne? ki shigo ina ɗaki."
ta katse wayar.

Saman ta hau,tana shiga ta ganta akan gado washe baki tayi"Amaryar mu kinga yadda kika yi kyau kuwa gaskiya amarci ya amshe ki."

Harara ta banga mata"Ke dai halinki sai ke."

"Yoou daman ai halin mutum sai shi."

ƙarasawa kan gadon tayi ta zauna ,tana kallon Sabreen ɗin tana murmushi.

"To gani a bani labarin."

saida ta doke ta a cinya sanan ta ce"Ke banza ce wllh,labarin me zan baki,ni idan zaki natsu ki gayamin abinda zan tambaye ki to,idan kuma ba natsuwa zaki yi sai ki gayamin."

"Zan natsu."

Natsuwa farrah tayi ta tattara dukkan natsuwarta akan Sabreen.

Ganin hakan yasa Savreen ta ce"Am.am..kinsan me?

"A'a hmm Yau Sabreen ki magana cikin inda-inda,kin chanja daga savreen ƴar aljannar da na sani."

"Na chanja taya zan chanja ina ban chanja ba niɗin ce dai ƴar aljanna shalelen Hajia",a zuciyarta tayi wanan maganar.

"Kiyi magana Sabreen ko da gaske kin chanja ne."

"Hmm ba zan chanja va,farrah ni ɗin ce dai..

"Na sani ba ƙaramin abu ne zai iya chanja ki ba,amma naga kina dabur-dabur ne,ko maganar ce kika rasa ta inda zaki faɗa min?

"Eh Farrah na rasa ta inda zan fara ne."

"Sabreen ki natso ni ƴar uwarki ce karki ji komai ki gayamin kai tsaye abinda ke ranki."

Kallon Farrah Sabreen tayi ta ce,"Kin san yayah ba ni yake so ba akwai wacce yake so,to shine nake son ya manta da ita,kuma bansan ta inda zan fara ba."

Dariya farrah ta fara yi sosai harda kwanciya kan gadon.

Rai a ɓace sabreen ta ce,"meye haka farrah kin abinda bana so kenan ina magana ana dariya."

Cikin dariyar farrah ta ce,"Ni mamaki ba kika bani."

"Mamaki me kefah banza ce."

"Ba dole ba wai ƴar aljanna ke tambayat yadda zata sa mutun ya manta da wani,bayan kin fini sani."

Tsaki Sabreen tayi "da na sani da zan kira ki ne."

"Kin sani savreen baki na tuna miki."

Zaune ta tashi da tsaida dariyarta ta ce"Sabreen kin iya kiss kisisi shagwaɓa duk wani salon jan hankali kin iya,to da su zaki yi amfani ki sa yaya ya manta da budurwar shi cikin ƙanƙanin lokaci,Sabreen ba zaki sha wata wahala ba gurin mantar da shi akan ko wacce mace domin kin samu dama duk yadda kika yi da shi dole yayi ko da bai so ba,kinga wanan babbar dama ce,idan kina so ki mantar da shi akan ko wacce mace dole sai kin kusance shi kin jashi a jiki kin nuna mishi kulawa."

"Ba abinda bazan iya yiba idan har sai sa ya manta da malama Haulat."
A zuciyarta tayi maganar.

Hannuwanta Farrah ta riƙo cikin kulawa ta ce,"Sabreen kina son yaya ya manta da budurwarshi."

"Sosai ma kuma cikim ƙanƙanin lokaci."

"Yawwa to bari na gaya miki abubuwan da na sani,ya zama dole ki tausassa kalamanki nasan ba'a ɗaki daya kuke kwana ba ,to kiyi yadda zaki yi ku dunga kwana ɗaki daya shi,kuma ki hana shi zuwa gurinta,ki kusance shi sosai duk inda yaje ki bishi,kissa kisisi na yaudara shagwaɓa ki dinga mishi ba zai baki wahala,kin gane inda na nusa."

"Kina ganin hakan zai yasa ya manta da ita kuwa?

"ki yarda da ni tabbas idan kika yi hakan zai manta da ita."

"To bari na jaraba."

"Sabreen karki ce haka lallai ki ɗauka hakan zai mantar da shi ita."

Murmushi Sabreen ɗin tayi dan jin daɗi "Hmm ni fa ƴar aljanna cikin ƙanƙanin lokaci zan saka ya manta da ita."

Dariya Farrah ta ce,"Yaya fa an shigo hannun manya,"

haka suka cigaba da firar su cikin jin daɗi da nishaɗi da kula da junan su.

~~~~~~~~~~~~~

Bayan ya fito daga bayin ya shirya tsabba ya ɗauko wayar shi pic ɗin Haulat yake kallo ya kasa gane dalilin da yasa yafi jin daɗin kallon pic ɗin Savreen akan Haulat,yana cikin kallon pic ɗin kiranta ya shigo ya daɗe yana kallon sunan da yasa mata,kafin ya ɗau waƴar ita ta fara magana.

"Hello dear!

Saida ya lumshe ido dan dalin muryarta.

"Ya kike?

"Ba lafiya ba,meyasa Naufal,"cikin raunanniyar murya tayi maganar.

Hankalin shi ya tashi jin yadda take maganar a ruɗe ya ce,"Kiyi hakuri Haulat kin san ina sonki ba zan iya miki haka ba,Dady na ne ,amma kin san ina sonki ke ce ra'ayina."

Gaba ɗaya farinciki ya mamaye ta duk wani baƙinciki ya kau,ji take kamar bat taɓa shiga cikin ƙunci ba.

Cikin wata irin sigar da ke ɗaga mishi hankali ta ce,"Na sani Naufal ka kwantar da hankalinka bana son ka shiga damuwa."

Yadda tayi maganar ya kashe mishi har tsigar jikin shi saida ta tashi.

Lumshe ido yayi ya ce,"Tnx dear nasan zaki fahimta,karki damu zanje gurin hajiya babba(Wacce  ta haife momy) akan maganar auran mu nasan zata samu dadyna da maganar kuma nasan zai aminci."

Ko kaɗan Haulat bata son ayi mata maganar aure dan baya ganta,shiyasa bata ji daɗin mgnr
~~~~~~~~~~~~~

shi ba,tadai ji daɗi da ya nuna mata yana son ta.

"Yaushe zaka zo,?bani da lafiya fa!

"Subhananllah meye sa meki?

"Hm ciwon son ka da kishinka tun ranar ina nan kwance sai yanzu ta tashi."

Saida yayi jimm shi ya yarda da son da haulat ke mishi na gaske ne,cikin sigar tausayi da ban baki ya ce mata,"Sorry zan zo yanzun nan,ba amfanin wahalar da kanki domin ni naki ne ke kaɗai ba wata maccen da nake so ,ke ce muradi na ra'ayina."

Gaba ɗaya ya kashe mata ji da kalamanci waɗan da suke ƙara narkar da ita,cikin murjar jan hankali ta ce"Okkk sai ka zo dear."

Ta katse wayar,daman ya gama shirin shi tsaba key motor kawai ya ɗauko sanan ya sauko ƙasa,a falo ya haɗe da su Sabreen da farrah.

Farrah tana ganin shi ta miƙe ta ce," ina wuni yaya?

"Lafiya lau ya hajia?

"Lafiya lau tana gaida ku."

Kallon Sabrewn farrah tayi ta ce,"To zan tafi sai anjima."

"To ki gaida momy da Dady."

"Zasu ji." tana faɗa ta wushe abinta.

Shi ma kai yasa zai fita da sauri ta ce,"Yaya ina zaka je,zan biki tsoro nake ji."

Kallon ta tayi kamar zaiyi mgn sai ya fasa ta ya juya abin shi.

"Yaya Naufal!

Banza yayi da ita ya fice abinshi.

Wani ƙululun takaici ya kama cikin faɗa da ɗacin rai ta ce,"Ni nake ma magana kayi banza da ni,wllh yaya kayi sa'a dan ina son cika kudiri na ,amma da ba zan  yafe maka ba,yanzun ma ba yafewa zanyi ƙafa zan ɗaga ma,kuma ba zanyi fushi ba duk abinda zaka min har sai na mantar da kai waye Haulat a rayuwar."

Kamar yana gaban tayi maganar tana gamawa ta hau sama cikin fushi.

~~~~~~~~~~~~~

Momyn su Haulat muguwar macce bara ilimi da imani bin bokaye ɗabi'ar gadon gidan su ne,Dadyn su haulat mutum ne kamili mai rikon addini da sanin ya kamata ɗabi'a ƴan boko bata dame shi ba,tun kafin suyi kuɗi,kullum burin shi yaga yaran shi suna riƙo da addini,yana kwaɓa musu idan suka kauce hanya,wanan dalilin yasa momyn mai suna balaraba ta asirce shi,sai yadda tayi da shi baya iya yin komai daga ita har yaran basu jin tsoran shi ko kaɗan.

Haulat ita ce babba wanda yanzu tana da shekara ashirin da shidda a duniya,tun tana candy ta fara lalewa  da bin maxa lokaci har jami'a,halayen ta iri ɗaya sak da na mahaifiyara,har tafi mahaifiyar ta taƙama fariya gadara uwa uba wulaƙanci da alfahari ,Salma ita ka bi mata ita ma halin su ɗaya,sai auta sakina baiwar allah mummuni ga tausayi saboda halinta yasa basu sonta ko kaɗan dan tana faɗa musu gaskiya.

"A lallai kinji sauƙi   irin wanan waahe baki haka." cewar momyn haulat wacce ta shiga ɗakin haulata ɗin dan duba jikin ta.

Ƙara faɗaɗa fara'arta tayi ta ce,"Eh momy naji sauƙi,Naufal zai zo gani na yanzu."

"Kunyi waya ne? ki son shi sosai,sai yaushe zamu je gurin bokan.?

"A'a tukun na dai,yana so na sosai  momy."

"Hmm haryanzu da sauran ku."

"Ba haka ba ne,momy nafi son irin wanan soyayyar da yake min nafi jin daɗin ta,yanzu kinga indan muka je gurin bokan avin sai koma kamar bin umarni da dole za'ayi mishi akai na,"

"to ita  yarinyar fah zata iya raba ki da shi."

"No momy ba zata iya ba,ni yake so ba ita ba,ni ce ra'ayinshi ba abinda zata iya."

"Haulat kenan ina nan zaune zaki zo ki same ni,bari naje mu fara shiri kafin ya iso".

~~~~~~~~~~~~~

"meyesa zan mata haka? akwai haƙƙin ta mai nauyi akai na,ga alƙawarin dadyn ,yanzun idan tayi fushi ta gayawa hajia fa,ita kuma ta gayawa dady."

Zuciyar shi ta fara bugawa tsoro ya kama shi ,"Sabreen bata da haƙuri zata iya gayawa hajia,nima ban kyauta to yanzu ya zanyi? ya zanyi ko na kirata ne?

Jikin shi na rawa ya ɗago wayar,tsakii ya ji tuno bashi da numberta gashi ya goge list ɗin kiran wayar gaba ɗaya,lokaci ɗaya yaji ranshi ya fara ɓace sai jan zaki yake yi,a hankali ya raba ambaton allah,har ya samu zuciyar shi ta fara sanyi.

Saida ya biya yai mata siyayya kala-kala kayan ci harda kayan sawa ya siya ba ita kaɗai ba harda na ƙannanta,sanan ya nufi unguwar ta su,kamar yadda ya saba shiga da motor shi cikin gidan yanzu ma ciki ya shigar da ita.

Yana isowa harabar gidan ya hango salma sa sauri ya kauda kai daga barin kallonta,gajeran wando ne iya cinya a jikin ta sai ƙaramar riga mai hannun bireziya,ba ɗan kwali a kanta.

Tunda ta hango shi ta fara faɗin,"A dole dole aunty haulat ta ruɗe irin wanan kyau ga izza ga kwarjini,cikin rangwaɗa ta iso gaban shi tana ƙare ma  halitta shi kallo,cikin muryarta mai kama da na Haulat ta ce,"Hi sannu da zuwa."

tun kafin ta ƙaraso gurin shi ya saƙa bakin glass,ɗagowa yayi amma bai yarda ya ƙara kallon ta ba ya ce,cikin iyayi da kilibibi da ƙarya harshe da ba kowani harafin haƙƙin,"Hi!

"Waw ka haɗu over Naufal." ta faɗa a ranta haɗe da kafe shi da ido.

"Akwai kaya a bayan motor."

ya ƙara faɗa ita kuwa yana ƙara birgeta,yadda yake hausar kai idan ba haifaffan ɗan ƙasar hausa ba ne,sai ka ce wani yare yake yi.

ɗan aikin gidan ta kwalla ma kira ,da sauri ya zo jiki na rawa,tana ganin kayan ta ƙara ruɗewa.

Duk da kasancewar ita ce a gaba shi yana baya,amma bai ko kalle ta kanshi a ƙasa har suka isa cikin,falon bai taɓa shiga ba yai yau,wani irin ƙamshi me kama da wari ne ke tashi a falon,daman ya lafiyar giwa balle tayi hauka😅sai ƙamahin nan yana dokan hancin shi ta,fara tsotsoke hancin yana taɓe baki yana yamutsa fuska kamar wanda ya shiga cikin masai😀

Momy haulat na shigowa falon ya ɗago kai ya kalle ta,ai da sauri yai ƙasa da kanshi zuciyar shi na bugawa,ita ma gajeran wandon ne a jikin ta da ƙaramar riga gata ba ƙarama ba.

Har ƙasa ya ɗuka yai gaida ita kamar yadda ya saba kaida manyanshi.

Ya birgeta sosai ga tarbiyya,to ashe dai ƴan isaka suna son mutum mai tarbiyya,a ranta ta ce,"Ah dole Haulat ta ruɗe,gaskiya zan matsawa haulat mu tashi tsaye dan irin so mugun riƙo ake mu su.

A fili ta ce,"Salma kai shi ɗakin Auntyn ku."

Wani irin banbara ƙwai yaji ,wai namiji da suna hajira😅,mamaki ya bala'in kama shi"wai akai shi ɗakin haulat." ,tunani ya fara yi wacce irin al-adace wanan.

Da ƙyar ya iya tashi yabi bayan salma dan tsavar kunya,tafiya kaɗan takai su ɗaki.

"Ka shiga nan ne." salmar ta faɗa ta juya,ya daɗe tsaye a bakin kofar,sanan ya tura ,yana turawa ta buɗe ,yana shiga yaji an rungume shi.

"Sannu da zuwa." ta faɗa cikin wata irin siga.

Yarrr gashin jikin shi ya tashi,kallon ta yayi ai tuni zuciyar shi ta fara bugawa wanda hakan ya haufar mishi da mutuwar jiki.

Janyo shi tayi zuwa kan gadon shi ,kamar raƙomi da akala,kuma wa tayi ta rufe kofar sanna ta dawo kan cinyar shi ta zauna,cikin salo ta fara shafa fuskarshi  akan lips ɗinshi ta tsaya wasa ta fara yi da  su,sanan ta haɗe su hot kiss ta fara mishi,daman an daɗe va'a gamo ba ,ai tuni naufal ya ruɗe  ya fara maida raddi,kan ku ce me sun fita haiyacin su,tura shi kan gado n tayi ta kwantar shi koƙarin cire mishi wando ta fara yi.......

Waiii yau ga rubutun wani iri hakan ya faru ne saboda nayi cikin gaggawa,saboda wanda nayi cikin natsuwa har read more biyar ya goge,ban yi niyar kara yi ba amma kuma nayi.

To fah fans me zai faru a ɗakin Haulat,dan naufal yayi nisa?

shin Sabreen zata cin ma burinta kuwa na son raba shi da haulat ɗin shi.?

To idan burin sabreen    ya ciki Wani irin mataki haulat zata ɗauka akan ta?

Maganar zuwa gurin bokan da momyn haulat ɗin zata ƙara ma haulat ɗin zata yarda?

Idan ta yarda wa za'a ma asirin tsakanin Naufal da sabreen kuma wni irin Asiri za'a yi ma???

.
Sir Anas!
[12/22, 5:28 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ 𝗣σѕт 𝗕у 𝗚яσυρ 𝗢 𝗙 𝗛уρє 𝗛αυѕα 𝗡σνєℓѕ 𝗕σσк 𝗪нαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/23, 1:52 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

.....................................................................

_*Manzon Allaah(ﷺ)* *ya ce;{BA ZAKU WADATAR DA MUTANE TA DUKIYARKU BA, AMMA HALAYENKU SUNA WADATAR DA SU.}*_
°

```[Sahihut Targib;2661]```
~~
_Wannan hadisin yana nuna mana cewa duk yanda zaka ba ma mutane dukiyarka to ba zaka iya wadatar da su ba, amma in kana da kyawun hali, kana mu'amalantar su da ita to zasu wadata da wannan kyawun halin. Allaahu a'alam._

```Allah ta'ala yasa mudace```

_*سبحانك اللهم وبحمدك, أشهد أن لا إله إلا أنت، أستغفرك وأتوب إليك.*_

___________________

Cikin zafin nama Naufal ya janye jikin shi ya miƙe tsaye,yana wani irin numfashi,koƙarin buɗe baki yayi magana yayi,amma ya kasa bakin ma bai iya buɗe shi ba,cikin kasala da rawar da jikin shi ke yi ya gyara jikin shi ya nufi kofa zai buɗe har yakai hannu Haulat ta riƙo shi,juyowa yayi ya kalle ta da rinannan idanuwan shi,ita kanta kasa mishi magana tayi kuma ga bakinta yana son cewa wani abu amma ta kasa,girgiza mata kan shi yayi alamar bazai tsaya ba,sakancewar jikin ta ba ƙwari yasa ya janye hannuwan shi ya fita.

Yana isa falon ba kuwa yaji daɗin hakan sosai dan ko wani baya son ya ganahi a irin wanan yanayin da yake ciki balle su iyayen ta.

Ta gyar ya iya jan motor  ya fita daga cikin gidan,yana fitowa daga gidan ya fara gudu kamar wanda za shi bangon duniya,cikin ƙanƙanin lokaci ya isa gidan su,yana zuwa mai gadi ya buɗe mishi ya shiga,a tsakiyar gidan yayi farkin ɗin motor ya fito.

Ba kowa a falon ko da ma akwai ba zai gane ba tunda halin da yake ciki,kai tsaye ɗakin shi ya nufa,bai kula da Sabreen ba wacce ke kwance akan gadon shi,ya faɗa danne tan da yayi ne yasa tayi ƙara.

"Waiyo Yaya baka ganni ba ne zaka danne ni?

Tashi yayi yana kallon ta da rinnanun idanuwan shi,"Mai ya kawo ki?

"Meya kawo ni ɗakin miji na kuma yaya."

Jin amsar da ta bashi ya tabbatar mishi da taji abinda ya faɗa,dan bai yi tunanin zata ji ba.

"Mijin ki! ya faɗa cikin dakushashar muryar shi.

"Eh ko kai ba miji na ba ne."

Lumshe ido kawai yake yi yana kallon ƙaramin bakin ta,da fararan idanuwan ta  masu hasken gaske kamar auduga.

Ya shagala da kallon ta,kamar ya janyo ta jikin shi yake ji,"Naufal kana da halal ɗin ka fah,to meye kake kai kan ga haram." shi da zuciyar shi suke wanan maganar.

"Kuma daga yau kullum ɗakin miji na zan dunga kwana."

Cikin kiss da kisisi na da shagwaɓa ta ke maganar,sai zazzaƙar muryarta ta ƙara zaƙi."

"Sabreen!

Ya faɗa cikin wata irin siga wacce ta wuce ya kira hakan da sha'awa saidai shauƙin so.

"Zaki iya kwana da ni?

"Eh zan iy....

Bai bari ta ƙarasa maganar ba ya janyota rungumeta yayi,dumm dumm zuciyar shi ta fara bugawa da mugun ƙarfi wanda hakan ya haddasar mishi da kasala.

ƙoƙarin janye jikinta ta fara yi,amma ta kasa dan ba ƙaramin runguma yayi mata ba,ƙoƙarin haɗa bakin shi da tana ya fara yi amma ya kasa dan taƙi natsuwa gashi baya da ƙarfi

"Ahnn waiyo allah hajiata ka sake ni."

Tura ta yayi kan gadon ya tashi a fusace ya faɗa bayi ,ranshi ya ƙuna,ya daɗe yana zuwa kanshi ruwan sanyi ko yaji sanyi a ranahi,amma ya kasa ji,yana mamaki irin rayuwar da yake ciki  haram na binshi halak na ƙin shi.

"Ohhho dai kuma sai na kwana a ɗakin nan kamin hakan ne dan karna kwana ko ,to sai na kwana." tana maganar tana murguɗa baki kamar yana kallon ta,tashi tayi tai kicin  copee da haɗa mishi ta dawo har lokacin bai fito daga bayin ba.

~~~~~~~~~~~~~
~~~~~~~~~~~~~

Bayan farrah ta dawo gida Momy ta tambayeta mai ya faru,ƙarya tai mata, akan cewa ta tambaye ta ne ta koya mata yadda muke yin kunun gyaɗa ranar da muka kai musu taji daɗin shi kuma shi ma yaya irin shi yake so.

Momyn tajo daɗi sosai ta fara tunanin ya fara son ta.

Zaune suke a ɗakin su Dady yana kan gado ita kuma momy tana gaban mirrow tana cire ɗan kunnayen ta.

"Hajiata uwar gida." Dady ya faɗa yana murmushi.

Bata kalle shi ba ta ce,"Na'am abban Naufal."

"Ya kamata su tafi honeymoon ko?

"Eh gaskiya daman ina son nayi maka maganar gashi sun shaƙu da junan su."

Washe baki dady yayi daman yasan auran Sabreen da Naufal alkairi ne,yasan hakan zata kasance kuma ya saka a ranshi ko ba daɗe sai Naufal ya musu godiyar haɗa sun da aka yi.

"To amma wacce ƙasa kike ganin ya kama ta su je?

"wacce suke so."

"A'a bana son su san da maganar sai ranar."

"To zanyu taya zaka gane wacce ƙasa suke son zuwa."

"Karki damu nasan yadda zanyi."

~~~~~~~~~~~~~

Ganin ya daɗe bai fito ba yasa ta fara gyara ɗakin duk da kasancewar Sabreen bata aikin komai a gurin hajia hakan bai  hana ta iya abubuwa ba girki,gyran ɗaki hatta wanki tana yi,bata da ƙyuya ko kaɗan.

Yana fitowa hanci shi yaji wani irin kamshi mai kwantar da hankali lumshe ido yayi ya buɗe,ƙarewa ɗakin kallo yayi kamar ba nashi ba komai tsaf-tsaf

"Wai mijina ashe haka kake daɗewa idan kana wanka."

Zuciyar shi ta fara amsan saƙon muryata sanan kunnuwan shi.
~~~~~~~~~~~~~

Kallon shi ta fara tsabb da sauri tai ƙasa da kai.

ba komai a jikin shi zai towel shi ma ɗan ƙarami ne.

ganin irin kallon da ta mishi yasa shi yin murmushi,lokaci ɗaya farinciki ya mamaye shi wanda bai san dalilin faruwan hakan ba.

Bai ce mata komai ba ya wuce gurin durowar ya buɗe zai naime kayan da zai saka.

"Ah nima daga yau zan ɗinga daɗewa a bayi gurin wanka,ai sai yanzu na gane ace daɗewan da kake yi ne yasa ka zama fari."

Dariya ta kuɓuce mishi mai ɗauke da jin daɗi juyowa yayi ya kalle ta ,ita ma murmushin dariyan take yi.

"To bari naje waje ka gama saka kayan",tana faɗa ta fita a ɗakin.

Murmushi ya ƙara yi,Sabreen tana burge shi,bai san lokacin da ta fara burge shi akan komai tana ba,ƙanana kaya ya saka mara su nauyi, sanan ya sha mai da turare,kan gadon ya koma ya zauna barici yake ji.

Ɗakin ta shigo fuskan nan ɗauke da annuri,"Ka gama shiryawan gaskiya kayi kyau sosai."

jin shi kawai yayi ya ce,"Tnx ke ma kinyi kyau."

Washe baki tayi,"Thanks my miji!

Murmushi yayi,yana jin daɗin sunan mijin da take kiran shi da shi.

copee ɗin ta miƙo mishi,"gashi ka sha zaka ji daɗin shi,kuma zai saka ka kayi barci ka huta."

Hannu ya miƙa ya amsa yana ɗan murmusawa.

"Yawwa miji na!

Sha yayi yana lumshe ido yana jin zuciyar shi wasai,zama tayi a gurin har ya shanye,ta sama kofin.

"Yaawwa sai ka kwanta ka huta."

Amsar umarnin ta kawai yake yi,yadda ta ce hakan yake yi.

Lamo yayi har barci ya ɗauke shi,tana zaune a gurin tana kallon shi.

Ƙarar wayar shi taji da sauri ta ɗako wayar zumbur ta miƙe ganin hoton haulat saida taji ani abu a ranta,kallon shi tayi sanan ta fita da sauri.

"Hello malama ta! har nayi fushi da ke,akan ƙin zuwan ki ɗaurin aure na alhalin an gaiyaci dukkan mutanan da ke garin abuja da ma kewayan ta."

Haulat wacce ke zaune akan kujera jin muryar Sabreen yasa ta miƙe zumbur.

"Naufal!

"No malama ta,miji na,mijin ɗalibata zaki ce."

"Sabreen!

"Na'am malama ta,zan zo ni da mijina na miki godiya dan da bandan ke ba da ban aure naufal ba,ko kin manta kike ce ina son aure  aka gayawa iyaye na."

Saida ta sauƙe gajerar ajiyar zuciya sanan ta ɗaura da faɗin,"Malam ta,jahili daƙiƙi ɗan kauye iri na da aura,ko ɗan gaye mai aji mai ilimi da kyau na aura wanda ko wacce macce take son rayuwa da.?

"Gaya min dan na kasa ganewa,laah ko shi ne wanda malamata ta ke mafarki akan shi?

"Malama ta! ya kike yi shiru ,ki zauna kinji ki natsu,ni Sabreen ba tsararki ba ce,yawwa kuma ki fita harkar miji na,baki da ikon juyamin shi tunda ba ɗalibin ki ba ne,ina fatan kin gane."

"Ƴar aljanna ke dawa kuma?

Ɗagowa tayi ganin hajia ce yasa ta katse wayar a ranta ta ce," *Ni* *DA* *MALAMA* *TA*.

A fii kuwa dariya tayi ta faɗa kan hajiar tana ihuu tana faɗin,"Oyoo ooyoo hajiata.

"Ba wani bayan kin manta da hajiar aure daɗi ko?

Cikin shagwaɓa ta ce,"Kai hajia ba wani daɗi."

"To ya kike? ina ta kewar ki shiyasa na ce bari na zo na ganki."

"Nima hajia ai nayi kewarki sosai."

Fira suka shiga yi sosai da sosai cikin so da ƙaunar juna.

******

Ɓangaran  Haulat kuwa tunda sabreen ta katse wayar ta fasa ihuu,mai rikitar wa.

"Lafiya kike haulat mai ya faru?
A ruɗe momyn ki tambayarta wanda ihunn na ta ne ya fito da ita daga ɗakin ta.

"Waiyo allah na momy na shiga ukku dan allah mu tafi gurin bokan nan."

"Duk da basan abinda ya faru ba,nasan sai irin hakan ta faru,ke ce banza bara wayau ai."

"Sabreen sai na yi ajalinki walahi sai na kashe ki!!

"Mu tafi yanzun nan."

"Matsalar yau baya sauraran mutane sai gobe."

"Ɓakin ciki sai iya kashe ni kafin goben ba zan iya hakuri zuwa gobe ba."

"Tun ranar da nake miki magana kika ƙi saurarata, amma harda shi zamu haɗa."

"No momy bana son a mishi asiri."

"Giyar so ko!,to shi ne wanda ya kamata ayi wa asirin ma ba ita ba."

"Momy baya da matsala ina son shi,soyayyar da yake min ita nake so,bana son a saka shi dole da bin umrnin."

"Hmm haulat kenan ina fatan zaki gane ki dawo hanya."

~~~~~~~~~~

Bangaran Naufal kuwa tunda ya kwanta ya faɗa duniyar mafarkin da ya saba yi,wanda ya kasa bin jikin shi,dan kullum abin sabo yake zuwar mishi.

Kamar yadda ya saba tashi a irin lokacin da tare barin shi yau ma hakan ne,farkawa yayi zuciyar shi na zafi da ƙuna ga zufa ta mamaye shi kanshi a ƙasa.

Sintar muryar ta yayi tana faɗin,
"Miji na ka tashi?

ɗagowa yayi suka haɗa ido,wani iri yaji ,ita kanta kasa tai da kai,"Hajia ta zo tana na jiranka,har ta wuce baka tashi ba,daman yanzu zan tashe ka dan lokacin sallah yayi."
~~~~~~~~~~

Lumshe rinannun idanuwan shi yake yi,ya kasa daina barin kallon ta.

Ganin kamar ita yake kallo yasa ta fara kame-kame,"Lokaci yana tafiya fah!

"Ko barcin bai ishe ka ba ne?

Dariya yayi dan sanan ya tashi ya shiga bayin,yana shiga ta ƙara gyran ɗakin tayi tsaba sanan ta fashe shi da turare.,ɗaukar wayar shi tayi ta kashe sanan ta fita  indomi ta haɗa mishi da kyau sai jus ta kawo har lokacin bai fito ba,zama tayi a bakin gadon.

Yana fitowa yaji ƙamshi me kwantar da zuciyar,idon shi suka sauka akan sabreen wacce ke zaune akan gadon tana wasa zuben da yake hannunta,ya daɗe yana kallon ta,wani iri yake ji a ranshi a duk lokacin da yake kallon ta,yadai kasa gane wani irin abu ne.

Ɗago kai tayi suka haɗa ido kai tai da kai da sauri,"Ka ƙara haske yanzu kawai."

 Murmushi yayi,"Waya gaya miki wanke ke saka mutum yayi haske?

"Gani nayi."

"Gurin wa?

"Gurin mijina kuma yaya nah!

Dariya yayi mai ɗauke da murmushi ,yana jin daɗin sunan da take kiran shi da shi"mijina"

ƙarasowa yayi har kusa da ita wani towel ɗin zai ɗauka ya goge jiki da shi,kuma yana bayan ta.

kaff da ita ya matsu ya miƙe hannun shi zai ɗauko towel ɗin jikin su ya haɗu da na juna,yarr dukkan su suka ji ,ruwan girjin shi ya zuba a fuskarta,wani irin sanyi taji har zuciyarta,tsintar kan shi yayi da son rungumeta, faɗawa yayi kan jikinta ya rungume ta,wani irin baƙon yanayi ya fara ziyartar zuciyar shi,mutsu-mutsu ta fara tana kokarin janye jikinta,"Ka gyale ni bana so." ta faɗa.

Zuciyar shi ta fara buguwa da ƙarfin gaske,wanan maganar tuno mishi da mafarkin shi tayi,kafin ya ƙarasa tunanin shi,ta ƙwace jikin ta,barin ɗakin tayi da sauri ta barshi da bugun zuciya....

.
Sir Anas!
[12/23, 1:52 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт Bу Gяσυρ O F Hурє Hαυѕα Nσνєℓѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/23, 2:16 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

Page 14
..........................................

*Addu'a Ga Wanda Yayi sabon Aure*

بارَكَ اللَّهُ لَكَ، وَبارَكَ عَلَيْكَ، وَجَمَعَ بَيْنَكُمَا فِي خَيْرٍ.
Barakal-lahu lak, wabaraka 'alayk, wajama'a baynakuma fee khayr.

Allah Ya sanya albarka a gareka, yayi maka albarka kum aya hada tsakaninku da alheri.

Wanga page na ku ne iyalan bintu Ahmad ,da tana jamcy ina yinki sosai na gode da kulawar ku,ku sha zaman ku ,ku huta batula tana yinku fiye da tunanin ku.

---

Ya daɗe kwance a inda ta barshi,"Ka gyale ni bana so",maganar ke mishi yawa cikin kai ,ba yau kaɗai aka taɓa gaya mishi ita ba,abinda ya kasa gane meye halaƙar maganar Sabreen da mafarkin shi,ganin kan shi ya fara ɗaukar zafi yasa watsar da tunanin,ya tashi ya saka kaya mara su nauyi wayar shi ya ɗauko yana sun kiran Haulat,"Mtseww na rasa gane meye matsalar haulat a cikin ɗakin take koƙarin taga mun aikata alfasha",ƙara jan tsakii yayi ya jefar da wayar bai ma kula da wayar a kashe take ba.

Hango kwanan abincin da Sabreen ta kawo mishi yayi,murmushi yayi ya ƙarasa gurin ya buɗe ci ya fara yi yana murmushi.

Cikin salon magana irin nashi  ya ce,"Wai zata iya kwana a ɗaki ɗaya da ni,sai bakin tsiya yadda take magana kamar wata mai faɗa a gani."

Saida ya gama cin abincin sanan ɗauko system ɗin shi yana chat,murmushi yayi mai ɗauke da farinciki pics ɗin sabreen ne farrah ta saka a status da kayan makaranta tayi su,nayi kyau sosai fuskar ta ɗauke da murmushi.

"Mijina!

Tsintar maganar yayi a kunnuwan shi,wani murmushin ya ƙara yi,bai ɗago ba ya ce,"Kin ƙara dawowa ne?

Saida ta ƙaraso ta zauna a gefen gadon kusa da shi sanan ta ce,"Eh  ya bazan dawo ba,ni da

zan kwana a nan."

Sai yanzu ya ɗago ya kalle ta,"Zaki kwana a nan?,ki kwana a ɗakin ki."

"A'a ni tsoron ɗaki na nake ji,to meye idan na kwana a ɗakin miji na."

Kallon ta yayi sosai dan tunda ta fara maganar ya zuba mata ido,har zai yi magana ya fasa,ya maida hankali gurin abinda yake yi.

Bata damu da hakan ba ta ce,"Me zan dafa ma?

"Kin san haƙƙin miji akan matar shi ? a maimakon ya bata amsar tambayarta sai tambayarta yayi.

Kai tsaye ta ce,"Na sa ni."

"To gaya min."

Saida tayi jimm sanan ta ce,"Eh ta kula da shi ta mishi biyayya da kula da kayan shi,ta dafa mishi abinci sai me ma? yawwa sai tarbiyar yaran shi sai...

"Taya ake samun yaran?

"Ciki!

"Taya ake cikin!

"Me?!

"Eh taya ake cikin?

Duk da kasancewar bata san abubuwa sosai ba waɗan da suka shafi ma'arata,amma saida taji kunya rufe ido tayi da hannuwan ta.

Kallon ta yayi yana murmushi Sabreen tana burge shi komai tayi abin kallo ne,"Hm meye na rufe ido ko kin san yadda ake yi ne?

kai ta girgiza mishi alamar a'a

"To ba zaki kwana a ɗaki na ba,tunda baki san haƙƙin aure ba." ya faɗa idanuwan shi suna kan ta yaga yadda zata yi.

"A'a ni anan zan kwana."

Yadda tayi maganar cikin shagwaɓa yasa ta kashe mishi jiki lumshe idanuwa yake yi yana kallon ta.

"A'a ba zaki kwana ba,wacce tasan haƙƙin mijinta ita ke kwana a ɗakin shi,kinga ke baki sani ba."

"To ka gayamin  sai in sani."

"Saidai na koya miki."

"Ka koyamin."

"Idan baki so shikenan sai ki kwana a ɗakin ki kawai."

"Ina so toh."

Dariya yayi sosai har saida haƙoran shi suka baiyana sautin muryar shi ya baiyana.

"Sabreen kenan idan  gaji yadda ta iya kiran mijina sai ka ɗauka tasan meye mijin,kamar wata wayayyya idan ka ganta amma a zahiri bata san komai ba,bata iya komai ba", shi da zuciyar shi suke wanan maganar har lokacin kallon ta yake yi yana dariya.

Ganin dariyar tayi yawa sa ya ita ma ta fara dariyar,yana jin ta fara dariyar ,ya ƙara fashe wa da dariya.

 dan dariyarta tana bashi dariya,kamar wasu sababbin kamo haka suka dinga dariya ,dan tsabar dariyar da suke yi bata san lokacin da ta faɗa akan jikin shi ba,kwanciyar da yayi yasa ta kwanta kan ƙirjin shi.

"Sabreen!

"Na'am mijina."

Dariya ta ƙara bashi amma baiyi dariyar ba yadai murmusa.

Kallon ta yake yi ,a ran shi yana faɗin ,"Ina ma kina so na ina sonki,da munji daɗin rayuwa."

"To mai zai hana ka so ni ɗin."

Zaro ido yayi jin amsar da ta bashi ,badai taji abinda ya faɗa ba.

Dariya tayi,"Naji ai."

Lokaci ɗaya girman kai ya shige shi,"Kinji ai ba da ke nake ba,ni bazan so ki ba,dan ba ra'ayina ba ce ke."

Ko kaɗan bata ji zafin maganar shi ma,dan ita ma ba son nashi take yi ba,kuma ba ra'ayin shi ba ce ita,duk abinda take yi dan Malama haulat ne.

A ranta ta ce,"Ban damu da ka so ni ba ni kawai ka manta da waccen banzar wacce bata san darajar muta ne ba,ni ban ma san abinda ka gani a tattare da ita da kike son ta ba."

Shiru suka yi ba abinda kunnuwan su ke ji banda bugun zuciyoyin su,musamman ita da ke saman ƙirjin shi,hannun ta takai saitin gurin zuciyar shi,bata ke komai ba tana dai jin yadda take bugawa ne.

Yana jin ta taɓa ya rufe ido dan ƙaruwa bugun zuciyar ta ƙara yi.

Lumfashin ta kan fuskar shi yake sauka,ɗaga ta yayi yaga tayi barci murmushi yayi,"Savreen kenan mai abin mamaki." zame jikin shi yayi sanan ya ƙara gyara mata kwanciya.

~~~~~~~~~~~~~

"Aunty Haulat dan allah karki biye momy abinda ta ke so kuyi bashi da kyau,kuma ba daidai ba ne,ga tarin zunubai ga ɗaukar haƙƙi gashi kuma baku san abinda zai biyo baya ba,dan allh....

Cikin daka tsawa ta ce,"Keee Sakina zaki gaya mana allah ,ke idan baki fita daga ido na ba,wllh zan ɓata miki rai,ni tsarar ki ce ma,ke a dole malamar addini ko,zaki dinga wani wa'azi an gaya miki ban san allah ba ne,ko ke kaɗai kika taɓa zuwa islamiya da za.....

"Sakina ko." faɗar momy wacce ta shigo ɗakin,kallon Sakinar tayi wacce ke tsugunne a ƙasa.

"Sakina anya kuwa ni na haife ki?da a asibiti na haife ki wllh sai na ce canja min aka yi."

Hawaye ya wanke fuskarta gaba ɗaya ,kuka mai tsuma zuciya take yi,halin uwarta yana ɓata mata rai ga tsanar da take nuna mata da banbanci,cikin muryar kuka ta ce,"Kiyi hakuri."

"Dalla ɓace ki bani guri bazan shasha wawayi wacce ta ɗibo ɗabiyar dangin mahaifinta na."

Jan jiki tayi tabar ɗakin tana kuka mai tsuma zuciya tausayin kanta ya kamata.

Kallon Haulat Momyn tayi ta ce,"Gobe da sassafe zamu tafi ki shirya da wuri dan a katsina ne."

"Momy ban yi tunanin zan yi barci ba,ko tsakiyar dare ne a shirye na ke."
~~~~~~~~~~~~~

"Yawwa Ƴar albarka."

~~~~~~~

"Sabreen ki tashi an kira sallar maqrib."

Sautin muryar shi ya doki dodon kunnan ta,a hankali ta fara buɗe ido,kan fuskar shi idanuwan ta suka sauka,kallon juna suka fara yi,ganin baya da niyyar barin kallon na ta yasa tai ƙasa da kai haɗe da tashi zaune.

"Kai ya aka yi nayi barci?

"Hm ko dan kin kwanta akan ƙirjin mijin ki ne?

Dariya yayi,yana  kallon fuskarta.

"Eh haka ne."

Murmushi yayi a ranshi yana faɗin,"Hmm komai aka faɗa miki yarda zaki yi da shi wawiya kawai."

Tashi tayi ta shiga bayin shi,tai alwala tana fitowa taga baya ɗakin,ita ma ta fita ɗakinta ta nufa saida tayi sallah sanan ta fito kicin ta shiga ta haɗa musu abinci sanan ta koma ɗakinta tayi wanka,doguwar riga ta saka ɓaka ba kwalliya a jikin rigar amma yadin rigar zai tabbatar ma da rigar bata yara ba ce,ta kama jikin ta komai ya fito kamar yarda allah yayi shi,hula ta saka bata ɗaura ɗan kwalin rigar ba.

Turaren miski shi ne  turaran Savreen dan haka shi ta shafa a jikin ta sai da haɗa da wani turare wanda hajia ta kawo mata,ba abinda ta sha ko mai bata shafa ba,amma kasancewar yanayin fatar jikin ta mai kyau ce baka ce bata shafa mai ba.

Cikin tafiyar ta irin ta kasaita ta ƙaraso falon,yana zaune yadda ya zauna zaka tabbatar da hanlakin shi ba'a jikin shi yake ba,saida ta ƙaraso daff da shi ta ce,"Miji na tunanin me kake yi ne?

ɗagowa yayi ya kalle ta,fuska ba yabo va fallasa,kamar bazai yi mata na ba,sai kuma ya ce,"Ina tunanin mosoyiya ta ne," ya kuma ɓata rai ya kau da ganin shi daga gare ta.

Haushin gaske taji cikin raunanniyar murya ta ce,"Ai mata gare ka."

"Matar da bata san haƙƙin miji ba."

"Zan koya kaji," da shagwaɓa tayi maganar.
~~~~~~~

Murmushi yayi har sai da haƙuran shi su ka baiyana,ya rasa dalilin da yasa yake son yi mata magana akan aure.

"Zaka koyamin?"

wanan karan dariya yayi sosai,"Sabreen ƴar hajia."

"Eh ba zaka koya min ba."

"Baki iya ba kike ce kina son aure,saboda fiti na irin ta ki."

"Ba fiti ba ne."

Bai ce mata komai ba dan bashi da lokacin yin magana da ita,baya cikin yanayin jin daɗi ko kaɗan abubuwa sun mishi yawa,gashi yana bugatar macce ga wacce yake so ba aure take so ba,gashi baya jin zai iya kula matar shi.

Ɗakin shi ya tafi,yana zuwa ya faɗa kan gadon.

Ko kaɗan Sabreen bata ji haushi ba dan taɗau alwashin duk abinda zai mata ba gudu ba ja da baya zata shanye har sai lokacin da ta tabbata ya manta da haulat sanan zata rabu da shi.

Ɗakin ta bishi ,da salama a vakin ta,ta isa ɗakin hannuwan ta ɗauke da tiren abinci,kusa da shi ta ajiye abincin,"Ka ɗaure ka tashi ka ci abinci."

Tabbaa yana da buƙatar amici,shiyasa bai yi mata musu ba,ya tashi ta zuba mishi ya fara.

Kallon yadda yake tauna abincin take yi,yana tsaka da ci aka kira sallar Isha'i kasancewar akwai masallaci a nan unguwar ta su.

Yana gama ci ya tashi ya fita,duk da bai gaya mata inda za shi ba tasan masallaci zai je.

Yana fita ta kwaahe kayan da maida su ma'ajiyar su kicin,sanan ta dawo ɗakin ta gyara,ta koma ɗakin ta,tayi sallah,bayan da idar ta koma ɗakin shi baya nan ,falo ta zo ta ganshi zaune yana kallon tivi ita ma zama tayi indian film ne,daga satar kallon shi ta gefen ido,shi kuwa gaba ɗaya hankalin shi ya tattara akan film ɗin kasancewar yana jin yaran,gajiya tayi gashi yaƙi mata mgn gashi bata gane komai a film ɗin.

"Mijina Barci ne ke ji,sai ka tawo," tana gama faɗa ta wuce ɗakin shi kai tsaye,tana zuwa tayi alwala sanan tayi addu'o'in da suka zama jikin ta sanan ta kwanta.

Karfe goma sha ɗaya da rabi ya tashi,saida ya kashe komai sanan ya hawo sama dakin shi ya nufa,bai yi tunanin zai ganta ba,mamaki ya tsaya yana,taya zai iya kwanciya tare da ita,ya daɗe

yana tunani sanan ya je nesa da ita ya kwanta,wani iri ya dunga ji zuciyar shi tana bijiro mishi da su,ƙin sauraran zuciyar yayi,a haka har barci barawo ya ɗauke shi.

~~~~~~~~~~~~~

Tun asubar fari Haulat ta tashi a gaggauce tayi sallah,ta shirya wayar momyn na ta kira saida tayi kira biyu sanan ta ɗauka.

"Momy baki tashi ba ne?

"na tashi jira ni a falo gani nan zuwa."

Ko sallah bata yiba tsabar sauri,a falon suka haɗe lokacin ƙarfe biyar,motor momyn suka hau, kamar waɗan da zasu birnin sin,dan tsabar sauri ko da takwas tayi suna kaduna.

Ƙarfe ɗaya da wani abu suka isa garin katsina,saida suka wuce birnin ta suka fara ratsa dajujjuka sanan momy ta tsayar da motor a wani ƙungumin daji mai yawan duwatsu,kasancewar haulat bata taɓa zuwa ba hakan ba karamin tsoro da ji, Amma tsabar ƙiyayya da guguwar ɗaukan fansa da ke tashi a zuciyarta ya hana ta baiyana tsoron ta.

Tunda suka fito momy ke rike da hannuwan ta,basu yi magana ba ko kaɗan,sunyi tafi mai tsawo akan duwatsu,kafin suka iso wata ƴar bukka wani irin hayaki na tashi daga cikin,da ido momy tayi mata alama da zu juya ma'ana da baya da baya zasu isa har cikin bukkar.

"Ya murmurken kulumruke,ɓaaɓun ɓuturen ƙaranjauuu,Da baya -da baya fitinan jan jaburan ƙaranjauuu na kan dutsen wuta yana muku barka da zuwa.

Sun daɗe a tsaye fuskar su tana fuskan ta waje kamar yadda suka shigo.

Wata irin rikitattan ihu yayi mai tsoro ta zukatan bayi.
Sauka kaɗan haulat da zuba da gudu momy ta riƙo ta.

Wata dariyar yayi sanan ya ce,"An baku izinin zama."

A Hankali suka juyo suka zauna,cikin tsoro haulat ta ɗauke kanta,sakamakon ganin munin halittar shi,gaba ɗaya idanuwan shi a waje su je,girman su ya kai girman ƙwai,ga su jajir,haƙura zakwa-zakwa suma jajir wani ƙazamin miyau ne wawwara ke dilaluwa daga bakin shi,mummuna ne fiye da tunanin ko,ni kai  na ban iya ganin shi ba,sai jaruma bloody ce ta tsaya ta kalle shi ta siffan ta min yadda yake.

Tun da ya kalle Haulat ya ƙura mata ido harda lasar harshen shi.
~~~~~~~~~~~~~

"Me kuke so ai mata? ya faɗa cikin wata irin mummunar murya wacce zata iya tsorata dodan kunne.

Cikin rawar jiki Momy ta ce,"Muna so a haukata ta,sanan kuma ta bar garin gaba ɗaya tayi can wata uwa duniya."

Razananniyar dariya ya ƙara yi,"Wanan ƙaramin aike a gurin  jabarun ƙaranjuuu na saman dutse."

Saida ya ƙara bashewa da dariya sanan ya ce cikin kausassiyar murya,"kin san sharaɗin farko kafin a fara aiki,ya kalle haulat ya lace baki,ƙaranjuuu yana vukatar ki,ya nuna haulat da munanan hannuwan shi kamar na kutare,saida gaban ta yai mummunan faɗuwa a razane ta kalli momy.

Cikin ihuuu ya ce,"Ba'a ma ƙaranjuuu musu  duka ce dukk wanda ya tako nan zai yabi umarnin ƙaranjuuu,kuna ɓata ma ƙaranjuuu lokaci  ."

"Na shiga ukku yanzu wanan mummunan kazamin zai kwanta da ni."

Idanuwan ta har sun ciki taff da kwalla,har lokacin idon ta yana kan momy

Cikin raɗa momy ta ce mata,"Minti nawa ne ki ɗaure kawai kar ran ƙaranjuu ya ɓace ya fasa aikin kuma ya hukunta mu." tana gaba faɗa ta bar ɗakin kamar yadda ta shigo da baya-da baya.

Waiyo ni tirrrr  da irin wanan ƙazamar rawuyar ya allah ka kare mu ka tsare imanin mu ba mu da wayau ba mu da dubara ya allah.

Ko da momy ta koma ɗakin ita ma haulat ta fito cike da ɓacin rai.

Ita ma momyn kwanciya yayi da ita sanan ya basu umarnin wuce wa...

.
[12/23, 2:17 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ 🅿σѕт 🅱у 🅶яσυρ 🅾 🅵 🅷уρє 🅷αυѕα 🅽σνєℓѕ 🅱σσк 🆆нαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/23, 2:19 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*
Page 15
.........................................

Addu'ar Saduwa Da Iyali:

بِسْمِ اللهِ اللَّهُمَّ جَنِّبْنَا الشَّيْطَانَ، وَجَنِّبِ الشَّيْطَانَ مَا رَزَقْتَنَا.

Bismil-lah, allahumma jannibnash-shaytan, wajannibish-shaytana ma razaqtana.

Da sunan Allah. Ya Allah! Ka nisantar da shaidan daga garemu, kuma ka nisantar da shaidan daga abin da Ka azurta mu da shi.

---

Kallon Haulat Momy tayi sanan ta maida hankalin ta gurin tuƙi  ta ce,"To baga shi ba mun wuce gurin minti nawa ne?yanzu wa yasan munyi ,ko shi bai sani ba tunda umarnin ƙanjuung ne,kuma yanzu zaki ga aiki cikin gaggawa."

Duk yadda Momy ta ke ba Haulat baki abin yaƙi dan jikin ta ya mutu,ranta bai so ba,ta so ta hakura amma tsoran abinda zai yi musu idan suka ƙi yarda yasa ta amce amma har ranta ta so hakura.

~~~~~~~~~~~~~
Kiran Sallar farko Sabreen ta miƙe,haɗe da addu'a a bakin ta,sanan ta dirgo daga kan gadon bayi ta shiga ta ɗauro al-wala sanan ta fito,har lokacin yana kwance yana sharar barci abin shi,kusa da shi ta matsa daff hannunta saka a kan shi tana shafa kwantacciyar zumar shi,a hankali kamar mai raɗa ta ce,"Miji na!ka tashi lokacin sallah."

Kamar daga sama yake jin muryarta cikin kunnan shi,a hankali ya fara buɗe ido,har ya ware su kan fuskarta idanuwan  suka sauka,sun daɗe suna kallon s
juna,har wani lumshe ido yake yi,ta shi tayi zubur tabar inda ya ke.

"Ka tashi kar a tada sallah ka rasa jam'i."

Lumshe ido kawai yake yi,yana son macce mai riƙon addini tana ɗaya daga cikin ra'ayin shi.

Sallaya ta shimfiɗa ta tada iƙama raka'atanin fijjir zata yi,yana kallon ta birge shi ta ƙara yi,dan yasan ba'a tada sallah ba nafila ta ke yi,ganin ta fara yi yasa ya tashi ya shiga bayin,saida yayi kwankan tsarki kamar yadda ya saba yi ko wacce safiya.

Lokacin da ya fito da idar tana zaune akan sallayar yana kallon bakin ta yasan tasbihi ta ke yi ,bai ɗau lokaci gurin kallon ta ba,dan karya rasa sallah kamar yadda ta faɗa mishi,farar jallabiya ya saka ya ɗaura hula akan shi sanan ya fice.

Bayan sun idar da sallar saida ya zauna jin huɗuba,abinda bai taɓa yiba kenan tun dawowar shi daga india,ya rage abubuwa da yawa, a rayuwar shi wanda da ba hakan ya ke ba.
~~~~~~~~~~~~~

Tun yana falo ya fara jin sautin karatun al-qur'ani yana tashi,mamaki ya gama shi jin muryar sabreen,kasa yarda yayi har saida ya shiga ɗakin ya ganta tana karantawa,zama yayi yana sauraran yadda ta ke karantun cikin natsuwa kamar wata balarabiya.

"Kai daman yarinyar nan ta iya karatun haka mai daɗin gaske,to a ina ta koya?,a garin su,tun tana shekara tara dady ya gayamishi ta sauke al-qur'ani kuma tun a lokacin tana da hadda izufi goma,amma ban taɓa jin tana yi ba? to a gaban ka zata yi,yadda ta ke da rawar kai da ƙiriniya ba zaka ɗauka haka ta ke da ilimi ba."

Duk shi da zuciyar shi su ke wanan zancen ya tambayi kan shi sanan kuma yaba kanshi amsa.

Ya daɗe yana sauraran zazzaƙar muryarta,wanda bai san lokacin da barci ɓarayo ya ɗauke shi ba.

Saida ta haɗa izufi biyar sanan ta rufe al-qurnin ta yi addu'o'in naiman tsari kamar yadda addinin ya zo mana da su sanan ta tashi ,ganin yayi barci yasa ta fita a ɗakin ,ɗakin ta,ta wuce wanka tayi dogowar riga ita ce kayan da tafi so a rayuwarta,ta atamfa  da saka orange colour da ɗan ratsin brown sai fari,kayan sun mata kyau ainun ɗauren gwaggwaro tayi  ganin kicin zata shiga yasa ba tai komai a fuskarta.

Karin kumallo ta haɗa musu kunon gyaɗa sai soyayyan danganin turawa sai ferfesu hanta,sai ta soya indomi da kwai da sayayyan kwan sai lipton.

Bayan ta haɗa komai sanan ta koma ɗakinta,ta ƙara yin wani wankan dugowar riga ta ƙara saka wa,ƙirar dubai pink  ne kalar rigari sai akai adon rigar da blue ɗin stone,rigar ba irin me kama jiki ba ce,amma duk da haka ta amshi jikin ta kuma kirarta ta baiya na,ɗan ƙaramin gyalen rigar ta yafa sanan ta feshe jikin ta da turaren da shi ne turaren da ta saba saka wa,light makeup tayi sai plat shoe kalar blue,tayi kyau ainun.

Safa da marwa yake yi a cikin bedroom ɗin shi ,"Me ya kamata nayi? Savreen zaɓin iyaye na ce,kuma bata da matsala ko kaɗan nabi umarnin mahaifana na zauna da mata ta,to amma ba ra'ayina bace,meye matslar hakan zan iya rayuwa da ita,inah da kamar wuya ita Haulat fa? ba da aure ta ke so na ba,na ƙyale ta kawai,a'a taya bayan ina son ta,ita ma tana so na,soyayyar ƙarya tunda ba auran ka ta ke son yi ba."

da ɗan ƙarfe yake maganar yana girgisa kai,"Taya? ba zan iya rayuwa da ita ba,to ya zanyi."

Marar shi tai wani irin murɗawa dafe ta yayi ,ya dawo ya zauna,"Ina bukatar macce,wata zuciyar ta ce mishi,"To ai kana da ita halal ɗin ka ce,ba zaka sha wahala gurin shawo kan ta ba."

"Zata raina ni."

Wata zuciyar ta ce mishi,"Wani raini mutuni na sai girman ka da zata ƙara gani,kayi tunani mai

kyau."

"Assalamu alaika!

Bai tsaya tantance muryar ta ba ya amsa sallamar.

ƙarasowa ciki tayi saida ya lumshe ido dan wani irin asirtaccen ƙamshi da ya doki hancin shi,a hankali ya  buɗe idannuwan shi ya sauke su akan ta,wani irin baƙon yanayi ya siyar shi zuciyar shi.

Ita kuwa ganin hakan yasa ta ƙara faɗaɗa fara'arta harda fari da fararan idanuwan tayi,ƙara takowa tayi daff da inda yake zaune ,ta duƙa cikin wata irin muryar ta ce," Ka tashi lafiya? ya gajiya?

Har lokacin bai ɗauke idanuwan shi a kan ta ba,wani irin abu zuciyar shi ke mishi.

jin yayi shiru yssa da ɗago kai wani murmushin ta ƙara sakar mishi,bai san lokacin daya maida mata martani ba.

"Tana gama kwarin kumallo ka sauko mu ci."

Ɗaga mata kai kawai yayi,ta tashi ta fara gyara ɗakin har lokacin yana nan ya kafe ta da ido,duk inda ta je binta da ido yake yi.

"Kayi wanka ne?

"A'a." ya faɗa a taƙai ce.

"Ba zaka yi yanzu ba ne."

"Zanyi."

"To  ka tashi dan Dady ya kira ni wai muje yana naiman mu."

Tana rufe baki ya tashi,gyara gadon tayi sanan ta fita.

Bayan ya fito daga bayin yaji wani irin ƙamahi wanda duk lokacin daya ji shi yakan ji wani iri a ranshi.

Wanan shi ne sirran turare Naufal hatta so yana tsufa komai yana tsofa kuma yana gundura amma turare baya tsofa baya gundura kullum ka ji ƙamshin shi sabo ya ke zuwa kamar baka taba ji ba.

Kallon ɗakin yayi tsaf komai a kimtse yadda yake ganin sabreen da sakuwa bai taɓa tunanin zata iya aiki ba,yana son tsafta a rayuwar shi.

Tuno zasu je gida yasa ya saka shadda blue tasha aikin sama ,ta mishi kyau ainun da hula ita ma blue takalmi blue saida ya gyara fuskar shi sosai da kayan kwalliyar maza san ya feshe jikin shi da turarruka  ma su ƙamahin gaske,zai yanzu ya tuno da wayar shi naiman ta yayi bai gane,bai damu ba dan yasan sabreen zata san inda ta ke tunda ita ke gyara ɗakin.

ƙasa ya sauko tun daga kan matattakalar ya hango ta,har ya iso cikin falon idan shi yana kan ta.

Jin ƙamshin turaran shi yasa ta waigo haɗa ido suka yi ,ta sakar mishi wani amintaccen murmushi shi ma sakar mata yayi.

"yawwa muyi sauri kar ya gaji da jiran mu."

Bai ce mata komai ba,gurin abincin ya wuce ya ja kujera ya zauna,ita ta zuba mishi gunun gyaɗa ta zuba mishi har saida ta kusa shika cup ɗin dan tasan yana son gunun gyaɗa sosai.

"Sabreen!

Saida ta ɗago ta kalle shi sanan ta ce,"Na'am miji na!

"Kin dafa lipton?

"Eh gashi nan shi zaka sha?

"Eh plss ki matsamin lemon tsami a ciki."

"Baka da matsala."

Kicin ɗin ta koma ta matsu ruwan sanan ta dawo,ta haɗa mishi da lipton ɗin.

"gashi sai me zaka ci?

Dan galin turawa da kwai su kama kaɗan ya iya ci.

"Sabreen ina waya ta?

"Wayarka tana ɗaki."

"Ki ɗauko min ban ganta ba."

Tashi kawai tayi ta dufi ɗakin nashi inda ta ajiye nan ta ɗauko,kunna wayar ta,pic ɗin shi ne

wanda ya ɗauka a india a gaban wayar saida ta kalli pic ɗin sosai sannan ta taɓe vaki,"Ko kyau ina farin namji ya ga kyau kamar wani macce,dariya tayi ta ƙara cewa,"Uban yan iyayi zaka ga aikin Sabreen lokacin da ka ji ka manta wata haulat a rayuwar ka."

Number Haulat ɗin ta shiga naima,"My dear", ta ga an rubutu blocking ɗin number tayi.

Tai murmushin mugun ta sanan ta ce,"Hm malama ta nasan ke wacece,amma ke baki san ko ni wacce ba,ba taƙamar yana son ki ba idan ya manta da ke zanga tsiyar da zaki iya yi."

A falon ta same shi,miƙa mishi wayar tayi,"Gashi!.

Amsa kawai yayi,"Muje ko."

"Eh.

Kamar wasu masoyan gaskiya haka suka jeru sun yi kyau gashi kayan su iri ɗaya.

~~~~~~~~~~~~~

Tun a hanya Haulat ke kiran number shi wayar a kashe kamar tayi kuka.

"Momy tun jiya wayar shi a kashe ya zanyi momy?

"Ki kwantar da hankalin ki,ai na daɗe ina gaya miki kaidin mata da yawa,halan ma duk ita ce,amma yanzu za'ayi maganin ta dan uban ta shege idan ta fara bin bola sai mu ka tsiyar abun."

Duk yadda Momy ke kokarin kwantar mata da hankali ta ƙasa,dan hankalin ta ya kasa natsuwa duk wani iri ta ke ji a ranta,wanda bata san ko meye ba.

~~~~~~~~~~~~~

Cikin ƙanƙanin lokaci suka isa gidan su Dady,cikin natsuwa da sallama a bakin su ,su ka isa cikin falon.

Suna isa dady ya taso da kan shi ya tarbo Sabreen riƙo hannun ta yayi su ka dawo inda ya ke zaune kan cinyar shi  ya zaunar da ita,ba yau ba ne ranar farko da dady ya taɓa zaunar da ita kan cinyar shi ba,amma ba ta taɓa jin kunya irin na yau ba,kasa gaida shi tayi dan kunya.

"Sabreen ya kike? ina fatan komai lafiya,idan yana miki wani abu da baki so ki gaya min karki ji komai,kinji Sabreen."

Saida ta ɗago kai ta kalle shi,shi ma kallon ta yayi yana son jin amsar da zata gayawa dady.

Ƙasa tayi da kan ta,"Ba komai dady."

"Kin tabbatar."

"Eh!

Ajiyar zuciya ya sauke sanan ya ce,"Masha allah komai daɗi,haka ne ke,kallon Naufal dady yayi,ƙasa naufal ɗin yayi da kai yana shirin gaida shi ya tari hanzarin shi.

"Naufal ka haifu,Lallai ka nuna min kai ɗa ne,na gari mai tarbiyar,naji daɗi Naufal na gode ma ka,da ka riƙe min Sabreen da kyau allah ya biya ka na god...

"Dadyn dan allah ka daina godiya,ni ya kamata nayi godiyae."

Farinciki da jin daɗi ya ƙara mamaye  dady,ƙarara fuskar shi ta nuna irin farincikin da yake ciki.

Duk wanan abun da ake yi Momy da Farrah suna zaune a ɗakin.

"Nima zan ma godiya Naufal ka cika min burina,Jibe insha allahu za ku tafi honeymoon kasar turkey..

.
[12/23, 2:19 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Ƥσѕт Ɓу Ꮆяσυρ Ơ Ƒ Ӈуρє Ӈαυѕα Ɲσνєℓѕ Ɓσσк Ꮃнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/23, 2:22 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

Page 16

---

*_السلام عليكم ورحمة الله وبركا ته_*
_*بسم الله الرحمن الرحيم*_

_*Sayyiduna Aliyu yace; Manzon Allaah(ﷺ)* *yace min; KA RI'KA (ADDU'A KA NA) CEWA; {YA ALLAAH KA SHIRYENI, KUMA KA DAIDAITA NI (A KAN HALAYEN 'KWARAI.}*_
°

```[Sahihu Muslim;2725]```
~~
_Muma sai mu dage da yin wannan addu'ar neman shirya da kuma hali na kwarai. Allaahu a'alam._

```Allah ta'ala yasa mudace```
◦
_*سبحانك اللهم وبحمدك, أشهد أن لا إله إلا أنت، أستغفرك وأتوب إليك.*_

......................................................................

Gaba ɗaya jikin Naufal yayi sanyi tunanin halin da zuciyar shi ta ke ciki yake yi.

Ganin yayi shiru yasa Dady ya ce mishi, "Naufal ko ƙasar ce ba ka son zuwa?

Murmushi yayi sanan ya ce,"A'a ina so sai dai ban san ko Sabreen ba."

Kallon Sabreen Dady yayi wacce har yanzu tana kan cinyar shi,cikin murmuahi mai ɗauke da farincike dady ya ce,"Sabreen ba ki son zuwa ƙasar ne?

"Ina so."

Ai nasan ba zaki ƙi ba my Sabreen."

Haba Alhaji ka barsu mu gaisa mana,tun zuwan ta ka janyo ta jikin ka,ka hana ta zuwa guri na,Sabreen ta so kin ji."

Dariya dadyn yayi ya ce,"ba gwara ke ba kuna haɗuwa ni fa tun bikin sai yau ba abin ki ce ta zauna a guri na ba ne."

"Ah...Momyn zata yi magana ya katse ta.

"Sabreen ta shi ki je gurin momy ko."

A kunyace ta miƙe ta isa inda momyn ta ke,jikin jin kunya ta gaida ita.

Bayan zun gaisa ta koma inda farrah ta,cikin raɗa ta ce mata,"Oh su Aunty Sabreen manya,to ki tabbatar kin dawo min da baby a cikin ki." Cikin dariya da zolaya tayi maganar.

Muntsinin ta Sabreen tayi har saida tayi yar ƙara sanan ta gyale ta,taja bikin ta tai shiru kamar ruwa ya ci ta.

Dady ya ce,"Sai kun dawo ne za'a yi maganar makarantar Sabreen ko kuwa,"ya faɗa yana

kallon Naufal.

"Eh a bari mu dawo kamar zai fi,amma yadda ka gani dai."

Sai da Dady ya ɗan murmusa sanan ya ce,"Naufal kai fa mijin ta ne,ka fi ni iko a kan ta yadda ka ce ɗin hakan za'a yi."

Fira sosai suka yi harda Naufal ɗin dan tunda su ka zo basu fita ko ina ba har Dady ,sai lokacin sallah su fita su dawo har la'asar sanan suka fito,sai sun biya gurin hajia kafin su wuce.

Kafin su tafi saida Momy ta bata magangunan mata kala-kala tun daga zamfara da sokoto ta saka aka siyo mata,ta kuma ce mata kar ta yi amfani da su sai sun je honeymoon sanan ta sha.

~~~~~~~~~~~~~

"Kin san meye honeymoon kuwa? bai kalle ta ba yayi maganar.

Saida ta kalle shi sanan ta ce,"Eh ba shi ne mata da miji ke zuwa wata ƙasa ba,cin amarci."

"Shi fa zamu je."wanan ƙaran ya kalle ta.

"Eh ko baka so ne,ni fa matarka ce ta sunna."

Ta taɓo mishi idan yake mishi kaikayi,zuciyar shi ta fara dan bugawa zuciyar  shi ta mishi ce,"Tsoran me kake  ji Naufal wanan ne gaskiyar lamari ita matar ka ce ta sunnah."

Da sauri ta riƙe hannuwan shi,ta ce a ɗan ruɗe,"Yaya ka manta ne zaka wuce gidan hajia ko ba ka so na je ne?

Taka birkin motor yayi da sauri,kallon ta yayi ido cikin ido sanan ya ce,"Yanzu idan na ce bana so ki je ba zaki je ba?

"Eh Momy da hajia duk sun gaya min duk abinda miji na ya ce baya so kar nayi kuma idan ya hanani yin abu kar nayi,idan ka ce baka son zuwa ba zan je ba."

Lumshe ido yake yi yana kallon lips ɗin ta yadda ta ke maganar,idanuwan shi har sun canza kala bugun zuciyar shi ya ƙaro,cikin izza da zafin nama ya janyo ta jikin shi ya haɗa bakin shi da tana ya fara kissing ɗin ta,abin mamaki yau bata yi koƙin ƙwatar kan ta ba,cikk ta tsaya yana juya harshen shi cikin bakin ta,shi kuma jin ta natsu ya saka ya ƙara zaƙewa,lalubarta ya fara yi ,jin ya fara taɓa jikin ta yasa ta ja jikin ta da sauri tana sauke ajiyar zuciya.

shi kuwa gogan kife kan shi yayi akan sitiyarin motor yana sauke nannauyar ajiyar zuciya,zuciyar shi kamar ta fasa ƙirjin shi ta fito dan bugawan da ta ke yi.
~~~~~~~~~~~~~

Bata ce mishi komai ba,har tsawon lokaci ba wanda ya iya yin magana a cikin su.

Ganin bashi da niyar magana gashi yamma na yi,ya saka ta mishi magana,"Yamma tana yi mu tafi."

Bai yi tsammanin jin wanan maganar daga bakin ta  ba,yayi tunanin ɗan iska zata ce mishi,ɗagowa yayi yana so su haɗa ido taƙi bari.

"Sabreen! da ƙyar maganar ta fito dan ma ta saba da jin maganar shi da ,da ne ba zata ji abinda ya faɗa ba.

Kan ta a ƙasa ta ce,"Na'am."

Har lokacin idon shi yana kan fuskarta,yana son fahimtar yanayin ta,ganin yana ƙara shiga wani hali dan kallon ta yasa ya ja motor da gudu baya ya juya ,ya kai ta gidan hajiyar.

Sun isa harabar gidan yayi farkin ,yana yin farkin ɗin ta fito da gudu tai cikin gidan.

Kallon yadda tayi gudun yayi,yasan irin yadda ta ke son hajia a fili ya ce,"Ke nan Savreen zata iya zama da ni a matsayin mijin ta,hakan yana nufin ta aminta da ni,an ya kuwa ,koma me nene zan gano."

Shi kaɗai ya ɗinga saƙa yana warwara.

Ita kuwa tana isa falon ta dunga kwala ma hajia kira.

"Hajia ta! Hajiata!

Hajiyar tana ɗakin ta da sauri ta fiton falon jin muryar Sabreen Rungume juna suka yi suna ihun jin daɗin ganin juna.

Saida suka gaji da tsayuwar sanan suka zauna sanan suka gaisa cikin farin ciki da jin daɗi.

Bayan sun gama gaisawa d daɗewa sanan ya shigo da sallama a bakin shi.

Hajia tana amsawa ta ce tun kafin yakai ga zama,"Da ba zaka shigo ba ne,ko baka so ta zo ba ne."

Saida ya zauna sanan ya kalle ta yana murmushi ya,"Na isa na hana ta zuwa gurin bugun zuciyarta muradin ranta."

Dariya suka yi su dukkan su kuwannan su yana cikin yanayin jin daɗi,bayan sun gaisa da shi

suka fara fira.

Kallon Naufal hajia tayi fuska ɗauke da annuri ta ce,"Naufal na gode,na gode lallai ka haifu,duk da Sabreen jikin ka ce dole akwai so a tsanin ku amma dole mu jin ji na ma dan abinda kayi ba ko wanne ɗa ba."

"Haba hajia ni kashe min jiki kuke idan kuna min godiyar ne."

Amma can ƙarƙashin zuciyar shi tunanin abinda ta ce yake yi,"Akwai so a tsananin ku" yana son ya gane wani irin so ne wanan.

Kallon ta yake yi yana son su haɗa ido amma taƙi yarda da hakan ta faru.

A zuciyarta ta ce,"Ba wani so wanan ne zai so ni, tabb kin saɓa number hajia."

Suna gidan aka kira sallar maqrib ya fita yayi su ma,su ka tashi zuka yi,bayan ya dawo saida suka ci abinci sanan suka tafi.

Saida hajia ta bata garin magarya da sabon magarya sanan suka tafi.

Har suka isa gida ba wanda yai ma wani magana,ɗakin shi ya tafi ita ma ɗakinta ta wuce dan ta chanza kaya.

Dan samon tayi wanka ta saka riga dugowa mara nauyi ba kwalliya a jikin rigar sai da ta fashe jikin ta da tararen da ta saba amfani na shi sanan ta fara gyara ɗakin ta duk da kafin su tafi ta gyara.

Yana isa ɗakin shi ya faɗa kan gadon kan shi na kallon saman ɗakin,sauraran bugun zuciyar shi ya tsaya yi,ya daɗe a haka sanan ya tashi yai toilet.

~~~~~~~~~~~~~

Kuka sosai haulat ke yi,"kin gani momy har yanzu ba wani labari tun muna kan hanya kika sa a fara saka ido amma ba wani labari sai ganin su ma da aka ce anyi suna jin daɗi  har da kiss fah aka ce ya mata."

Dafa ta momy tayi,"Ki kwantar da hankalin ki,na gaya miki aikin shi a ranar ya ke yi,kuma yanzu baki ga gobe tayi ba ance bata hauka ce ba,yau komai dare sai aikin mu yayi ki kwantar da hankalin ki."

"Hankali na ba zai iya kwanciya ba momy."

"Na gaya miki ki kwantar da hankalin ki idan wani abu bai faru ba sai mu koma goven."
~~~~~~~~~~~~~

Duk wanan abun da suke yi sakina tana jin ,idanuwan ta sunji ja kwalla dam a idon ta.

Cikin  raguwar murya ta ce,"Momy ba kyau kuyi tsoran allah,dan.....

"keeeeee dan uban ki ,ki ɓace  daga nan kafin na buɗe ido na."

Gaba ɗaya jikin sakina rawa ya fara yi,da ƙyar ta iya jan ƙafar ta,ta bar gurin.

Ita kuwa momy taita vamvami kamar karamar mahaukaciya sai kwace ma sakina albarka ta ke yi.

~~~~~~~~~~~~~

Da sallama ya shiga ɗakin yana tashin ƙamshi,ganin kamar hankalin shi baya jikin shi yasa,ta lallaɓa ta vayan shi ta rufe mishi ido da hannuwan ta.

Mai da idanuwan yayi ya rufe su,dan yasan ita ce,a hankali zuciyar shi ta fara bugawa hannayen shi ya ɗauka kan na ta,sai da yaji wani irin jin lallasar fatar mai.

Cikin wata irin siga wacce shi kan shi ba zai iya bambance yanayin ba ya ce,Sabreen!

"Maimaita."

"Sabreen!

"Waw na baka kyautar Abuja harda kaduna ba,kasan me? ta sake shi ta dawo inda ya ke zaune taff da shi ta zauna,har suna gogan jikin juna.

Kallon ta yayi ya sake mata wani irin kyakyyawan murmushi sanan ya ce," taya zan sani."

"Ka bala'in iya kiran sunan da indiyanci kike kira gaji daɗi ku....

Dariya ta fashe da ita sosai ya dara ita kuwa bin shi da kallo kawai ta ke yi dan bata ji abin dariyar da ta faɗa ba.

Saida yayi me isar shi sanan ya tsaya bai ɗaure fuska ba ce kalle ta ya ce,"Wai da indiyanci,kai sabreen kina da abin dariya."

"Toh ai gaskiya na faɗa wa gaji yana kira na irin yadda kake kira  na?

"Hajia da Dady."
~~~~~~~~~~~~~

"A'a su da hausa su ke kira."

Murmushi yayi mai ɗauke da annuri,"Hm kina da abin dariya,na tambaye ki."

"Uhum!

"Wai lokacin nan da na zo gurin hajia a lokacin ban daɗe da dawo wa ba,har na same ki a falo kina kallo kika banza da,naga kina da dariya a lokacin me ya sa ki dariyar?

Yana kai ayaa ta fashe da dariya,kallon ta ya  ke  yi tana dariya kamar irin wancen lokacin,taya da yayi.

Saida suka yi me isar su sanan su ka tsaya,suna kallon juna,wani irin abu ke ta so mishi a rai.

Cikin yanayin jin barci ta ce,"Barci na ke,bari na kwanta."

Bata jira cewar shi ba ta,tashi saida ta shiga bayi nayi al-awla sanan da tayi nafila tayi addu'o'i iri iri  sannan kwanta,duk yana kallon ta,tana kuma ƙara birge shi,addu'o'in da yaji tana yi yayi magana dan wasu mai iya ba,wasu ya manta su.

"Na hakura nayi rayuwata da ita,bata da matsala ko kuma hakan zai saka iyaye na su ji daɗi sosai."

Nannauyan numfashi yayi sanan ya ƙara faɗin,"kai abin is not easy taya? to daman ai  matsalar tawa ce," dafa kan shi yayi wanda ya ɗau zafi,wata zuciyar tana tausar shi akan ta zaduda kawai wata kuma na bijiro mishi da abubuwa marasa amfani.

Safa da marwa ya kw yi a tsakiyar ɗakin yana kuma kallon ta ,ta duƙunƙune guri daya tana varcin.

Tausayin kanshi ya kama shi tabbas yana da buƙatar macce,kuma yasan idan har mai samu yadda yake so ba,har wani ɗan lokaci zai iya samun matsala.

Kamar wanda aka ba umarnin ya zauna can kuma ya tashi tsaye,hura hanci ya fara, a fili ya ce,"Ba zan iya cutar da kai ba,bayan allah ya ƙubutar da ni."

Murmushi yayi me ƙyayatarwa har da lumshe ido da hura hanci,"Ban san ta yadda zaki ji al'amarin ba amma dole zanyi Sabreen, ba yadda..

.

[12/23, 2:22 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт Bу Gяσυρ O F Hурє Hαυѕα Nσνєℓѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/23, 2:24 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

Page 17
....................................................

Kwanciya yayi ɗan nesa da ita kaɗan,ya daɗe yana saƙa da warwara, yana jin tana barcin ta hankali kwance,shi kuwa sai juye yake yi sai ƙarfe ɗaya saura sanan barci ya ɗauke shi.

Kamar dai kullum kiran sallar farko ke tada ita yau ma hakan ne,tana tashi da kunna hasken ɗakin kallon inda yake tayi saida tayi murmushi ganin yadda yake barcin hannayen shi gaba ɗaya a ƙirjin shi.

Saida tayi alwala sanan ta matso kan shi ta taɓa sanan ta ce,"Miji na ka tashi lokacin sallah."

Shiru barci yayi nisa ganin hakan yasa ta  matso kusa da hunnan shi ta hura mishi iska,motsi yayi amma bai buɗe ido ba,hancin shi ta fara ja nan ma shiruu na koma gurin idon shi ta fara shafa batar idon nan ma shiruu,ganin hakan yasa takai hannunwan ta kan lips ɗin shi ruwan alwalan da bai bushe ba na hannunta shiyasa lips ɗin suka jiƙe,shafasu ta ke yi,ta shafa da ƙasa ta shafa na sama nan da nan ya fara juya su kamar me kokarin cin wani abu,ganin hakan yasa ta fashe da dariya,wacce tai nasara isa ga dodon kunnan shi.

Firgittt! ya tashi kallon ta ya ke yi cike da mamakin abinda ta ke ma dariya.

Cikin dariya ta ce,"Wai Halan yunwa kake ji."

Cikin rashin fahimta ya ce,"Me?

"zan tashe ka ne ka ƙi tashi shi ne ta hura ma kunne na jajja hancin ka ƙi tashi shi ne da na taɓa ma baki ka fara motsawa kamar zaka ji wani abun."

Murmushi yayi labarin sabreen  yana bashi dariya ya kuma bashi mamaki.

"To meye na dariya."

Har ta buɗe baki zata yi magana akai kiran sallah,"Kai ka tashi."

Tana faɗa ita ma ta tashi ta shimfiɗa sallaya sanan ta fara sallar nafila kamar yadda ta saba.

Ganin hakan yasa shi ma ya tashi ya faɗa toile bai ɗau lokaci ba ya fito gurin saka kaya ba bai ɗau lokaci ba ya fita.

Bayan ta idar da sallah ta fara aikin gyara ɗakin saida ta ƙimsa komai sanan ta wuce ɗakin ta,tana zuwa ta gyara shi sanan ta nufi kicin.

Yau bai zauna  dan barci bai ishe shi ba,yana shigowa falon yaji ƙamshin abinci yana tashi,kallon hanyar kicin ɗin yayi kamar ya shiga sai ya fasa ya wuce ɗakin shi bai yi mamaki ganin shi tsab ba dan yasan halin ta ne,ya kula da ita sosai tana da tsabta har ta kusa fin shi,kwanciya ya koma yayi.

Bayan ta gama haɗa komai ta koma ɗakin ta,tai wanka ta shirya cikin riga da siket na atamfa,Karuwan jiki sabreen gare ta,irin jikin da ko wani irin shiga yana amsar shi,irin shi ne ka kan kasa gane al-adar mutum idan ya kasance mai yawan shiga iri-iri.

Bayan ta gama shirin ta tsab,kai tsaye ɗakin shi ta nufa,a hankali ta buɗe kofar,ganin shi kwance yasa ta ƙarasa hawa tayi kan gadon,naniƙe shi tayi,shi kuwa bai sani ba yayi nisa yakai ziyara golden pen😃

Ita barcin ne ya ɗauke ta.🚶‍♀️nidai nayi nan asha barci lafiya.

~~~~~~~~~~~~~~

"Baki san waye mutumin nan ba,bashi da mutunci   kar mu koma mu bani mu lalace dan mugu ne."

Cikin kukan mai sauti Haulat ta kalli momyn nata ta ce,"Haba momy gaskiya mu koma kina gani momy ya daina so ba,na shiga ukku momy ya zanyi."

"Ai tun farko shi ya kamata ayiwa asirin ba ita ba,da shi aka mawa ya isa ya daina sonki bai isa,amma me kika buɗe baki kika ce min,ke baki son a mishi asiri kin fi son irin son da yake mi ki,to ai gashi kin ga ni irin son da yake miki dai ko yanzu kin ganshi."

"Har da it..

"Harda ita ko,ke banza ce har yau baki gane avubuwa da dama an gaya miki namiji irin macce ce."

A sanyaye ta ce,"Momy yana so na ni ce nai bishi abinda yaji haushi."

"Koma meye da anyi asirin bazai ji haushin ki ba duk abinda kika mishi saida ya baki hakuri."

"Momy to muje dan allah mu je yanzun nan."
~~~~~~~~~~~~~~

"Tashi to mu tafi."

Cikin gaggawa suka tashi ko shiri basu yiba mayafi kawai suka ɗauka,a harabar gidan suka haɗu da sakina ta dawo daga makaranta ko kallon banza ba su yi mata ba.

Ita kuwa tana kallon yanayin su tasan ba  hanyar allah zasu bi ba,aran tai musu addu'ar gafara da shiriya ta wuce avin ta.

~~~~~~~~~~~~~

Sama-sama ya fara fuɗe idon ƙamshi ya fara ziyarta hancin shi,na hanzari ya buɗe su dan tabbatar da abin da yaji,a hankali zuciyarshi ta fara bugawa da ɗan ƙarfi,lumshe idanuwa yake yi,kallon hannuwanta yayi waɗan da gaba ɗayan su suna rungume a jikin shi,kafafuwan ta duk suna kan cinyar shi,fuskarta kuwa tana ƙirjin shi kasan cewar yafi ta tsawo.

A hankali yasa zame hannun shi da ga jikin ta ya tallafo fuskarta idanuwa ya zuba mata,numfashin ta yana dokan fuskar shi,a ran ya ce,"kamar mu kasance a haka,"

Ko kaɗan baya gajiya da kallon ta,wani irin yanayi ya shiga wanda bai san irin shi,bai kuma taɓa shiga ba,saida ya ƙarewa halitta fuskarta gaba ɗaya kallon,ɗan ƙaramin bakin ta shi yafi ɗaukar hankalin shi,gai gashin idanuwanta,tsarin fuskar ya mishi kyau,hannu ya kai kan lips ɗin,da sauri ta buɗe ido,sai cikin nashi kallon ƙuda suka fara yiwa juna,cikin muryar da batai yi tunanin zai ji abinda zata faɗa ba ta ce,"Kai ma zaka rama ne."

Bai ji sautin muryarta ba amma motsin bakin ta ya gani,murmusawa kai yayi.

"Yaushe ka tashi?

"Ɗazun."

Shiru tayi sanan ta ce,"Kai baku ƙarya ba."

Janye jikin ta tayi ,wani irin abu ya zake shi a heart ɗin shi,ko kaɗan bai ji daɗin janye jikin ta ɗin da tayi ba,lumshe ido yayi yana jin wani iri a ran shi.

Hannuwan shi ta yanyo,"Ka tashi rana tayi."

Wani irin  yaji kallon hannu yayi sanan ya kalle ta shagwaɓe fuska tayi haɗe da rausaya kai alamar ya tashi.

Kai tsaye zuciyarshi ta amsa umarnin ta,tashi yayi ya banɗaki ya nufa,ita kuma ta fita.
~~~~~~~~~~~~~

Ƙarfe goma sha ɗaya da rabi agogon  bangon dake manne a jikin bangon fallon ya nuna.

Gurin abincin ta nufa ya ɗan rage zafi amma bai yi sanyi ba zasu ci a haka.

Bayan ya fito daga bayin saida ya zuba kasaita gurin shiri,cikin ƙananan kaya ya shirya sun mishi kyau ainun navy blue rigar sai baƙin wando,saida ya gyara fuskar shi da gashin shi sanan ya fashe jikin shi da turare,sanan ya fito.

Tun daga saman benan ya hangota tsintar kan shi da yin murmushi yayi wanda bai san dalilin yin shi ba,kamar ance ɗago kai ta ɗago suka haɗa ido murmushi suka sakar wa juna,wanda ya fito ne daga ƙasan zuciya.

Zama yayi,ta fara zuba mishi waina ta fara zuba mishi sai lipton da kwai,ita ma shi ta zuba,ba wanda yace ba wani ƙalla saida idan sun haɗa ido su sakar wa juna murmushi.

Dukkan su suka tsince zuciyoyin su cikin natsuwa da jin daɗi da farin ciki da walwala,ita ta fara gaba ci yana jin ta tsaya shi ma ya tsaya kallon shi tayi wai murmushi,"Nima na ƙoshi."

"Ka ci dai ka ga ni ko ban ci ba,ina da qiba ta,amma kai kuwa idan baka ci ba sai yadda...

"Kin fi ni qiba ne?

"Kam wa zai haɗa ma."

Kauda zancen yayi ya kawo wani ta hanyar faɗin,"Gobe ne fa!

"Wai zuwa honeymoon ɗin mu."

"Kin shirya ne?

"ƙwari kuwa ,kai baka shirya ba ne?

"Hmm na shirya zaida ke nake tunanin anya kuwa."

"Na shirya ma komai da komai ka daina shakka."

"Komai da komai fa kika ce."

"Eh komai da komai."

"To amma kin koya kuwa."

"Me?

"Haƙƙin miji!

"Ka fasa koya min ne?

Murmushi yayi mai ƙunshe da abubuwa da yawan gaske.

Bai kai ga bata amsa ba ta ce,"Dady ya ce,wai da wuri zamu tafi goben yau sai muje muyi musu sallama,amma fa ina ɗan jin tsoro kar wani abu ya faru mara kyau a can,ko da yake tsoran me zan ji ina tare da mijina ɗan uwa na,nasan ba zaka bar wani abu ya cutar da ni ba."

Ta ƙare maganar tana kallon shi,yanayin shi kuma ya ɗan canza wanda zai iya alaƙanta wa da maganar da ta mishi.

"Wai zanga fararan muta ne,ai nima kuwa irin sabulon su zaka sai min nayi fari irin na su."

Dariya ya ɗan yi,"Ai ke zama abin kallo ce a gurin su."

Saida ta ɗan zare ido,"Wai saboda muni ko.?

Wanan karan saida sautin muryar shi ya  fito,ita kuwa ya mutsa fuska tayi tana kallon shi.

🚶‍♀️🚶‍♀️Ina zan iya muku dan firar ku bata ƙarewa.

~~~~~~~~~~~~~

Banka gudu Momy ke yi,har suka isa garin katsina ba wanda ya ce da wani komai,wanan ƙaran tsoron Haulat ya ragu.

Kamar yadda suka yi farkon zuwa yanzu hakan suka yi,saidai shi yanayin shi ya ƙara canzawa ya ƙara muna,kuma bai yi dariya ba kamar wancen zuwan sai uban ihun ta yake yi.

Ya daɗe yana amvaton shi yana ihiuu yana yarfe-yarfe  dukan su sun tsorata ainun ganin sun daɗe bai ce musu uffam ba gashi sun daɗe da zuwa.

Cikin mummana kuma kaussar muryar ya ce,"Hatsabibiyar yarinya ce,da ƙyar ƙaranjuug yasha ya kasa kusantar inda ta ke,ba nazara ba nazaraaa,ba zai iya zuwa inda take bahhh."

Wata razanannar ihuu yayi wacce dan tsoro har hantar cikin su saida ta juya,hatta kasar gurin da bukkar zai da ta girgisa.

Bayan wasu ƴan mintina sanan komai ya lafa shi ma ya tsagaita.
~~~~~~~~~~~~~

Cikin rawar murya momy ta ce,"Yaanzuu  shiii yaaron f."

Ai kamar ta ƙara tunzura shi ya ƙara buga wani sabon ihhu na tsawon sakonni sanan ya murtuke fuska,ƴan karance karancen shi da kalle-kallen shi yayi sanan ya bushe da muguwar dariya  saida yayi mai isar shi sanan ya ce,"Akwai nazarraa Nazara,me kuke da bukatar ai mishi?

Har momy ta buɗe baki zata yi magana haulat ta katse ta,"Ya so ni  kamar ya mutu sanan sai abinda na ce zai yi magana ta kaɗai zai ji sai  yadda nayi da shi."

Dariya ya bushe da ita ,sanan kuma ya murtuke fuskar,"Wanan ƙaramin aiki ne amma akwai sharaɗi bai tsauri...

Kallon Momy Haulat tayi a tsorace sai zare ido take yi.

"Hhhhh maganar tsoro babu ita tunda kuka kawo kan ku ƙaranjuuug ya amshi saƙon ku dole ku yarda da sharaɗin."

Tsuull! fitsari ya zubowa Haulat tsabar tsoro da farga ba,kallon momyn take yi wacce ba alamar tsoro da fargaba ko kaɗan a idon ta.

Kallon shi momy tayi ta ce,"Kasan ni indai akwai nazara to ina amincewa  da ko wani irin sharaɗi."

Dariya ya ƙara fashe wa da ita,wanan karan saida na tsorata da gudu na fito ina haki ina naiman taimako duk na ruɗe na kasa gane hanyar da zan bi,kawai sai ga Aunty beelat janyo hannu na tayi muka fara gudu,kwatsam sai ga ommu deedat da motorta tayi fakin a gaban mu,ai tsorum muka taɗa,ina shiga ng bloody a ciki janyo ni jikinta tayi ta fara jijjiga ni tana ban baki nayi shiru cikin raɗa ta ce min,"Bloody na  ki kwantar da hankalin ki kinji ga shadowwn ki tana jiran ki tun dazun."

Cikin hanzari na ɗago na kalle ta😅😅🚶‍♀️🚶‍♀️🚶‍♀️🚶‍♀️🚶‍♀️kunga dole na kama ɗariqa shadow tayi kira💃💃.

.

Ina mugun -mugun son ku har raina,ba abinda zan ce saidai allah ya barni da ƙaunar ku a raina❤.

[12/23, 2:24 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт Bу Gяσυρ O F Hурє Hαυѕα Nσνєℓѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚

[12/23, 2:25 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*
*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*
Page 18
......................................

_*Manzon Allaah(ﷺ)* *ya ce;{BABU WANI AIKI DA AKE 'DORAWA AKAN MIZANI YA SANYA MIZANI YAYI NAUYI KAMAR KYAWAWAN HALAYE DA 'DABI'U, KUMA LALLAI MAI KYAWUN HALI YANA SAMUN MATSAYIN MAI RAYA DARE DA IBADA, DA RANA YA RAYA DA AZUMI.}*_

```[Sahihut Tirmizy;2003,Sahihul Jaami'i;1620]```

_Shi kyawun hali yana dauke da dumbin alkhairi wanda mai yi zai amfana da shi Duniya da Lahira. Allaahu a'alam._

```Allah ta'ala yasa mudace```

_*سبحانك اللهم وبحمدك, أشهد أن لا إله إلا أنت، أستغفرك وأتوب إليك.*_

___________________________________

Wata mahaukaciyar dariya yayi mai haɗe da ihuu sanan ya murtuke fuska ya kalle Momy ya ce,"Kin yi nisa! asiri zai kama shi amma kuma duk sanda ya ƙarye kan ki zai dawo zaki haukace ne."

Ya kara bushewa da dariya sanan ya ɗaura da faɗin,"Kuma asirin ba mai nisan zango ba ne,duk sanda ya tambaye kan shi akan naiman dalilin da yasa yake bin umarnin ki kamar raƙomi da akala to ranar zai ƙarye."

Haulat dan tsabar tsoron jin abinda ya faɗa saida fitsarin da yake zulluwa ya fito gaba ɗaya,zuciyarta ta shiga buguwa da karfin gaske zufa duk ta wanke ilahirin jikin ta,kallon Momy tayi wacce ita kan ta tana cikin tsoro da tashin hankali.

Murya na rawa Momy ta ce,"Mun amince!!

Ya kwarara uban ihuuu yana kallon ta yana tasar baki,"Duk sanda yaji muryarki asirin zai fara aiki."

Ita kuwa Haulat kamar gunki haka ta koma,saida ya ƙara kwanciya da su sanan suka tafi.

~~~~~~~~~~~~~
~~~~~~~~~~~~~

Bayan sun kama firar suka shiya gidan su hajia suka nufa a can suka tadda dukkan su momy da dady da farrah,fira suka yi sosai dan Naufal ma ya manta da wata haulat ni kuwa na ce daman ba son  nata yake yi ba.

Har bayan maqrib sunan nan zaune a falo Dady wacce Sabreen ke zaune akan cinyar shi ya zaunar da ita kasa  gaban shi,kiran Naufal yayi ya zo kusa da ita ya zauna.

Cikin dattijowar murya ya ce,"Naufal!

Naufal wanda ke zaune a kasa gaban Dadyn kusa da matar shi  ɗukar da kan shi yayi ya ce,"Na'am Dady."

"Naufal ba zan iya misalta maka irin farincikin da na ke ciki ba,duk da nasan  ka ji magana ta kuma ka bi umarni na ka amshe matarka da hannu biyyiyu,amma hakan ba zai hana na ƙara tunatar da kai akan amanar da ka ɗauka ba,Naufal Sabreen amana ce na danƙama, ka sani Naufal ko wani irin yanayi zaka tsinci kan ka a rayuwar nan idan har ka cutar da sabreen ban yafe ma ba ko bayan ba raina bani ba ka."

Zuciyar Naufal ta fara bugawa da mugun ƙarfin wanda faruwar hakan yai sillar haifar mishi da mutuwar jiki,bai yi tunanin zai iya magana va yai karan banin buɗe bakin shi,"Dady na ma alkawari ba zan cutar da ita ba  komai rintse komai wuya zan rayuwa da ita zan kyautata mata."

"Yawwa Naufal Allah yai maka albarka."

Jin amsar  da Dadyn ya bashi ne ya tabbatar mishi da ya faɗi abinda ke ran shi  kenan.

"Naufal ka ga Sabreen ba sabawa da zuwa irin ƙasacen nan tayi ba ,dan haka sai ka kula da ita sosai,Sabreen matar ka ce nasan ka fi ni sanan yadda zaka kula da ita,tsananin son da na ke mata ne yake sawa naga kamar ba wanda zai iya kula da ita,Naufal karka cutar da sabreen dan ni zaka cutar ,idan ka kyautata mata ka kyautata min,ina son sabreen fiye da tunanin ka jinin jiki na ce,ka kula da ita k....

"Ya isa haka kamar yadda kake son ta shi ma yana son ta matar shi ce,"
Cewar hajia ,kallon Naufal ɗin tayi fuskar ta ɗauke da murmushi wanda shi har lokacin kan shi yana ƙasa,"Naufal ba abinda zan ce ma sai abu ɗaya ni ma na baka amanar Sabreen shi ne kawai abinda zan faɗa ma,matarka ce  ka fi mu sanin yadda zaka kula da ita,allah ya kaiku lafiya ya dawo da ku lafiya."

Dukkan su suka amsa da amin,sanan momy ta kalle shi ta ce," nima abu ɗayan zan faɗa ma ka riƙe amanar Sabreen Naufal allah ya kaiku lafiya."

Nan mu suka amsa da amin,sanan suka ɗan taɓa firar duk akan tafiyar su ɗin labarin garin su

ke yi,da gidan ya zasu sauka.

Duk abinda ake yi jikin Naufal a mace,zuciyar shi ta cunkushe  wanda hakan ya hana shi yin tunanin  komai.

Sai ƙarfe takwas suka tashi zasu koma gidan su,Sabreen tayi kuka kamar ranar auran ta tunda goben tun biyar zasu bar gida ba haɗuwa zasu kuma yi ba,da ƙyar aka janye jikin ta gurin hajia.

"Kiyi hakuri ki daina kukan nan plss."

Kallon shi tayi cikin kukan ta ce,"Ji na ke kamar na tafi kenan bazan dawo ba."

Saida gaban shi ya faɗi taka burkin motor yayi da sauri ya juyo
ya kalle ta,janyo ta jikin shi yayi ,"Hava ƴar aljanna yaushe kika zama haka ne ban san ki da rauni ba fah,taya zaki ce haka zamu dawo cikin ƙushin lafiya."

"Ba zamu daɗe ba ne."

"Eh ai sai yadda kika ce,idan kina so a fasa zuwan ma za'a fasa."

"A'a ina son zuwa."

"Kina son cin amarci kenan."

Murmushi tayi ta ɗaga mishi kai alamar eh.

"To ai baki iya komai ba."

"To ba ka ce zaka koyamin ba."

Ɗago kanta yayi kasancewar akwai haske a motor yasa ya ga fuskarta da kyau lipa ɗin ta ya fara kallo,haɗa bakin shi da nata yayi sun ɗau lokaci suna abu ɗaya kafin ya fara fita haiyacin shi,ganin abin yafi ƙarfin ta yasa ta fara koƙarin zame jikin ta,amma ta kasa.

"Ya Naufal!

Yaya yayi nisa nishi ya fara yi,janye jikin ta tayi da ƙarfi ita ma haƙin ta fara yi.

Sun daɗe a haka suna nishi wanda kowa ke jin na kowa,can ya ja motor cikin ƙanƙanin lokaci ya isa gidan.

Tunda yayi fakin ɗin ya tsaya yaƙi saukowa,ganin hakan yasa ta ce,"ka zauko."

Tana gama faɗa ta sauko gaba tayi bata tsaya jiran shi ba.

"ke ce kaddara ta Sabreen dole na karɓe ki ba yadda na iya,nasan wata  rana zan son ki."

Ya daɗe yana tunanin ya amincewa zuciyar shi yin rayuwa da ita cikin kulawa ga alƙawarin iyayen shi baya son ya saɓa musu,kuma ko da ba alƙawari Sabreen abin tausayi ce marainiya ta uwa da uba dole a tausaya mata,ya yaken wa zuciyar zai koyan son ta idan sun je turkey .

Ita kuwa kai tsaye ɗakin shi ta nufa saida yi ɗan gyare-gyare sanan ta shiga bayi tayi wanka ta tauro alwala,shafa'i da wutiri ta yi.

Tana cikin yi ya shigo murmushi yayi dan san tayi sallar isha'i zama yayi bakin gadon yana kallon yadda take sallar komai daidai cikin natsuwa,bayan ta gama ta fara addu'o'i duk yana jinta saida ta yi komai sanan ta tashi da nufi ɗauke sallayar ganin shi yasa tayi murmushi.

"Ka shigo? na haɗa ma coffee?

"Eh lipton ki matsa lemon tsami."

"To wai kana jin daɗin shi ne."

"Eh!

"Nima zan haɗa na sha."

Vata tsaya jin avin da zai ce mata va ta bar ɗakin,saida ta shiga ɗakin ta sanan ta sauko kicin ɗin ,cup biyu ta haɗa duk ta saka lemon tsamin sanan ta nufi ɗakin.

Da sallama a bakinta,ta isa ɗakin,can ƙasa ya amsa mata gaban shi ta je ta ajiye mishi sanan ta ɗau na ta.

"Kin saka ma naki lemon tsamin ne?

"Eh baka ce akwai daɗi va."

"Magani ne fah kuma bai kama ta ki sha ba."

"maganin me? ko ma na meye tunda kai kasha nima zan iya sha,oh yanzu gobe iwar haka muna can garin ƴan gayu."

Kallon ta kawai ya ke yi yadda ta ke jero zance wani kan wani,murmushi kawai yake yi,kuma taƙi dainawa zai yi ta ke yi.

Can ta gaji lokacin ta sanye lipton miƙa tayi da sauri yai ƙasa da kai dan baya son yaji wani abu.

Cikin muryar jin barci ta ce,"Ni barci na ke ji kar na makara gobe."

Tashi tayi ta hau akan gadon yana kallon ta,ta rufe da bargo,murmushi kawai yake yi yana jin wani irin baƙon yanayi yana kai wa zuciyar shi ziyara.

Bai tsaya wani tunani ba ya kwanta nan da nan barci yai awan gaba da shi.

>>>><<<<

Kamar dai kullum yau ma hakan ita ta fara tashi da jin kiran sallar farko na asuba,bata tsaya tashin shi ba ta fita ɗakinta,ta nufa na zuwa ta fara haɗa ƴan abubuwan da zata naima Dady ya ce gidan akwai kayan sakawa amma saboda tsoro zu ɗau abinda zasu bukata,haka ta haɗa abubuwan ta a cikin akwati duk abinda tasan zata buƙata,tana gamawa ta shiga bayi tai alwala,da ta fito saida tayi nafila sanan ta wuce ɗakin shi tashin shi tayi dan lokacin an kira sallah,yana tashi ya shiga yai wanka ya ɗauro alwala,ko kafin ya fito ta fara gyara ɗakin,yana fitowa ya tafi masallaci ,ita kuwa ta gyara ɗakin tsab.

Yana dawowa Dady ya iso dan shi zai kai su tashar jirgin,tara da hajia su ka zo dan ta ƙara yi musu sallama basu wani ɓata lokaci ba suka ɗau hanyar ,saura minti hudu jirgin ya tashi,hajia da Sabreen kuwa sun sha kuka.
🛫🛬Wai sai ƙasar turkey.

~~~~~~~~~~~~~

"Ke dan allah ki kwantar da hankalin ki wahalar da muka yi ba zata tafi a vanza ba,kawai dai yanzu kiyi ta kokari ki samu wayar shi yana jin muryar ki aiki zai fara,idan ya so zai ki bishi ƙasar ma."

Ita kuwa Haulat ɗin wacce ta zuba uban tagumi a gaban Momyn tana hawaye da wayar a hannun ta.

Dafa ta momy tayi,"Ki kwantar da hankalin ki idan sun sauka ki ƙara kira ,karki manta ba duk abinda kika faɗa shikenan to meye da damuwa."

"Kina ganin zai ɗau wayar kuwa."

"Dolen shi ba,ai ki fara shirin zuwa ƙasar turkey private zaki hau ya kai ki yau ɗinnan komai dare."

"Taya Momy."
~~~~~~~~~~~~~

"Wai yaushe kika zama banza ban sa ni ba,kuna yin waya ya turo miki kuɗi ki bishi."

"Je ki fara shiri ma,kuma idan jin je karki rama ma ƴar iskar matar ta shi,ku ƙuntata mata dan uban ta duk ita ce ta bamu matsala."

Wani irin farin ciki ya mamaye Haulat da rawar jiki ta tashi ta fara shiriii.

~~~~~~~~~~~~~

Ƙasar turkey kyakyyawar kasa ce mai abubuwan birgewa,yanayin tsarin garin da yadda al-adar mutanan garin ya ke shi yafi komai birgewa.

Tunda suka zauko Sabreen ta fara zare ido tana kallo riƙe shi tayi gamm kamar wani zai ƙwace shi.

Wata tsadaddiyar motor da wani ɗan afirka a cikin ta yazo tarbar su,cikin harshen turanci ya gaida su cikin girmamawa,suna shiga motor ta lafe a jikin shi.

"Lafiya ko garin bai miki ba ne?

gaɗa kai tayi alamar a'a,taɓa jikin ta yayi,dan ya lura yanayinta ya canza da zuwan su.

Cikin nuna kulawa ya ce,"Baki da lafiya ne?

"A'a lafiya lau,yaya karka barni plss."

Saida gaban shi yai mummunan faɗuwa,"Sabreen ba zan barki ba ki kwantar da hankalin ki ,amana ce a guri na,taya zan bar ki na je ina? kin san ban isa na ce gida babu ke ba,ke fa ƴar uwata ce ,zan kasance da ke har abada." cikin sigar lallashi ta tausasawa yayi magnar.

Ɗago da kanta tayi wanda ta kwantar da shi akan ka faɗar shi,ta kalle shi yaƙe tayi.

A zahirin gaskiya tunda suka zauko dga jirgin faɗuwar gaba ya kamata jikin ta ya mutu,wani irin yanayi mara daɗi ya shiga zuciyarta.

Sun daɗe zuna tafiya a motor bata ɗago ba balle ta kalla yanayin garin shi ma haka,wani irin abu mara daɗi ya ke ji a ranshi.

Wani hamshaƙin gida dan madaidaici direban ya nufa yana isa mai gadin wanda shi ma ɗan africa ne ya buɗe musu hamshaƙin get ɗin,karamin gida ne amm huɗuwar ta yi yawa,wanda idan kwatantawa zai ya ɗauke mu fiye da shafi biyar.

Yana tsayar da motorn ya fito da sauri ya buɗe musu,hannunwan ta ya riƙo su ka fito cikin su ba
~~~~~~~~~~~~~

wanda ya tsaya kallon gidan sun bi bayan mutumin da ya kawo ne ,sun ɗanyi tafiya kafin suka isa cikin lafiyayyan falon suna isa ya tsaya,cikin harshen yar musu barka da zuwa ya juya.

Zaunar da ita yayi a kan kujerar da ke fallon kallon falon ya tsaya yi ,ya mishi kyau ainun,ita ma kallon falon tayi tai gutun murmushi ta ce,"Gidan yayi kyau sosai."

Kallon ta yayi ya sakar mata murmushi,"Nima yamin kyau,tashi mu je ɗaki muyi wanka muyi sallah sai mu fito mu kewa ya mu ƙara ganin gidan ko."

"Eh!

Hannunta ya riko suka nufi wata hanya wacce su ke tunanin ita zata sada su da ɗakin kwana,hakan kuwa ɗaku na ukku ne a jere,fuɗe wanda su ke kusa yayi suka shiga,ai nan suka yada ido dan haɗuwar ɗakin har yafi falon kyau gashi babba harda tavi da kujeru a ɗakin sai gadon ne ɗan ƙarami.

Basu wani tsaya ɓata lokaci ba,gurin ajiyar kaya ya nufa yana duvawa ya gane ɗakin ta ne,dan kayan mata ne.

"Ki shiga bayi kiyi wanka." ya faɗa haɗe da nuna mata bayin ,ba musu ta shiga,tana shiga ya fita ɗayan ɗakin ya shiga  yana dubawa kowa yaga ɗakin shi  ne,bayi ya shiga shi ba wani tsayawa kallon haɗuwar bayin yayi ba,dan ba yau ba ne farkon ganin gida irin shi ba.

ita kuwa ta zuba ƙauyanci kamar wacce ta fito a zaria ba abuja ba.

Da ta fito baya ɗakin sakin jikin ta tayi ta saka kaya duguwar riga cikin wacce ta tawo da ita,sallah ta fara yi.

Shi ma hakan sallah ya fara yi,tun yana sallah yake jin ringin ɗin wayar shi har ya idar ana kira,kafin ya idar anyi jira goma sha bakwai,yana idarwa ya nufi gurin wayar sabowar number ya gani,gaban shi yai mummunan faɗuwa    yana gurin har aka ƙara kira amma bai ɗauka ba,number ya zubawa ido number 9j ne bawai yasan mai number ba ne,yadda gaban shi ke mugun faɗuwa ne yasa ya kasa ɗauka,wani kiran ya ƙara shigowa,yai jan hali ya ɗau wayar da kalmar "Hello" a bakin shi..

.

😘love u guys irin over ɗin nan fah.
Sir Dboy
[12/23, 2:26 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ 𝗣σѕт 𝗕у 𝗚яσυρ 𝗢 𝗙 𝗛уρє 𝗛αυѕα 𝗡σνєℓѕ 𝗕σσк 𝗪нαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/23, 2:27 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA*🌹

*By*
*fatima* *Batula*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

Page 19
.................................................................

_*Manzon Allaah(ﷺ)* *ya ce;{MUTANE SUNA DA HALIN MUTUM BIYU NE; NA KIRKI TSARE DOKA MAI 'KIMA A WAJEN ALLAAH, KO BANZA MARA RABO DA 'KIMA A WAJENSA.}*_

```[Sahihul Jaami'i;7867]```
~~
_Wannan hadisin yana nuna mana cewa shi dan Adam a halinsa dayan abu biyu ne; ko dai ya zama na kirki mai tsoron Allaah ko kuma ya zama na banza mara qima da rabo a wajen Allaah. Allaah Ya sanya mu daga cikin masu halin kirki. Allaahu a'alam._

```Allah ta'ala yasa mudace```

---

A tare su ka ce, "Me ya faru da ita?

Farrah ta ruɗe sama kawai ta ke nuna musu,cikin inda-inda ta ce,"Sabreen bata da lafiy...

Tun kafin ta rufe baki sun bar gurin saman su ka hau da sauri,suna zuwa su kai kanta lokacin zazzaɓin ya tsanan ta.

"Ƴar aljanna!
Gaba ɗaya hajia ta ruɗe,momy ce tai ƙarfin hali ta ɗauke ta,da gudu su ka fita da ita dukkan su,su na zuwa su ka shiga motor direba ya ja su.

Su na isa asibitin doc zain ya tarbe su,alluran barci yai mata,duk suna tsaye a gurin bayan ya gama ƴan abubuwan shi,sanan ya juyo ya kalle su.

"Momy Hajia akwai damuwa a tare da ita,ban son shiga lamarin da ba nawa ba,ba ita ba ce matar Naufal? kuma kamar ita yai ma laifi?amma ta hakura ta yafe mishi ba lallai sai ya zauna da ita ba idan ba ku san haka,amma yana buƙatar ku yafe mishi yana cikin wani hali ƙiris zuciyar shi ke jira ta fashe,ɗazun bayan fitar ku ya kalle Farrah,ya farka saida yayi zuma sama da ashirin da aman jini da ƙyar mu ka samu yayi barci."

Tunda ya fara magana jikin su yayi sanyi,hatta hajia saida tayi kwalla farrah kuwa kuka me ƙarfi ne ya kama ta,Allah sarki momy kukan zuci kawai ta ke yi.

Shi kuwa doc ta zain ganin kalaman shi sun shiga jikin sui yasa ya fita daga ɗakin.

~~~~~~~~~~~~~

Haulat kuwa a ƙasa ta taka har unguwar su,kamar wata mahaukaciya tana tafiya tana surutu ga hawaye,tana isa gidan su ta fara jin ihuuu yana tashi,gigicewa tayi jin muryar me ihuun da gudu ta faɗa cikin gidan.

"Haulat nasara a jini na ta ke,ko yanzu na ci nasara,kin gani kin gani,ina ita yarinyar?

Momy ke wanan maganar tana rawa duk ta raba jikin ta da kaya,alamun hauka ƙarara.

Sakina ita da Salma sai kuka su ke yi,sun kasa riƙe ta gashi sai ɓarna ta ke duk ta fasa glass ta yanke hannuwan ta.

Kamar gunki haka Haulat ta koma hawayen da na sani sun wanke fuskarta,"Momy mun cuci kan mu,ba muyi nasara ba ,momy"

Ita kuwa momy sai hauka ta ke yi tana rawa tana ihuu sun yi nasara,da ƙyar salma da sakina su riƙe ta ,a ɗaki su ku kulle ta.

Sakina ta fashe da kuka,"Sanda na ke gaya mu ku,baku saurare ni ba,tun yanzun kenan a duniya,ga haƙƙin mutanan da ke kanku wanda allah ba zai iya yafe mu ku shi ba,yanzu su waye da nasara? kun mata duk nisan jifa ƙasa zai dawo ai...

Luuu Haulat ta faɗi kasa zumamma wanda zuman ne ya katse sakina maganar da ta ke yi,a ruɗe su ka je gurin ta su na ihuuu.

~~~~~~~~~~~~~

A hankali ta fara buɗe nauyayan idanuwan ta,sama-sama ta fara ganin mutanan da ke ɗakin.

"Dady Yaya"dan Allah dan annabi hajia."

"Ya isa kwanta kin ji ki kwantar da hankalin ki."

Zaune ta tashi tana hawaye,"A'a Dady dan allah yaya zai mutu ba wllh bashi da laifi  dan ..

"Shikenan!

Dukkan su sunji daɗi da har su ka kasa ɓoyewa,ko wanne su fuska ɗauke da annuri hatta hajia.

Sabreen kuwa rungume Dady tayi tana kukan jin daɗi,"Na gode dady muje mu gan shi."

Daman a lokacin doc zain yana nan yai musu jagora har ɗakin,hatta dady sai da ya tausaya mishi ganin halin da ya ke ciki,Dady da momy ne kawai ba su yi kuka ba,momy na zuciya tayi.

Kusa da shi Sabreen ta matsa tana kuka mai ratsa zuciya,kan shi ta taɓa a hankali ta ce,"Yaya!

Kamar daga zama ya fara jin muryar ta,lokaci ɗaya yaji zuciyar shi wani haske da daɗi yana kai mata ziyara,koƙari ya fara yi ya buɗe idanuwan shi,dan ya kan ta.

Sama-Sama ya fara ganin dushi-dushi,ganin hakan yasa Sabreen ta yin wani yalwataccen murmushi.

a kan fuskarta idanuwan shi su ka zauka,kallon-kallon su kai wa juna,wani irin abu ke ziyarar zuciyar shi,duk sai yaji ya manta da komai.

Wasu hawayen ne su ka fito mata,"Ya jikin?

Hannu ya miƙa mata ta riƙe alamar ta zauna kusa da shi yai mata,zaman tayi kusa da shi,da ido yai mata alama da ta goge hawayen ta.

Su kuwa tsayawa kallon ikon allah su ka yi,abin ya basu mamaki ganin wata ɓoyayyar soyayya a idanuwan  su,momy kuwa ita da farrah sun fi kowa jin daɗi ,Dady kuwa mamaki ne ya kama shi,"To daman yana mata irin wanan son kuma zai aikata abinda yayi.",abinda zuciyar shi ke gaya mishi kenan.

Su kuwa sun manta da akwai wasu muta ne a ɗakin kallon juna kawai su ke,su na fira da ido.

Farrah ce ta ƙarasa gurin basu san da zuwan ta ba,murmushi tayi ta ce,"Yaya ya jikin?

Kallon ta yayi ya ɗaga mata kai,daidai da haɗuwar idon shi da momy,da sauri yai ƙasa da kai,zuma ya fara yi,a ruɗe su ka ƙaraso gurin shi harda Dady duk sun ruɗe,ita kuwa sabreen kuka ta fara yi.

Aman jini ya fara yi nan da nan numfashin shi ya fara koƙarin fita,Ihuu su ka yi gaba ɗayan su banda Dady,jin ihuun yasa doc zain ya shigo a ruɗe ya kore su,da ƙyar dady ya ja Sabreen dan ƙin fita tayi.

nan da nan doc zain ya fara koƙarin taimakon rayuwar shi.

su kuwa su na waje Sabreen sai rusa kuka ta ke yi an kasa samun wanda zai bata hakuri,dan

kuwa kukan ya ke yi.

Hankalin momy ya tashi ainun,tasan ganin ta ɗin ta yayi ne,"Taya anya kuwa idan har da gani da zuciyar shi zata buga kenan abinda ya aikata ne wanda na ganshi ya tuno." sai hawaye,"Hm koma mene ba da san ran ka ba ne Naufal mutumin da baibi mata a india ba sai a nan."duk a zuciyarta taita maganganu tana hawaye.

Hajia kuwa faɗi ta ke,"Allah sarki Naufal mun yafe ma,kadɗara ce."

Shi kan shi Dady jikin shi duk ya mutu.

ko doc zain ya fito bayan ya dau lokaci mai tsawa, yana fitowa su ki kan shi.

"Na shaida mu kar ya farka da wani tunani wanda zai fada mishi rai ko ya ga wani avu, a gaskiya yanzun idan ya farka da irin haka to gaskiya va zamu iya komai va, yanzu kawai ku tafi gida dan va zaku samu damar ganin shi ba."

Gaba dayan su jikin su ya mutu sun tausaya mishi ainun, savreen kuwa sai rusa kuka ta ke yi, Dady ne yai karfin halin jan su,haka su ka koma gida ko wanne jiki a mace hatta dadyn ma.

Ba wanda ya saurari wani kowa da kan shi yayi, da kyar sabreen ta samu tayi sallar isha'i ta kwanta bayan ta kama kwaranyo mishi addu'a, ba ta yi wani barci va ,tana jin kiran sallah ta tashi tayi...

Abubuwa sun dan min yawa kuyi hakuri da wanan

.
[12/23, 2:27 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ 🅿σѕт 🅱у 🅶яσυρ 🅾 🅵 🅷уρє 🅷αυѕα 🅽σνєℓѕ 🅱σσк 🆆нαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚
[12/23, 2:29 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA* 🌹

*By*
*Fatima* *Batulah*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

Page 20

......................................
Addu'a ga Wanda Ya ce Maka: Allah Ya yi Maka Albarka:

وَفِيكَ بَارَكَ اللهُ.

wa fika barakallah.

Kai ma Allah ya yi maka albarka.

......................................
Zaune ta ke akan sallaya tana kuka tana cewa,"Allah na tuba! ka yafe min duk laifi na ne da ban shiga rayuwar shi ba ,da hakan bata faru ba,nayi kuskure."

"Ba wani kuskuren da kika yi Sabreen ,ke ce alkairi a rayuwar shi,Yaya Naufal  yana son ki Sabreen."

Kallon Farrah tayi da jajayen idanuwanta ta ce,"A'a Farrah baya so na malama Haulat ya ke so ba ni ba..

Tass ta kwashe dukkan labarin abinda ya faru tsanin ta da malama haulat har dalillin da yasa ta ce zata aure shi bayan bata son shi baya son ta.

Saida Farrah ta sauke raguwar ajiyar zuciya sanan ta ce,"Sai yanzu na fahimce wani abu,amma kuma zargi ne kuma ba komai,amma zan yi bincike akai  sosai."

"Me kike zargi?

"Ba komai zan gaya miki komai idan na tabbatar da bincike na,Sabreen abinda kike yi daidai ne,kuma yaya na son ki."

"Baya so na Farrah."

"Hm yana son ki,ke ma kina son shi."

zare ido tayi,"Me? rufamin asiri yaya ba zai so ni ba,nima bana son shi."

Ganin ba zata iya fahimtar da ita ba yasa ta ce,"Yanzu ki tashi mu je gurin shi."

"Ni ai tun dazun na shirya ,ke na ke jira."

Murmushi kawai Farrah tayi,tana mamakin sabreen da bata gane abubuwa sosai.

Tun da safe momy ta tashi daman ba wani barcin kirki tayi ba,tunanin ɗan ta ya hana ta yin barci,ba ita kaɗai ba hatta Dady saida yayi  tunani.

Tun da safe momy ta,tashi ta haɗa musu abinci har wanda zasu kai asibiti,saida ta gama haɗa komai ta shirya,tana cikin shirya abinvi hajia ta shigo kicin ɗin a tare su ka gama.

Suna zaune a falon su sabreen su ka zauko kasa,cikin girmamawa su ka gaida su.

Momy ta kalle Sabreen so  da kaunar ta yana ƙara shiga ran ta,murmushi tayi  mata alama da ta zo gurin ta tai mata,tashi tayi daga kusa da farrah ta dawo inda momyn ta ke.

"Sabreen ya jikin?

"Da sauƙi momy."

"Masha allah ki kwantar da hankalin ki sabreen karki sawa kan ki damuwa kin ji,yau idan mun je asibitin ke kadai zaki shiga,dan na ga alama ganin mu ke ɗaga mishi hankali."

Kai ta ɗaga ta ce,"To momy."

"Yawwa allah yai miki albarka."

"Amin."

"Momy ni fa ce,"cewar farrah haɗe da turo baki.

Murmushi momy tayi ta ce,"Allah yai mu ku albarka baki ɗayan ku."

A tare su ka amsa da ,"Amin."

Saida Dady ya fito sanan suka ci abinci bayan sun gaisa,Sabreen na jikin shi yana bata a baki kamar wata yarinya,saida ya tabbatar da ci sosai sanan ya gyale ta.

Suna gama ci su ka tashi,motor biyu su ka yi,Dady da su Sabreen da farrah a motor shi,Momy ita da Hajia.

Suna isa asibitin su ka naimi doc zain,bayan sun gaisa ya kalle Dady ya ce mishi,"Tun jiya bai farka ba,ina jin tsoron ya farka ne da wani ɓacen rai a zuciyar shi gaskiya zaku iya..

Katse shi Dady yayi da faɗin,"Dan Allah doc kai mishi allurar da zata tashi shi ,matar shi kaɗai zai gani kuma nasan ganin ta zai kwantar mishi da hankali kamar yadda ita ma ganin shi zai samar mata natsuwa."

"Okk ba matsala,amma plss karki mishi maganar da zata ɗaga mishi hankali,"ya kare maganar yana kallon Sabreen.

Ɗaga mishi kai kawai tayi alamar eh zata yi yadda ya faɗa.

A tare su ka fita daga office ɗin na shi,har sun kusa ƙarasawa ya juyo ya kalle su ya ce,"Ku tsaya daga nan plss."

Ba abinda su ka ce mishi illa bin umarnin shi da su ka yi kawai,ita kuwa binshi tayi da sauri yana buɗe kofar ta shiga ita ma.

Saida yai mishi wata allura,kamar a jikin ta za'a yi taji,yana kama allurar ya fita ya barta ita kaɗai.

Akan gadon ta zauna har jikin su ya na taɓa juna,hannuwan ta ɗaura a saman kan shi,kwantaccen baƙin gashin shi mai laushi ta fara shafawa,cikin wata irin murya ta ce,"Miji na!

Kai tsaye muryarta ta kai zuciyar shi,wanda hakan ya harfar mishi da jin daɗi wanda saƙon zuciyar ya isa fuskar shi.

Murmushi tayi ganin murmushi a fuskar shi,ta ƙara faɗin,"Mijina! ka buɗe idon ka,Sabreen ce matar ka!

Murmushin fuskar shi ya ƙara faɗaɗa idanuwan shi su ka fara koƙarin buɗewa bakin shi ya fara motsi.

Dushi-dushi ya fara buɗe nauyayan idanuwan shi wanda har yanzun bakin shi yana motsi.

"Sabreen! ya faɗa tare da sauke idanuwan shi a kan ta,ba wai taji sautin muryar ba ne,ta ga yadda bakin shi ya nuna alamar ita ya kira.

Kallon juna su ka fara yi wani irin baƙon yanayi yana ziyarta ko wannen su ,sun daɗe a haka kafin ta yanke shirun da faɗin,"Ka ji sauki dan allah mu koma gida ga ji,gidan ba daɗi kasan na xaba da kai,ko kana son nayi ta kuka ne?

Murmushi yayi mai ƙyayatarwa muryar ta na mishi daɗi musaman yadda idam tana magana cikin sauri bata tsayawa sauke numfashi.

Lumshe ido kawai yake yi yana kallon ta tana magana lips ɗin ya zubawa ido yana ganin yadda ta ke sarrafa su,yakan rasa dalilin da yasa idan yana tare da ita yakan manta komai da kowa.

"Ka ji Sauƙi ko! mu tafi gida,ba zan ɗinga damun ka ba."

Murmushi kawai yake yi.

Turo baki tayi ta ce,"Ba xaka yi magana ba ne,zan tafi fah."

Da sauri ya riƙo hannun ta,saida wani abu ya tsikari zuciyarshi a hankali dan baiyi tunanin zata ji ba ya ce,"Pls stay with me,mai xan ce?

Dariya ta fashe da ita,a ranta tana faɗin,"Ba xaka canza ba halitta ce wanan iyayin na ka.

mutum ba lafiya ji yadda ya ke magana."

Ganin ta fara dariya yasa shi ma ya fara duk da sautin nashi baya fitowa sosai ita kaɗai ta ke ji.

Kallon kallo su Dady ke wa juna dan jin dariyar Sabreen ƙarara mamakin su ya baiyana,momy kuwa da hajia da farrah sai washe baki su ke yi,shi kuwa dady mamaki ne ke ƙara kamashi matuƙa.

Doc zain ne ya zo inda su ke ,shi ma fuskar shi ɗauke da annuri ya ce musu,"Kun ji ko? suna matuƙar son juna,wanan shi ne maganin shi,am srry to say,ba zaku gan shi ba har sai ciwon yayi sauƙi ,amma ita dole a barta anan,yanzu zaku iya tafiya,zan shigar da abincin a bashi,amma zuwa anjima zaku iya dawowa ku ɗauke ta idan ya kwanta."

Ba wanda yaji ba daɗi a ranshi sai ma jin daɗin da su ka yi,dan samun sauƙin shi na tattare da sabreen ɗin.

Kallon shi Dady yayi fuskar ɗauke da annuri ya ce,"Ba komai doc mun gode sosai kuma mun ji daɗi allah ya ƙara mishi lafiya."

A tare su ka amsa da ,"Amin ya Allah!,su juyo abin su .

Murmushi yayi doc zain yayi ya ɗau kular abincin ya shiga da ita ɗakin,da sallama ya shiga dariyar da su ke bai bari sun ji sallamar ba.

" Hmm irin wanan love!

A tare su kalle shi suna ƙoƙarin tsagaita dariyar su,shi ma murmushin yayi ya ce,"To ga abinci ya shi sai ya sha magani yadda za ku tafi gida da sauri."

Murmushi Sabreen tayi ta ce,"To doc nima na ƙagara mu tafi shi ne dai ya ke son zaman."

Bai ce komai ba,ya fita abin shi yana murmushi.

Kular abincin da buɗe farfeson dan kalin turawa ne da hanta,sai tashin ƙamshi su ke yi, zubu mishi tayi.

"Au sai ka ɗan tashi zaune kaɗan,"Tana faɗa ta kai hannuwan ta kafaɗar shi da zummar taimakon shi ya ɗan zauna kaɗan.

Tsigar jikin shi ta tashi yarr,lumshe ido kawai yayi,wani abu ya mishi yawo a zuciya.

Ɗauko abincin tayi "Ka fuɗe baki da ido,ka ci abinci."

Buɗe idanuwan yayi,amma ya ƙi buɗe bakin,marairai ce fuska tayi alamar shagwaɓa.

Murmushi yayi komai Sabreen tayi burge shi yake yi,ba wai abincin ba ne ba zai iya ci ba,yana son ya wanke baki ne.

"Ba ka son muje gida ko?

"Ina so ko dan.. sai yai shiru.

Bata naimi ƙarin bayani akan abinda ya kasa faɗa ba,ta ce,"To ka ci dan allah,"cikin shagwaɓa ta ƙarasa maganar.

"Baki na ba'a wanke ba."

"Hm kai ana ta kai kana ta kaya.",a ran ta ta faɗa a fili kuwa cewa tayi,"Toh bari na kawo ma roba da ruwa ko."

Tana faɗa ta ajiye abincin ta nufi bayin,maclean da brush,sai ta ɗibu ruwa a wani cup sai ta tawo da ɗan ƙaramin ruba kamar bahu me faɗi.

Da ɗayan hannun ya ɗan wanke bakin,taɓe baki kawai ta ke yi ganin haƙuran basu yi datti ba,ya gama ta maida da su bayin,ta zubar da ruwan.

Har ta shiga bayin ta fito idanuwan shi su na kanta.

"To bismillah! faɗa haɗe ta ɗan murmushi,shi ma murmushin yayi ya buɗe bakin ta fara bashi,a hankali yake ci,ka ɗauka haɗiyewa kawai ya ke yi,ba taunawa ba.

Yaci sosai shi kan shi bai san ya ci da yawa ba,"Yawwa nawan saura magani,"yana gani ta ɓallo magani dan daman likitan ya gaya mata yadda zata bashi.

Miƙa mishi tayi ba musu ya amsa ya sha,saida ta ɗan gyara gurin sanan ta dawo ta zauna.

Murmushi tayi ganin irin kallon da yake mata,gashi tana son yi mishi maganar su Dady tana jin tsoro.

"Ki ce wani Abu."

Saida ta murmusha sanan ta ce,"To na gaji da magana ni kaɗai saidai kayi ta kallo na ka ƙi magana."

"Ina jin daɗin yadda ya  kike magana."

Dariya tayi sosai ta ce,"nima ina jin daɗin yadda kake magan har dariya kake ban"

Lauya harshe tayi ta ce,Ki ce wani Abu," ta fashe da dariya ta ce,"Haka kake magana fah."

Dariya yayi yadda tayi maganar y mishi daɗi,suna nan zaune aka kira sallah da sauri ta tashi tayi yana kallon har da iddar tayi addu'a tana zaune a gurin ya ce,"Amin!

Bayan ta tashi ta dawo ta zauna,"Me kika roƙa ne?

"Me kuwa banda allah ya ba miji na lafiya."
Dariya yayi yana jin wani irin farinciki na ratsa zuciyar shi,duk ya manta da komai da kowa.

A haka su ka cigaba da fira cikin farinciki da jin daɗi musamman Sabreen duk wata kalma da zai faɗa dariya ta ke bata,har lokacin la'asar ta tashi tayi sallah yana kallon ta har da idar ta dawo ta zauna suka cigaba da fira jikin jin daɗi.

Bayan maqrib su Dady su ka dawo tare da abinci,ko wannen su yana son ganin naufal amma suna tunanin ganin zai iya jan matsala shiyasa ba wanda ya tunkari wani da maganar,kai tsaye office ɗin doctor zain su ka nufa bayan sun gaisa Dady ya ce,"Doctor ya koƙari ya me jikin?

Fuskar ɗauke da annuri ya ce,"Alhmadulilah! jiki yayi sauƙi sosai abin  mamaki gaskiya yaran nan su na son junan su sosai,amma zaku ƙara hakuri da rashin ganin shi har nan da kwana biyu da zuwa lokacin insha allah jikin zai yi sauki sosai."

"Ba komai likita allah ya ƙara sauki,am..zamu iya ganin sabreen ɗin?

"Why not bari na kira ta,"yana gama faɗa ya fita.

Da sallama ya isa ɗakin fuskar shi ɗauke da annuri ganin yadda su ke fira ko gajiya basu yi abin ban sha'awa.

"Kai wanan irin so haka."

Murmushi Sabreen tayi a ranta ta ce,"Wani so ana zaune ƙalau."

A fili kuwa murmushi tayi ta ce,"Ya koƙari doctor?

Saida Naufal yaji wani irin abu ya soke shi a zuciya ganin yadda sabreen ta ke zubawa doctor xain murmushi,shi ma zai murmushin yake yi,lokaci ɗaya ya ɗaure rai,yai ƙasa da kai.

"Alhmdulilah! ya me jiki?

"Jiki yayi sauƙi."

"Ai kuwa naga alama,allah ya ƙara sauƙi Sabreen ki zo ki amsar mishi magani.",yana faɗa ya juyo bai tsaya jin amsar da xata ba shi ba.

Wani irin haushi mai ɗauke da mugun kishi ya kama Naufal taya zai ce ta bi shi,kuma harda kiran sunan ta,a hankali yaji zuciyar shi ta fara mishi zafi.

Hannuwan ta,ta ɗaura kan ƙirjin shi,lumshe ido ya fara yi yana ajiyar zuciya a hankali ga tsigar jikin shi ta ke tashi.

"Ya dai magani zan amso fah,koma ba daɗewa zan yi ba,wai ba ka son gaji sauƙi ne kafi son ganin mu cikin damuwa."

har lokacin bai buɗe ido ba,a hankali yake sauke ajiyar zuciya,muryarta na ratsa kunnan shi tana shiga cikin zuciyar shi.

"Ya hakuri yanzun zan dawo."

Jikin shi ya mutu bai jin zai iya yin magana kai kawai ya ɗaga mata alamar eh,ganin hakan yasa ta janye hannuwanta daga ƙirjin shi,ta fita saida yaji wani iri.

Kai tsaye office ɗin ta nufa,ganin su dady yasa ta washe baki ,gurin dady tayi ta rungume shi tana jin son shi na ratsa sassan jikin ta,sun daɗe rungume da juna kafin su ka janye,cikin jin daɗi da soyayya su ka gaisa da kowa,bayan sun gama gaisawan zasu tafi har bakin motor ta raka su,Dady ya kalle ta ya ce,"Sabreen Kin cika ƴa abin alfahari    allah yai miki albarka ya ba mijin ki lafiya da zuri'a ɗaiyaba."

Saida tayi ƙasa da kai sanan ta ce,"Amin Dady n gode."
Duk sukai sallama da juna su ka tafi,kamar tayi kuka ta daɗe a gurin kafin su ka tafi,saida ta ɗauki abincin sanan ta wuce ɗakin,na zuwa yayi barci,kusa da shi ta zauna ta ƙura ma fuskar shi ido tana jin wani irin abu a zuciyar shi.

Har lokacin sallar isha'i bai tashi ba,har ta idar ta sallar shiru,ta ci abincin bai tashi ba,har ta gaji ta kwanta.

"Kiyi hakuri karki barni zan rayu da ke,ina buƙatar ki.."cikin wata irin sigar numfashi mai  ɗauke da nishin kuka yayi maganar.

"Ah..Ahh ..ni ka barni bana soo...

"Ɗan allah..."firgitt ya tashi yana nishi da haki ga wani irin abu da ya ke ji a zuciyar shi mara daɗi,idan da sabo ya ci ya saba da irin wanan mafarkin amma ya kasa savawa,ya daɗe yana sauke ajiyar numfashin ,kafin ya ɗago kan shi,a ɗayan gadon ya hango ta,tana barci kasancewar ɗakin da haske bata kashe wuta ba,ji yayi kamar ya tashi ya tunkare ta dan yana

cikin tsananin sha'awa,da ƙyar ya iya faɗa da zuciyar shi akan tai hakuri,a haka har barci ɓarawo ya ɗauke shi.

Asubar fari sabreen ta tashi alwala tayi da tada sallah har ta idar da sallar asuba bai tashi ba,bayan ta idar ta tawo ta zauna kusa da shi,idanuwa ta zuba mishi,har ƙarfe tara naufal bai tashi ba,doctor zain ya shigo ya duba shi,har su Dady su ka xo bai tashi ba,sun daɗe kuma sun leƙo sun gan shi,har su ka tafi bai tashi ba.

.

Kuyi hakuri posting din  dazu an samu tsallake sai dai Kuyi hakuri wlh sbd ba laifina bane nima a haka littafin yazo min.

.

[12/23, 2:29 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт By Gяσυρ O F Hуρє Hαυѕα Nσνєℓѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚

[12/23, 2:34 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: 🌹 *NI* *DA* *MALAMA* *TA* 🌹

*By*

*Fatima* *Batulah*

*~✍🏽✍🏽GOLDEN PEN WRITERS ASSOCIATION✍🏽✍🏽~*

Page 21 (last)

.....................................

Asubar fari sabreen ta tashi alwala tayi da tada sallah har ta idar da sallar asuba bai tashi ba,bayan ta idar ta tawo ta zauna kusa da shi,idanuwa ta zuba mishi,har ƙarfe tara naufal bai tashi ba,doctor zain ya shigo ya duba shi,har su Dady su ka xo bai tashi ba,sun daɗe kuma sun leƙo sun gan shi,har su ka tafi bai tashi ba.

Ƙarfeɓgoma sha biyu da kwata daidai ya farka lokacin tana zaune kusa da shi akan kujera,akan fuskar ta idanuwan shi su ka ƙarasa buɗewa,murmushi tai mishi ,shi ma murmushin yai mata.
"Ka tashi? ya jikin? yau ka daɗe baka tashi ba,kasan yanzun ƙarfe nawa ne?abincin ka har yayi sanyi."

Murmushi yayi wanda saida haƙuran shi su ka baiyana,ganin yadda ta ke magana  ba ko tsayawa.

Tunowa yayi bashi da tsarki da sauri yai koƙarin miƙewa,taimakon shi tayi ya miƙe zaune,ta kalle shi ta ce,"Ya dai?

"Bani da tsarki zan yi wanka."
 "Baka da tsarki." ta faɗa cikin rashin fahimtar inda ya dosa a mgnr tashi.
"Eh xanyi wankar tsarki bani da tsarki."

Bata tambaye shi ta shige bayi,ta haɗa mishi komai da komai,sanan ta fito ta temaka mishi ya tashi ya shiga bayin,saida ta ƙara gyara gurin tsabb,bayan ya fito ya zauna ta sulale ta fita ganin yana koƙarin cire kaya a jikin ta,murmushi yayi kawai,ya saka kayan shi,yaji daɗin jikin shi sosai,kafin ta shigo har ya fara sallah,ko da ta ahigo ta ga yana sallat taji daɗi ,guri ta samu ta zauna tana kallon shi,saida yayi Izahar  ta kwana ukku sanan ya idar,bayan ya idar ya dawo su ka zauna ta bashi abinci ya ci kaɗan sanan ya sha magani su ka cigaba da firar su cikin jin daɗi.

Yau kwanan Sabreen ukuu a asibiti tare da Naufal,yanzun kam jiki yayi sauƙi sosai da sosai,shaƙuwa ta shiga tsakanin su mai ƙarfi,musamman Naufal wanda ya gama tabbatar da ya kamo da ciwon son Sabreen,wanda yake jin duk wani fitar numfashin su tare su ke fita,ga wani irin mugun kishi.

Zaune ta ke kan kujera shi kuma yana zaune kan gado idanuwan shi duk sua kan ta,tunani ta ke yi a ran ta,"Ta ina zan fara mishi maganar su dady gashi yau za su zo gurin shi,yanzun ya zan yi," ɗago wa tayi haɗe ido su ka yi tai murmushi murmushi da ido yai mata magana da lafiya kuwa dan ya ga fuskar ta akwai abinda ta ke son faɗi.

Saida ta ja garuwar ajiya zuciya sanan ta ce,"Ɗazun su Dady sun zo kana barci,"idanuwan ta suna kan shi dan taga yanayin da zai shiga.

ƙasa yayi da kai wani abu yana bijiro mishi a rai,ganin hakan yasa ta kama hannuwan shi ,ta raunana murya ta ce,"Dan allah karka ji wani abu wllahi dady da momy duk sun yafe ma,kaddara ce,ka kwantar da hankalin ka."

Runtse idanuwan shi yayi abubuwan da suka faru suna dawo mishi,ahankali ya buɗe su,saida sabreen ta tsorata ganin yadda idanuwan su ka canza sukai jajir,rungume shi tayi,"Dan allah kayi hakuri kar wani abu ya same ka,ba wanda ke fushi da kai."

A hankali yaji zuciyar shi tana mai sanyi,amma yana jin nauyin iyayen shi harda sabreen ɗin,saidai ya kasa gane dalilin da yasa ya aikata irin wanan ɗayan aikin ki,ji ya ke kamar ba shi ba,taya zai yi zina abinda ya tsana a duniya,wasu zafaffan hawaye sukai nasarar zubu mishi,ƙokarin yin magana yake yi amma maganar taƙi fitowa.

Kuka Sabreen ta fashe da shi,saida yaji wani radaɗi a ran shi,cikin kukan ta ce,"Dan allah kayi hakuri nasan ba laifin ka ba ne laifi na ne,bana sun su dady su zo su ganka a haka,kayi shiru."

Shafa kan ta yayi yana jin zafin hawayen ta,tamkar shi ke yin su,janye ta yayi su ka fuskanci juna da ido yayi mata magana da tayi shiru,zuwa yanzu Sabreen ta iya magana da ido sosai ,ita ma da idon tayi mishi magana ta yayi hakuri ya natsu,share mata hawayen yayi,shiru su ka yi kowannen su yana ƙokarin samawar zuciyar shi.

Sun ɗau lokaci a haka suna kallon juna kafin sabreen ta janye jikin ta,kasa ce mata komai yayi duk da kasancewar ba ji daɗi ba,bayi ta shiga wa wanke fuska sanan ta fito,ta dawo ta zauna

ɗan nisa da shi sanin su dady zasu iya zuwa any time,kallon ta kawai yake yi yana mamakin hali irin na ta,yasan ya mata mugun laifi amma bata nuna mishi ba ko kaɗan sanan har ta ke ɗaurawa kanta laifi,lallai yasan halin dady kuma ba xai manta kalaman shi ba,yanzu ya yafe mishi wanda ko shakka babu sabreen ɗin ta buƙaci haka,runtse idanuwan shi yayi yana ƙara jin wani irin mugun azababben son sabreen na ratsa zuciyar shi lallai ta haifu,shi kuma yaci amanar iyayen shi da marainiyar allah.
ganin yadda ya kulle ido yasa sabreen kiran sunan shi,"Ya Naufal!,kai tsaye zuciyar shi ta amsa saƙon muryarta,a hankali ya bude idon.
"Yah kayi hakuri dan all..
"Ke kin hakura."
"Na hakura ai baka min laifin komai ba,ni ka hakura duk abinda haulat tayi dan na ji haushi ne sann.....

Sallamar su dady ne ya katse ta,da sauri ta ƙarasa gurin shi,amma ta kasa rungume shi,shi ne ya rungumu ta,shi kuwa naufal yana jin su yai ƙasa da kai wata irin kunya ta mameshi musamman momy.

Kowannen su kallon su naga naufal wanda yai ƙasa da kai,farrah ce ta fara ƙarasawa gurin shi,fuska ɗauke da annuri ta ce,"Brother ya jikin?

kan shi a ƙasa ya ce,"Da sauƙi sosai."
"Allah ya kara sauki yaya.",yaji daɗin yadda yaji tana mishi magana wanda hakan yasa ya ɗan ji daɗi.

"mutum india ya jikin? kabar amarya da damuwa gaskiya kaji sauƙi kasan bana son ganin damuwar ta,gashi ka siye zuciyar mu," cikin dariya ta ƙasara maganar,dariya kowa yayi harda momy da dady wanda ba ƙaramin daɗin hakan yaji ba.

Kusa da shi kaɗan momy ta matso shi kuwa har lokacin kan shi na ƙasa bai hadda ido da kowa ba,duk sun fahimce kunyar su yake ji sai tausayin shi ya ƙara kama su.
"Naufal ya ƙarfin jikin."
Rawa bakin shi ya fara ji,"da saauƙkii."
ganin ya fara daburewa yasa ta faɗin,"Sauƙi sosai,dan yau zamu koma da kai gida, gidan duk ba daɗi ",idanuwan ta na kan shi,ta ƙarasa maganar,lumshe ido yayi yana jin wani irin sanyi a ranshi momy ce ke mishi magana kamar yadda ta saba kenan batai fushi da laifin da ya aikata ba,ganin yanayin da ya shiga yasa dady ƙarasowa inda yake ya ce,"Naufal halan dai baka son zuwa gida ne."

Lokaci ɗaya yaji bugun zuciyar shi na ƙaruwa,koƙarin faɗa da numfashin shi ya fara yi wanda ke koƙarin ɗaukewa,ganin hakan ya ruɗa su dady sosai,zama yayi kusa da shi ya dafa kafaɗar shi ya ce,"Naufal gudun iyayen ka kake yi? kana tsoran mu ne? naufal ba ka da wasu bayan mu,ko meye ya faru mu iyayen ka ne,plss my son ka kwantar da hankalin ka,kaddara ce wanda,Allah da kan ce ya ce," *Idan* *yana* *son* *mutum* *da* *alkairi* *sai* *ya* *jarabce* *shi* ."

Saida ya numfasa sanan ya ɗaura da faɗin,"Naufal allah yana son ka da alkairi ya jarabce ka dan ka kiyaye gaba,ba lalai abinda ka aikata ɗabi'ar ka ba ce,ko kana da kuɗirin aikata hakan ba saidan kaddara ce jarabta,mun ƙara fahimtar abubuwa da yawa faruwar wanan abun,wanda ni kai na,na gane kuskure na,na gaya ma irin waɗan nan kalaman ,wanda yanzun allah ya nuna min,kuskure na duk sanadin faruwan hakan,sry my son mubar hakan a matsayin kaddara," jin hawaye na son fitowa daga fuskar shi yasa ya tsaida maganar badan ya gama ba.

Maganganun Dady sun yi tasiri sosai a jikin su,musamman naufal wanda yake jin shi wani iri tamkar an canza mishi duniya,rungume Dadyn yayi wasu zafafan hawaye su ka fara bin fuskar shi haɗe da kuka mai sauti,shi kan shi dadyn hawayen da yake makalewa su ka fito,haka zalika ko wanne da ke ɗakin saida ya kuka,sun daɗe a haka su na kuka ba wanda ya kalle wani balle yai kuƙarin ba da hakuri.

Shafa kan shi dady yayi yana faɗin,"Is okk kayi haba kai fa namiji ne."
  ai kamar ƙarawa naufal kukan ya ke yi, daɗi ya haifar mishi da kukan,jin ya ƙara sautin kukan yasa sabreen ta kara fashe da matsanaicin kuka,da sauri hankalin su ya dawo gare ta,dariya su ka yi dukkan su har dady da naufal ɗin sanin abinda yasa ƙara kukan.

"Ka gani ko," dady ya faɗa yana kallon naufal ɗin wanda shi kuma idanuwan shi yana gurin sabreen.

"Ga gani ko,ni kai shiru dan allah dan ta samu tayi shiru ita ma," cewar hajia wacce idanuwanta ke kan naufal.
 fashe wa da dariya su kara yi,ita kuwa sabreen gurin momy tayi tana kuka ta rungume ta.

"Kiyi hakuri kin ji,ƙyale su ba ruwan mu da su," cikin rarrashi tayi maganar su kuwa,dariya su ke kasa-kasa.

Sun sake jiki sosai kamar ba wani abun da ya fara,duk yadda su ka so naufal ya sake jiki ya kasa,dan ya kasa haɗa ido da kowa a cikin su,yana son kallon sabreen amma ya kasa dan tana jikim momy,yana dai ɗan taɓa fira kaɗan kaɗan,ba su damu ba dan sun san daman ba sai son mgn ba ne.

Tun daɗe suna fira jikin jin daɗi da nuna kulawa,wanda naufal yaji daɗi matuƙa wasai yake jin zuciyar shi sai wani daɗe ma ta jake ji mara misaltuwa,tun mantar da shi abinda ya faru,sun so a sallame su yau amma doctor zain ya ƙi,dole sai gobe shi kan shi naufal ɗin bai ji daɗi ba,ya so zuwa gida,amma ya nuna musu yau da gobe duk ɗaya ne a gurin allah,har gurin motor sabreen ta raka su farrah sai zolayarta ta ke yi bata kula ta,anan ma saida su ka rarrashe ta sanan ta ɗaurr bata yi kuka ba,tana tsaye har motor su ta bar asibitin sanan ta juya lokacin an kira sallar maqrib,tana zuwa ɗakin yana fitowa daga bayi,kallon juna su ka ji yayi kamar ya shekara bai ganta ba,murmushi su kai wa juna,da saure ya ɗauke kai tuno yayi alwala,sallaya ta shimfiɗa mishi ya hau,ita ma bayin ta shiga ta ɗauro alwala,baya da shi kaɗan ta tayi.

Tana zaune tana lazimi ya idar da sallar har ya gama lazimin ya juyo ƙura mata ido yayi yana jin wani abu yana tasar mishi,saida ya lumshe ido sanan ya ce cikin nakasassar muryar shi,"Me kika roƙar mana."
ɗagowa tayi ta kalle haɗe da sakar mishi murmushi,"Wa zan ma addu'a idan ba ku ba,kai Dady hajia momy farrah,ku ne duniyata rayuwata."
Tausin sabreen ya ƙara kama shi,"lallai bata waɗan da su ka fi mu,zan raini ki sabreen zan kula zan miki gata,kin min komai kin temaki ni kin min gata..
"Ya dai? ina kallon ka ɗazun kasa cin abinci ka yi."
Tashi yayi ya ɗauke sallayar ya koma ya zauna,da ido ya kira ta,kusa da shi ta zo janyota jikin shi yayi ya rungume ta tsamm,wata irin ajiyar zuciya ya fara sauke wa,zuwa wanan lokacin sabreen ta saba da runguma gurin naufal,saidai bata bari yai mata kiss duk yadda ya so.
"Ka ci abinci ka sha magani ",ta faɗa tana kokarin janye jikin ta.

"Meye sa ki kuka ɗazun?
saida ta gama janye jikin ta sanan ta ce, "ba komai."
Runtse ido yayi yana sauraran bugun zuciyar shi wanda ke buguwa da son sabreen,"Allah yasa ki amci da soyayyata sabreen ban san lokacin da zuciyata ta kamu da son ki ba,"a ran shi yai maganar.
Abincin ta zubo mishi kamar yadda ya saba ita ke bashi a baki,yaci sosai sanan ya sha magani,xama su ka yi su na jiran kiran sallar isha'i,ƙura mata idanuwan shi yayii,yana jin wani irin abu a ran shi kamar ya janyo ta ya haɗiye ta yake ji.

Jin kiran sallar yasa duk su ka tashi shi ya fara shiga yayi alwala sanan ita ma ta shiga,bayan sun idar da sallah,ya koma ya kwanta baya jin yin magana ita kuwa bata matsa mishi ba,dan ba wani damuwa tayi ba,kwanciya kawai su ka yi,kowa yana saƙar zuciya daga haka har barci yai awan gaba da su.

Kiran sallar farko ya tashi sabreen daga barci,tana tashi tayi addu'a sanan ta tashi gurin shi ta je dan tashin shi.
Shi kuwa a lokacin yana tsaka da mafarkin da ya saba yi,hannu ta kai ta taɓa shi,"Ka tashi lokacin sallah yayi."

Can cikin mafarkin yake jin maganar,ga shi a lokacin su na cikin love.
"Ka tashi! da ƙarfi ta faɗa wanda yasa ya tashi da sauri,yana haki yana nishi,a kan fuskarta idanuwan shi su ka sauka,janyo ta yayi jikin shi ya rungume ta yana wani irin nishi.
"Yah lafiya kuwa,ko jikin ne?
Daman ba'a cikin haiyacin shi ya ke ba,yasan dai yaji tana magana amma bai fahimtar abinda ta ke faɗi,hankalin shi baya jikin shi,gaba ɗaya ya ruɗe ya fita haiyacin shi,ta ko'ina a jikin ta yake kai hannuwan shi,ruɗewa tayi jin yana kokarin zura hannuwan shi cikin rigarta,gashi ta ƙwatar kan ta.

Cikin zaƙuwa yake wasa da halittar ƙirjin ta,zuwa yanzu Naufal ya ruɗe ya fita haiyacin

shi,koƙarin yaga mata riga ya fara yi,kuka ta sake me ɗan ƙarfi shi be san ma tana yi ba,ganin yana ƙara kuƙarin raba ta da kayan jikin ta yasa ta ganna mishi cizo a kafaɗa,yaji zafi hakan yasa ya sake ta,yana sakin ta,ta faɗa bayi da gudu tana kuka.

Da ƙarfin gaske yake sauke ajiyar zuciya,ji yake kamar yayi hauka kwanciya yayi ya runtse ido,wani abu ke bijiro mishi a rai,ji yayi ba zai iya hakura ba,ko kaɗan bai taɓa tunanin haka sabreen ta ke ba,zumbur ya miƙe sai kuma ya dawo ys zauna,yana kuƙarin ba zuciyar shi hakuri,safa da marwa ya fara yi,duk dan yaji sauƙin abinda yake ji,da ƙyar ya isa sarrafa zuciyar shi ta hakura.

Ita kuwa tana faɗawa bayin ta fashe da kuka wanda bata san dalilin yin shi ba,saida tayi me isarta sanan ta tashi ta ɗaura alwala,kasa fitowa tayi dan tsoro da kunyar shi ta ke ji gashi lokacin sallah na tafiya.

Ganin bata da niyar fitowa gashi lokaci yana yi kuma sai yayi wanka yasa ya fita daga ɗakin,dan ba zai iya magana ba,balle da ita.
Jin shiruuu yasa ta ɗan leƙo ganin ba kowa yasa ta fito,ta fara sallah,tana cikin sallah ya shigo bayi ya shiga,yana fitowa ya fara sallar shi ma.

Gaba ɗaya kunyar shi ta ke ji,kan ta a ƙasa ta ɗan kimtsa ɗakin,bayan ya idar da sallar ya dawo ya kwanta,dariya yayi ganin yadda ta jin kunyar shi a ran shi ya ce,"Akwai aiki kuwa."

Ƙarfe bakwai daidai su Dady su ka iso asibitin ba su je office ɗin doc xain ba kai tsaye ɗakin suka nufo,suna zuwa sabreen ta washe baki tai kan su,cikin so da ƙaunar juna su ka gaisa,har naufal duk sun gaisa sosai cikin jin ɗaɗi,har lokacin naufal yana kula da sabreen bata yarda sun haɗa ido ba dariya ma ta ke bashi.

Basu tsaya ɓata lokaci ba,su ka tafi gurin doc xain dan ya basu takardar sallama,ya kuwa basu tare da musu fatan alkairi.
Har gurin motor doc zain ya raka su,yai musu sallama.
Naufal da Dady suna gama su kuma suna baya,har su ka isa gida,suna zuwa sabreen tai ɗakin farrah,shi ma ɗakin shi yayi,kowa ya watse.

"Yadai malama."
Kallon farrah sabreen tayi haɗe da taɓe baki,ta juyar da kan ta kawai.
Dariya farrah tayi ta ce,"Yarinya kenan ai ina kula da ke a asibiti ",cikin dariyar da zolaya ta ƙarasa maganar.

"ke fah ƴar iskace,ƴar sa ido kawai."
"Naji gayamin kun yi ne,kai lamarin ku sai ku asibitin ma."

Da sauri Sabreen ta tashi ta fita ɗaga ɗakin tana faɗin,"Idan na biye miki wuta zaki kai mu banza ƴar isaka kawai."

Dariya farrah tayi sosai,tana mmk hali irin n sabreen.

Tana fita tayi ɗakin hajia,saida hajia ta gama yi mata tsiya sanan ta barta,ta kwanta.

Shi ma yana zuwa ɗakin shi ya kwanta bayan yayi wanka da tunanin sabreen a ran shi,addu'a yake yi allah yasa dady ya barsu zu je gidan su.

Ita dai momy bata koma barci ba,abinci ta haɗa musu me rai da lafiya bayan ta gama ta koma ɗaki tayi wanka sanan ta fito,lokacin ƙarfe goma sha biyu da kwata,ɗakin Dady ta. shiga barci ta tarar yana yi tashin shi tayi,dan lokacin sallah yayi bayan ya tashi yayi wanka ya nufi ɗakin naufal dan su tafi masallaci tare,kafin naufal ya shirya an kira sallah,yana shiryawa su ka fita ya so ganin ta a falo  .

Saida hajia ta idar da sallah sanan ta tashe ta,bayan tayi sallar ta koma ta kwanta hankali kwance ba tunanin komai a ranta.

Bayan sun dawo lokacin duk suna falo,ware idanuwa yake yi amma be hango ta ba,wani iri yaji yana marmarin ganin,"yanzun cikin nan mun dawo gida haka zaki tunda min,"ya faɗa a ran shi ,duk sai yaji da basu dawo ba.

Bayan sun zauna sun Dady ya tambaya ina sabreen,Hajia ta ce,"Barci ta ke yi."

"Ayyah ku barta ta huta tana buƙatar hutu,da nayi tunanin ko yau zaku tafi sabon gidan ku wanda na siya."

Wani irin daɗi ya kama naufal wanda saida ya kasa ɓoyewa kowa ya fahimce hakan.

"Amma ina jin ku ƙara hutawa bari dai sabreen ɗin ta tashi."

Nan ma saida labarin zuciyar shi ya isa fuska,"Ya dady zai yi haka",ya faɗa a ran shi,yanzu ba zai iya kayan wata mgn akan wanda dady yayi ba,da ya ce wani abu.

Har su ka gama cin abinci sabreen bata tashi ba,hankalin shiul baya gurin su,duk abinda su ka ce daga eh sai a'a ya ke cewa.

Tashi yayi ya shiga ɗaki,lokacin kowa ya tashi dady ya fita,wayar shi ya ɗauka,number farrah ya kira tana ginin kiran ta ɗauka da sauri.

"Ke turomin Number Sabreen yanzun nan",yana gama faɗa ya kashe wayar.

Dariya farrah tayi,"Hm su yaya manya,ko number matar ta ka baka da shi,tana mgnr tana tura mishi number.

Tunda ya katse wayar ya ƙura ma wayar ido yana jikin numberta,ganin soƙon ya shigo ya buɗe da sauri,kiran number yayi a ƙufule,ringin wayar ta fara yi ,ya ƙagara ta ɗauka.
Lokacin tana barci bata ji kiran ba ,har wayar ta katse,kira ya ƙara yi amma bata ɗauka ba,wani jin zafi yaji a zuciyar shi,gaba ɗaya sai yaji ya ruɗe taya zata mishi haka,idan ta guje shi a lokacin da yake fuƙatar ta,bai san yadda zai yi ba.

Kamar yaje ɗakin hajia yake ji,kwanciya yayi badan yana jin barci ma,"Taya zaki min haka ina son ki,"a file yake faɗin hakan

Karfe ukku da rabi sabreen ta tashi saida tayi wanka sanan ta dawo ta saka duguwar riga ƙirar dubai,kamar ance ta ɗauke wayarta ,tana ɗauka ta ga kiran"Ya Naufal" sunan da ta sa mishi kenan,kallon wayar tayi ta ce,"Lafiya kuwa",kiran wayar ta shiga yi.
Daman har lokacin be kwanta ba yana jin ringin ya ɗau wayar ganin kiranta yasa ya miƙe zumbur ya ɗau wayar.

"Sabreen",cikin sanyin murya ya faɗa.
A ruɗe ta ce,"Ba ka da lafiya ne jikin ne?
"Sabreen zuciyata ki zo ɗaki na."

A ruɗe ta jefar da wayar ta,tashi ɗakin shi ta nufa a ruɗe bata haɗu da kowa ba,tana shiga ɗakin ta gan shi a kwance da gudu ta ƙarasa,juyo da shi tayi duk ta ruɗe ta kasa magana ga bakin ta yana rawa.
"Sabreen zuciyata xata fashe!
A ruɗe ta taɓa zuciyar shi saida ta ƙara ruɗewa jin bugun zuciyar kuka ta fara yi rungume ta yayi.
"Sabreen zaki fasa min zuciya,son yi yayi min yawa dan allah ki cece ni sabreen."

Ta abai-abai ga ke fahimtar shi,ta kasa magana gashi ya haɗa ta da jikin shi,wanda tana jin dokan da zuciyar shi ke yi.
"Sabreen kimin alfarma ki zauna da ni,ki kula da ni ba zan iya rayuwa babu ke ba,plss sabreen ki amince da ni dan allah mu tafi gidan mu muyi rayuwar mu."

Ta kasa magana ta kasa fahimtar inda maganganun shi su ka nufa.
Shiruu dukkan su suka,sai zuciyoyin su da ke bugawa,sun daɗe rungume da juna,sanan ya ɗago ta suka fuskanci juna lauyin idanuwan shi duk sun canza wani irin yanayi ya tsinci kan shi,cikin dakusassar murya ya ce,"Sabreen pls ke amince da ni bazan cutar da ke ba."
kai kawai ta ɗaga mishi alamar eh,ƙara rungumota yayi,shiruu tayi tana jin yana kissin ɗin ta ko'ina.

"A'a yaya kayi hakuri dan allah,kar wani ya shigo fah."
danne zuciyar shi yayi ya sake ta,idanuwan shi a rufe,janye jikin ta tayi tana son fita daga ɗakin,hannuwan ta ya riƙo.

cikin muryar da bai yi tunanin zata ji abinda xai faɗa ba ya ce,"Stay with me sabreen i can't without u,ba zaki taimake ni ba."

maganganun shi sun kashe mishi jiki ainun,"me ye nufi yana son ta komai."

Cikin ƙarfin hali ta juyo ta ce lokacin hawaye sun fara zarya a idon ta,"Meyasa xan zauna da kai,bayan baka so na,Malama haulat keke so,ni saki na zaka yi."

Da ƙarfi zuciyar shi ta buga,kama zuciyar yayi ji yake yi kamar zata fashe dan yadda take mishi zafi,ganin halin da yake ciki yasa sabreen ta ruɗe riƙo shi tayi a ruɗe ta ce,"Waiyo Allah na! na shiga ukku! zan zauna da kai har ƙarshen rayuwata dan allah kar wani abu ya fara zan zau.... Haɗa bakin su yayi wanda hakan yasa tai shiruuu sai wasu hawaye da ke bin fuskarta wanda ba ta ce ga dalili ba,wanan karan dai shiruu tayi ta zubawa sarautar allah ido sai sarrafata ya ke yi yadda ya ke so.

Saida ya gama jagwalgwalata sanan ya ƙyale ta,badan komai ba sai dan tuno a inda su ke ,kallon ta yayi tana hawaye haushin kan shi ya kama shi.

"Dan allah kiyi hakuri kin ji na kasa sarrafa kai na ne,plss ki daina kuka,ya sa hannu ya share mata hawayen.

Rigarta ya fara gyara mata,daman bata saka komai ba sai rigar,idanowan ta a rufe tana hawaye.

Janyo tayi yayi,"Kiyi hakuri ba zan ƙara ba kin ji ki daina kuka,"lallashin ta yai tayi har ta daina kukan amma ta kasa buɗe ido ta kalle shi,gashi an kira sallar azahar.

"Sabreen ki buɗe ido kin ji Dady zai shigo yanzun kin son ya zo ya gan ki a..

Tun kafin ya rufe baki ta janye jikin ta,ta fita da gudu.

A lokacin Dady da momy sun fito,bata lura da su ba ta wuce da gudu,kallon kallon Su kai wa juna,murmushi momy su kai magana da ido wanda su kaɗai su ka fahimce inda su dosa,daman ɗakin naufal ɗin za shi har ya sa hannu zai buɗe sai kuma ya fasa ya juyo.

Ya daɗe anan inda ta barshi dan gaba ɗaya jikin shi ya mutu,sai can kuma yai ƙarfin hali ya tashi ya shiga bayi yayi wanka sanan ya fito yayi sallah.

Da gudu ta shiga ɗaki binta da kallo kawai hajia ke yi,kwanciya tayi tana kuka wanda ba ta ce ga dalili ba,ta kasa yin tunanin komai dan kwakwalwarta ta cushe.

Bayan sallar maqrib Dady ya tara su a falo,nasiha ya musu wacce ta ratsa ɗukkan jikin su,sanan kuma ya ce naufal ya ɗau matar shi su tafi,kuka sabreen kamar ranar farko da xata gidan naufal ,shi kuwa wani mugun daɗi ya maimaye shi saidai fuskar shi ta nuna,da ƙyar sabreen ta rabu da so,direba ne zai kai su gidan ,akwai ƴar tazara sosai dan unguwar ba ɗaya ba.

Kuka sabreen take yi sosai,kusa da ita ya matso duk da idanuwan ta a rufe su ke saida taji kunya amma ta kasa ko da motsi sai ƙara sautin kukan da tayi,riƙo ta yayi,cikin sanyin murya ya ce,"Sabreen baki so na?kina tsoro na ko?

Kamar bata san abinda ta ye faɗa ba tai banza da shi,ganin hakan yasa ya ce,"Sabreen plss ki daina kuka har cikin rai na nake ji,zan nuna miki so wanda ba wanda ya taɓa nuna miki irin shi,dan kiyi hakuri kin ji."

Anan ma shiruu tayi kamar bata jin shi.

"Ni dai ban taɓa ganin inda miji ke ba mata hakuri tai banza da shi ba,shiyasa Haulat ta fiki dan ta iya komai kuma duk abinda na ke so shi ta ke yi."

Kuka sabreen ta fashe da shi me ƙarfin gaske,rungumuta yayi,janye jikin ta tayi cikin kuka ta ce,"Daman baka manta da ita ba?

"Eh ita duk abinda na ke so shi take yi."

Kuka sabreen ta ƙara fashewa da shi.

"Yi hakuri kin ji Baby nah ke kaɗai na ke so a duniya a kan ki na san meye so,amma ban manta da haulat ba,dan ta iya soyayya idan kin so na manta da ita ki yi dukk abinda na ke so kin ji."

kalaman shi har ranta take jin su,ɗaga mishi kai wai tayi,wani irin mugun daɗi ya kama shi.

Gida ya haɗu yafi wance haɗuwa sau biyar,da koma da komai a cikin shi,ba su tsaya wani zagaye ba su ka shiga wani ɗaki,ya umarce ta da suyi sallah bayan sun idar ya kalle ta ya gane yanayin da ta ke ciki a ranshi ya ce,"Sorry Sabreen ba zan iya hakuri ba da na hakura amma ki kiyi hakuri da na."

Toh fah! an zo gurin ni dai ɗan abinda na sani kenan shi ma a book ɗin k/mashi na gani,nan gurin yafi ƙarfi na dan wllh ban san komai ba dan haka nayi nan🚶‍♀️🚶‍♀️

Cikin salo da wayau da dubara yabi da ita,amma sun sha kuka shi kuka ita kuka😅wai ni batool na kawo rahutan ƙarya.

~~~~~~~~~~~~~

Momyn haulat kuwa hauka tsuburan dan kulle ta a ɗaki ake yi,ita kuwa haulat gaba ɗaya ya sukurkunci kamar sabon kamon hauka haka ta koma,ga ɗaya rayuwar ta sauya musu daman momyn ke naiman kuɗin yanzun kuwa ba ta dan da ita da babu duk ɗaya.

Ba abinda su sakina ke yi banda addu'a dan basu ba je naiman magani ba,ita kuwa salma ta gane annabi ya fako,ita kan ta haulat ɗin ta tuba tana son zuwa naiman gafara gurin su naufal amma ta kasa dan yadda jikin ta yake,ta yanke shawarar tura sakina da naiman mata gafara gurin su,rayuwar su ba daɗi kowa ya guje su ba masoya ,masoyan sun koma maƙiya.

Toh haka rayuwa ta ke,duk nisan jifa kasa zai dawo kuma duk wanda ya ce dukinyar wani ba zata tafasa ba shi ma tashi kuwa ko ɗumi ba zata yi,duk abinda ka shuka shi kake girba.

baƙinciki hassada duk wani mugun hali ya ubangiji ka raba mu da su,bamu da wayau bamu da dubara ya allah ka tsare da zuciyoyin daga munanan aiyuka.

🤲Amin ya allah.
~~~~~~~~~~~~~

~~~~~~~~~~
"Nidai ka maida ni gida."
Marairaice fuska yayi ya ce,"Dan allah sabreen kiyi hakuri bazan ƙara ba,ba zan iya rabuwa da ke da domin ke mafarki na kuma zahiri na."
"A'a ƙarawa zaka yi na sani."

Murmushi yayi dan ta bashi dariya ma,"Ba zan ƙara ba."
"Idan ka ƙara xan gayawa Dady da hajia."
"Na yarda yan zo taso nayi miki wanka."
"A'a bana so." ta saki kuka,kallon ta yake yi yana jin wani irin mugun son ta na ƙara yawa a ran shi.

Haka rayuwa ta cigaba da tafiya cikin jin daɗi da ƙaunar juna tun sabreen bata yarda tana son naufal ba har ta yarda.
Farrah kuwa an daidaita da doctor zaina an saka ranar bakin su,lokacin sabreen na ɗauke da ciki.
Sakina kuwa ita da salma sun zu gurin naufal da iyayen shi duk su ka gaya abinda ya faru,dady kuwa har kuka yayi shi da momy da ma hajia,suka ƙara godewa sabreen dan ba dan ita ba da basu hakura ba,sun yafe mata har sabreen wacce daman bata da riƙo ka kaɗan.

An yi bikin farrah cikin jin daɗi an gashe naira dan lokacin naufal ya zama babban mutum mai ƙuɗin gaske,bayan bikin da sati biyu Sabreen ta haifi ɗa namiji sunan mahaifin ta ya ci su ke kiran shi da Ayman kyakyywan yaro mai kama da iyayen shi,bayan sun yi arba'in.
Suka tafi kasa mai sarki saida,sanan su ka wuce malesia anan Sabreen zata cigaba da karantun ta.
Bayan shekara hudu Sabreen ta gama karantun ta computer ta karanta,a lokacin ta ƙara haihuwa ƴa mace,ita ma farrah ta haihu.
rawuyar jin daɗi da so da ƙaunar juna,Hajia kuwa girma ya ƙara kamata sosai.

Kwance ta ke kan cinyar shi tana kallon shi tana murmushi shi ma kallon na ta yayi.

"Haske nah!
"Yadai Baby nah

Saida ta murmusa sanan ta ce ,"Haulat zamu saka wa ƴar mu."

Ɗa ƙyar ya iya maimaita sunan,"Haulat wani irin suna ne kuma haulat,ba daɗi ki canza wani."

Murmushi tayi a ranta ta ce,"Hm ni Sabreen na saka ka manta da haulat kamar yadda na faɗa."
A fili kuwa cewa tayi," to mu saka mata Amina ko khadija ko fatima."

"Sunaye masu daɗi da daraja,dukka ya kamata mu saka mu su sunan fa,dan haka yara huɗu
~~~~~~~~~~

xamu ƙara ya kashe mata ido...

*ALHAMDULILAH*!

*Godiya ta tabbata ga Allah ubangijin taliƙai me kuwa me komai,kamar yadda allah ya bani ikon fara wanan littafin lafiya cikin rahmar shi yasa na gama lafiya tare da alfahari da farinciki wanda ba zan iya misalta su ba.

Sai kun ji ni insha allah nan ba da daɗewa ba.

*TAKU* *HAR* *KULLUM*
*FATIMA* *BATULA*
*BATOOLERTY*
*FATI* *MASHi* .

.
[12/23, 2:34 PM] 🅰° 🅰 D°🅱⭕Y🔛🔝: _ Pσѕт Bу Gяσυρ O F Hуρє Hαυѕα Nσνєℓѕ Bσσк Wнαтѕαρρ 08064400100_ 📚📚